very important aiki yake da Oganshi yasashi yayi yaturomai by 11 na daren nan, gashi yanzu 11 saura, zama tayi tasake fuzar da ijiyan zuciya sannan tadauki wayan nata hannu tasa ta goge fuskanta tass sannan ta shiga turamai address din, kafin tai dialing number Hawwa amman harya katse bata dagaba message ta shiga ta turamata. “Be safe Hawwa, I’m worried about you, Allah tsare hanya” kusan 2min saiga reply na Hawwa tace “I know you are worried, don’t be nakai zan kiraki, love you Best” love you best din takalla sai taji wasu hawaye masu zafi sun sake zubomata tashi kawai tayi tafada dakinta iPad dinshi dake saman drawer side nashi na bed ta kalla yawanci yana daukanshi da daddare yadanyi karence karance, samin kanta tayi da dauka, hoton family portrait nasune ne as wall paper, tadade tana kallon Baban Yaseer a hoton sannan tai kokarin duba wayan taga password shiru tayi tana tunani sai kawai tasaka birthday na su Yaseer taga yabude tashiga cikin wayan, tana dube dube chan ta shiga gallery wayan, hotunan Hawwa taci karo dasu a gallery, dasauri ta shiga ciki hotunan duka na wayanta ne wanda ko Hawwa batadasu dan ita ke snapping nata, tun hotunan su na primary and secondary school, da hotunan datake mata occasionally, da hotuna datama Hawwa adakinta tana sanye da rigan bacci mai kyau ga boobs nata da sukai showing dasauri takai hannu tai deleting wannan, saikuma hotunan datagani wayanda Hawwa nafitowa daga gidansu da hotunanta in different places kaman stalking dinta ma yake yana bibiyanta batare data sani bama ita Hawwan, ganin zuciyanta zai buga yasa tashiga marking pictures din tai deleting everything ta maida iPad din ta ijiye tana sauke ijiyan zuciya saikuma tafashe da kuka sosai na tausayin kanta.

Sosai Hawwa ke gudu akan titi da daddaren nan zuciyanta gabaki daya yazo mata wuya, bini bini take goge hawaye, she can’t even explain d kind of pain datake ciki today has been a bad day for her, daidai ta shigo kaduna around 12 tayanta ya faci gangarawa gefen hanya tayi kawai tai parking tadaura hannayenta asaman fuskanta tafashe da kuka sosai tace “Ya Allah maisa ban sami mijiba? Nayi imani da kaddara mai kyau da mara kyau, I accept whatever you choose for me Ya Allah, ina salla, ina azumi, ina nafilfilu, ina karatun Al Qur’ani, bantaba fasikanci ba, bantaba shan giya ko wani abu na maye ba, inama iyayena biyayi, ina taimakon mutane, daidai gwargwado ina bautamaka Allah” cikin murya mai rauni sosai tace “Ya Allah kaji tausayina kaji Ya Allah, Ya Allah kabani mijina nima, Ya Allah ka kawomin mijina nima, Ya Allah ka aurar dani da gaggawa banson yanda hankalin Babana yake atashe sabida ni, nazaman mishi abin kunya, dani ake kwatancen shi, Ya Allah ka tausaya mini kaji” tafashe da kuka sosai she missed mamanta she missed her, kusan 1hr ita kadai a motan nan babu tsoro ko fargaba aranta koma yatakama takama din kawai, idanunta a lumshe bawai bacci takeba but jikinta duk ya saki taji ana bubbuga marfin motanta “Hawwa Hawwa, Hawwa talk to me,

Hawwa” kaman ana kiranta daga nesa hakan yasa tadan bude idanunta kadan, ganin hasken flash na haskota yasa gently tajuyo da rinannun idanunta ta kallo glass na motan shima ganin haka yasa Baban Yaseer ya haska mata fuskanshi sabida taga shine, wani irin kafeshi da idanu Hawwa tayi batun yauba taga soyayyanta a idanun Baban Yaseer but koda mistake bata taba saran zamata bashi chance ba saisa bata cika zuwa gidansu ba saidai ta sami kawarta awajen aiki kosuyi outing tare, She will never ever betray her friend koda baban Yaseer ne d last man aduniya, but yau for the first time ganinshi cikin tsakiyan daren nan yazo yabi wannan hanyan tundaga Abuja yazo nemanta bayan he came to her rescue earlier today yasa ta tsareshi da idanu tana tambayan zuciyanta could Baban Yaseer be the man she just finished asking God for? Is Allah testing her? Mijin best friend dinta? She rather hakura da auren gabaki daya aduniya tayi alahira, sosai take kallonshi hankalinshi amugun tashe yake buga kofan ganin yanda take kallonshi yana Hawwa open, kusan 2min tadauka tana kallonshi kafin gently ta danna lock motan yayi unlocking kanshi yabude motan da sauri yaduko yana kawo fuskanshi daidai nata cikeda tsantsan so da kulawa da damuwa yace “Hauwa’u! Are you okay?” Tsare shi da idanu tayi sai kawai hawaye ya gangaro daga idanunta dasauri yashiga ciro handky daga aljihunshi jikinsa har rawa yake yace “don’t cry and don’t be afraid I’m right here, Aliyu is here”.

EPISODE 2️⃣4️⃣

Kawai tausayi taji tabama kanta saisa takasa rike hawayen dan tana cikin jarabawan rayuwa, she’s 30 batai aure ba babu miji, kowa is pressuring her, her biggest support, her biggest fan is her best friend Ni’ima da tun suna yara suke tare, kawancen amana da iyayensu sun zama daya ma, she’s not a small girl when she sees love she knows love, wani irin kaddarane wannan? Baban Yaseer can never be her amsa nooo please Ya Allah not my best friend’s husband, ganin hawaye yakasa tsayawa daga idanunta asanyaye Aliyu yace “I’m here for you, I will forever be right here! Ina taredake Hawwa in good times and bad times, dare da rana, I’m right here” ahankali yadaura hanky kan fuskanta wani sanyi taji dayasa ta lumshe idanunta da sauri takai hannunta i ta karbi handky tana goge fuskanta, tadanja majina dadan ragowan karfin zuciya tace “maisa kabiyoni Baban Yaseer? Nace kabiyoni ne must u follow me everywhere? Must you get involved in my issues? An gayamaka I can’t take care of myself ne ko I need your protection”? Ataushashe yana kallonta ganin ranta abace, cikida zazzafan kauna yace “sabida bazan taba iya bacci ba bayan nasan kina irin wannan hanyan, I care for you” ahankali Hawwa tace “wat if something

happens to you”? Asanyaye yace “I don’t care koma menene yasameni I just wanna keep u safe” abu tahadiye a wuyanta sai kawai ta juyo ta yunkuro tace “I need to change my tire, spare tire na booth” matsamata yayi tafito tai booth yabi bayanta tana bude booth din takai hannunta zata dauki tayan yarigata dauka yace “let’s go muje motana ki zauna” tsayawa tayi tana kallonshi, “muje dan Allah Hawwa dare ne mu kadai a titi” batai musu ba yayi wajen motanshi da ita yabude mata gaba ta shiga ta zauna ya maida yarufe sannan yadawo booth nata yaciro supanu yaje gaban motan yana kwance tayan dayay less, sosai Hawwa take kallonshi kaman yauta fara ganinshi abubuwa da dama suna yawo aranta, tana zaune awajen saiga yan sanda sunzo wajen fitowa tayi ta nuna musu ID card dinta tayasu gyara tayan sukayi, suna gamawa Baban Yaseer yabar musu motanshi yabasu kudi su tsaremai sannan yashiga na Hawwa, hakan yasa ta zagayo ta zauna ya kunna motan yaja waje tajuyar da kanta tana kallo ahankali yace “do you think is right kije kidan Anty ki middle of the night? Kodai idan mukaje zaria namiki booking hotel, idan gari yawaye saikije”? Tana kallon waje batare data juyoba tace “zan iya zuwa wajen Ammi na anytime anyday” gyadamata kai yayi bai sake magana kusan 30min sai chan yace “Hawwa it’s okay not to be okay” lumshe idanu tayi tabude anatse yace “you got this! Karki bari kalaman Baba natabaki, karki karaya, I hate seeing you like this” yadan kalleta yanda take kallon waje yace “kinji” gyadamai kai tayi daganan basu sake magana ba harsukakai zaria, nunamai hanya tadingayi har zuwa wani gida a wani anguwa mai dan kyau da mutunci, saukowa tayi ta zagayo tadan kalli Baban Yaseer dake kallonta tace “dan bani car key” zare key motan yayi yabata yana kallonta, a gate tasaka wani key dake jikin motan tabude kofan tashiga ciki tana sallama tsakar gida ne mai fadin gaske, tourchlight taga an haskewa taji muryan yan dattijuwa na “waye awajen gate din nan” ana bude kofa da gudu Hawwa tai wajen kofa matan na bude kofa dadan charbi a hannu Hawwa ta rungumeta da karfi tace “Ammiiii na” ririketa matan tayi tace “Hasbunallahu wa ni’imal wakeelu Hawwa kece da daddaren nan, ke tashi kiga na ganki lafiya Hawwa” tadago Hawwa daga jikinta murmushi Hawwa tayi tace “Ammi baban Naseer na waje bani key gate na bude ya shigo da mota saiya dan zauna zuwa safiya yakoma Abuja” wani dan kallo Ammi tamata tace “Baban Yaseer kuma? Aliyun Ni’ima”? Gyadamata kai Hawwa tayi Ammi tabata key fita tayi Ammi itama tafito tana haskawa bude gate din Hawwa tayi yashigo da motan ta maida gate din tarufe Ammi tace “maraba da Baban Yaseer, sannunku sauko sauko” Saukowa yayi kanshi akasa cikeda kunya yace “Ammi mun sameku lpy” cikeda fara’a tace “Alhamdulillah ina jikokina? Da y’ata Ni’ima hope duk suna lpy”? Akunyace ya gyadamata kai yace “Alhamdulillah” murmushi tayi tace “muje nakaika side din su Baffa ka kwanta bazakabi hanya da tsakar daren nan ba sai idan Allah ya kaimu da safe akawo maka abinci ne”? Dasauri yace “a’a Ammi dare nayi bana iya kara cin abinci” satan kallon Hawwa yayi dake gefen

Ammi tana wasa da hannunta yamika mata car key ta yace “take” dan dagokai tayi kafin tasa hannu ta karba Ammi tace “muje” suka wuce suna hira itakuma tawuce wajen motar ta booth taciro akwatinta ta gu huri ta shiga dashi ciki, bayin Ammi tafada tana cikin wanka Ammi tashigo tasami waje ta zauna yanda ta ganta haka tasan dawani abu.
Towel din Ammi ta dauro tafito Ammi ta kalleta tace “zonan Jidda” kayan shafanta tadauka tazo kusada Ammi ta zauna tana bata cream dinta a hannu Ammi ta karba tana sauke ijiyan zuciya tace “meya faru?” Dan shiru tayi sabida kawai taji komi yadawo mata sabo, hannunta Ammi takama tana shafa mata mai kafin takalleta strictly tace “ya akayi kike tare da mijin kawarki at this type of time and day Hauwa’u”? Baki tabude zatai magana saikuma tadan sauke ijiyan zuciya Ammi tace “speak” anatse tace “Ammi wlh I don’t know cus ni ko kiran Ni’ima ma banyi da abun yafaru ba, probably Baba ne yakirasu to check ko ina gidansu, saita kirani daga gayamata ina hanya zanzo wajenki hala to shine ta turoshi” Ammi na kallonta ta sauke ijiyan zuciya tace “Hawwa babu wani naki dabaisan relationship dinki da Ni’ima ba, yarinyar nan kawar amana ce, yanda kika daukeni haka tadaukeni, don’t ruin friendship naku under no circumstances, you know maganan danake” gyadamata kai Hawwa tayi tace “nasani Ammi” saikuma ya tashi daga gadon ahankali zuwa akwatin nata tadauki dogon riga na bacci tasaka ta zare zanin wankan ta shanya ta dawo gadon tahau ta daura kanta kan cinyan Ammi tareda sauke ijiyan zuciya tabude watsapp tama Ni’ima chat “Just got to Ammi’s place, Ni’ima why did you send Baban Yaseer? Why” tura chat din tayi taga yayi layi biyu alamun datan ta a kunne amman ba’a budeba jira tayi ta amsata but shiru ijiye wayan tayi ahankali tana lumshe ido kafin kaceme bacci yayi awon gaba da ita dan tagaji yau.
Yanda bacci ya shigeta yasa Ammi bata tadataba ta shiga dakin yammatan ta su biyu Amina da Ramla ta tadasu don salla itama tayi sannan tasa suka shiga kitchen cus taji Baban Yaseer yafice salla.

Wuraren 7 yashigo gidan a tsakar gida yaga Ammi tareda Ramla datake gwadama yanda ake buga kosai sun hada gawayi dan basu soya kosai a gas, ganinshi yasa Ramla tace “ina kwana Baban Yaseer” murmushi yamata yace “lpy lau” yace “ina kwana Ammi” murmushi tamai tace “an tashi lpy sannu da kokari fa Aliyu, Allah ya maka albarka, bari yanzun nan zan kawoma kosai nariga an dama kamu saina kawoma kayi karo kafin kashiga hanya” girgixakai yayi yace “no Ammi bazanyi kari ba bana kari da wuri yan sanda na barma motana chan hanyan kaduna dole nafita yanzu Ammi” yayi maganan yana ciro kudi daga aljihunsa daya samo a ATM fitan nan nasa a kujeran tsakar gida dake gefen Ammi ya ijiye kudin yace “aba Hawwa idan ta tashi, wannan kuma aba su mai girki” cus baisan sunan Ramla ba, hade fuska Ammi tayi tace “kaga dauki kudaden nan karna saba maka Baban Yaseer” dasauri yajuya yayi gate yace “Ammi nagode” yafice dasauri dudda har ranshi yaso

yaga Hawwa kuma sarai ta tashi tun dazu har salla ma tayi kawai bataso ta ganshi ne kawai yasa bata fitoba, tanajin fitanshi tafito falo Amina dake gyaran falo na ganinta tai ihu sosai “Ramla Ya Hawwa ta tashi” tawani zo dagudu tai tsalle tafada jikinta Hawwa tai dariya sosai Ramla tasaki kosan datake ta rugo dakin aguje itama tai tsalle kawai Hawwa tai kasa suna kanta, Ammi ta shigo dakin ta kwadamusu duka abaya tace “Oya ku dagamin ita bance ku karyamin diya ba” kankamesu Hawwa tayi tace “Ammi I missed my babies” hararansu Ammi tayi tawucewarta tafito tashiga soya kosan da kanta tunda taga shirme suke Hawwa tafito tareda su tana Ammi wai ina su Hamza da Ahmadu? “Hamza na school, Ahmadu yace anjima zaizo da matarsa su gaidake, Baffan ku na dayan gidan sai gobe zai dawo nan amman hala anjima ki gansa” murmushi tayi ta karbi kosan tana soyawa su Ramla nabata labari she looks so happy Ammi tayi murmushi ganin ayanda idanunta sukadan kumbura jiya sabida kuka sun sauka sosai yanzu kaman batayiba.

Wuraren 12 Ni’ima taji ana bude gate, tunda tasan Hawwa bata taba taga miss call na Hawwa taki kiranta back ba sai yau, nor tai replying message nata, jiya tamata message shiru, da safen nan takirata sau biyu ba amsa sai tamata magana tace “call me idan kin dawo daga hospital Best, su Ramla nata tambayanki”.

Jin ana bude gate yasa ta tashi dagakan kujeran tawuce da sauri tashiga kitchen, ita kadaine agidan su Yaseer na school sai though 1 suke tashi on Friday, sallama taji yayo yashigo abu kawai taji yatokare mata zuciya tama kasa amsa sallaman, kofan bedroom nasu taji yabude ya shiga sannan tasauke ijiyan zuciya tashiga fito da flasks da plates tana ijiyewa a dinning tazauna a dinning din saikuma chan tamike tawuce bedroom din nasu ta zauna bakin gado tanajin karan zubam ruwa ba’a wani jimaba yafito daure da towel a waist yadan kalleta hada idanu sukayi tana kallonshi kaman yau tafara ganinshi dauke kai yayi da sauri yawuce wajen wardrobe nasu yace “wife ya gida? Su Yaseer basu dawo daga school ba”? Tana kallonshi kaman gunki tace “basu dawo ba tukunna” gyadamata kai yayi ya tsaya gaban mirror yadau mai yana shafawa yakasa wani maganan, kalulu ta hadiye a wuya tadan bude bakinta kadan saikuma tarufe sai chan kuma tace “ka kuwa sanar da Hawwa kana sonta?!” Dum! Haka maganan yadaki kunnenshi man daya diba zaikai jikinshi yashafa kasa shafawa yayi yajuyo yakalleta suka hada ido yace “wace irin magana haka kikeyi Ni’ima”? Mikewa tayi a fusace ta nunashi da hannu tace “don’t you dare lie to me, nasan son Hawwa kawata kake why are you hiding it? Eh maisa kake boyewa bayan ka kamu da mugun sonta” hade giran sama dana kasa yayi yadan dafe kanshi yace “kinsan mene? I don’t want your drama this afternoon I had a long journey I just want to sleep peacefully, dan Allah ki kyaleni I don’t know wat you are

talking about” yajuya zai wuce yanda abu kecin zuciyan Ni’ima batasan sanda tai ihu ba tace “Namiji munafuki, namiji mara amana, namiji butulu! Aliyu I know everything! I know about hotunan Hawwa dake wayana da duk ka sace suna wayanka, I know kana stalking friend dina kana biye biyenta kana mata hotuna without her knowledge, how dare you kana karyata cewa sonta kake don’t be a coward, kaji be a man for once mayaudari kawai” “Ni’eematullah!” Baban Yaseer yakirata azafafe idanunshi sun kada sunyi ja, yace “yes yes yes I love Hawwa! Yes inason kawarki! Yes I love your best friend Ni’ima and so what!?” Hannu Ni’ima takai tadaura kan bakinta tana kallonshi completely heart broken hawaye masu jarababben zafi na saukowa daga idanunta, yace “do you think I’m happy with the fact that I’ve fallen in love with your friend? Kin dauka choice dina ne? Kokin dauka son Hawwa ya tambayi izinina? Why are you insulting me calling me names mena miki? Tayaya na yaudareki? Kinga na sanar da ita ina sonta ne? Ko kinga nayi wani abu ne? I love Hawwa yes and I also love you! Sabida I don’t wanna hurt you saisa all this years ban auri Hawwa ba, I can’t bring kaina into to hurting u that much, nasan yanda zakiji, I know wat kishi is! Yes I love Hawwa, and I also love Ni’ima, nima I don’t know mesa Allah zai dauramin soyayyan kawaye biyu kuma best friends, I know this same reaction kikeyi maybe na gayama Hawwa ina sonta zatamin more than yours, so just let me be, ban miki komiba ban yaudareki ba, and bance zan auri Hawwa ba cus nasan bazata yardaba, but all I know is harna mutu bazan taba daina son Hawwa ba, son danake mata yawuce tunani na, when it comes to Hawwa banmasan me nakeyi ba, I just want her to always be happy, I want to protect her, and always be there for her and make her happy, that’s just it” yayi maganan yana komawa wardrobe yadauki kayan dazaisa yafice daga dakin, Ni’ima tafashe da kuka bana wasaba gwanin ban tausayi tana zubewa akasan dakin…….

TOH JAMA’A IMAGINE MIJINKI NA SON BEST FRIEND DINKI, YAYA ZAKIJI???

HOW WOULD YOU HANDLE THE SITUATION???

KAI YAYA ZAKIYI NE????

IDAN KECE NI’IMA MEZAKAYI KO YAYA ZAKIYI DA HAWWA???

THINK AND TELL ME 

EPISODE 

Ni’ima kuka kawai take bana wasaba, tana ganin tunda aka haifeta bata taba feeling wannan kalan zafin da zuciyanta kemata yauba, for years sunyi aure itada Baban Yaseer basu taba having issues ba like babban issue haka, batada wani complain akanshi but yau yayi hurting nata kwarai, kalan soyayyan datagani a idanun Aliyu ko ita baitaba mata shi ba, duk soyayyan dazaisa kafara stalking mace kana bibiyan hotunanta harda na kusan tsiraici ma dan kayan bacci ne ba karaman soyayya bane, soyayya ce ma dakana bukatan kaga therapist, he is sickly in love with Hawwa that’s idan akwai word din, ciwon son Hawwa yake, yanzu Hawwan ta Baban Yaseer zaiso? They’ve been through so much together with Hawwa, Hawwa is her biggest support bazata taba manta sanda Hawwa tasayo mata form na school of Nursing takawo mata ba, sabida lokacin Babanta baida lpy basuda kudin daza’a saimata form agida haka Hawwa tadinga dinki tahada kudin tasayo mata form 5k takawo mata that day was the happiest day of her life, Hawwa tarakata taje tai entrance exam na shiga school of nursing din, dataci Hawwa was happier than her ma datai jarabawan, bayan 2days aka kirata zuwa interview still Hawwa tabita sukaje tajirata awajen tayi tafito suka tafi gida dagabaya aka saki admission taci an bata admission, babu kudin registration Hawwa tadinga dinki day and night, tasaida babban wayanta alokacin tasa sim nata akaramin waya takawo mata 30k itama Maman Ni’ima tasaida sarkanta da dankunne aka hada 20k daga wajenta aka hada mata taje tai registration da 50k, the first ever book da pen datai rubutu dashi a school of nursing Hawwa ta siyamata su, hawaye ta share tana tuna rayuwansu da Hawwa duk yanda mutum zaiyi tunanin friendship, kawancenta dana Hawwa yawuce haka, sabida kawance ne mai asalin amana, Hawwa harda Maman Ni’ima take fada akanta just like yanda take fada da Baba akan Hawwa tanajin haushinsa kan Hawwa haka sukema junansu wajen iyayensu, they supported each other like better half, kawance su babu ha’inci, babu kyashi ko rowa, babu bakinciki, they’re always happy for each other, dudda tayi aure Hawwa bata taba mata bakincikin wani abuba, datana da ciki wlh wlh ko Baban Yaseer mai cikin baikai Hawwa kula da ita ba, idan tana craving wani abu Hawwa zata iya barin aiki taje ta nemo takawo mata, yanzu haka yaranta su Yaseer sun fison Hawwa kan mahaifiyarta grandmother su sabida aminci da kaunan dake tsakaninsu, she’s just crying bitterly bamatasan ina zata saka kanta ba, kawai taji ta bama kanta tausayi bamatasan inda zatasa kanta ba wannan wani irin intertwine situation ne haka? Wani irin kaddara ne wannan? Ita da Hawwa started friendship ana maganan tun suna around 6yrs

old cus primary one suka hadu, yanzu suna 30yrs, 20yrs plus friendship kifa kanta tayi akafanta tana shesheka tajiyoshi an budemai gate yafita tasan mosque zashi yau juma'a.

**

Har yamma na rannan Friday din nan shiru ba kiran Ni'ima which is so unlike her, dudda su Ramla dake damunta da labarai but still binibini Hawwa na duba wayanta ko Ni'ima tamata watsapp message ko kira ko wani abun amman shiru, tasake kira but still ba amsa dan damunta abin yafarayi sosai.
Bayan sallan magrib suna zaune sunacin abinci duka tare harda Hamza wayan Ammi yahau ringing wayan ta kalla taga Baba ne hakan yasa tadauki wayan tafito daga dakin dan bataso yaran especially su Ramla susan maisa Hawwa tazo tawuce ta shiga side nasu Hamza zama tayi kan katifarsu tayi dialing number Baban ringing daya yadaga ya buga mata sallama yace "ya wajen naku Rukayya" Ammi tace "Alhamdulillah" ijiyan zuciya Baba yasauke yace "Baban Yaseer ya sanar dani Hawwa na wajenki kice mata ni ban koreta ba ta tattaro tadawo gidan nan" anatse Ammi tace "sabida kacigaba da tallatata a masallaci kana neman kai da ita" dan shiru Baba yayi saikuma chan yace "kinga Rukayya ni ba kira nayi fada dake nayi ba, tun fadanmu na farko bayan rasuwan mahaifiyan yarinyar nan kikaso tafiya da ita nace a'a kika dinga bala'i dani nasan ba kaunata kikeba da akwai yanda zakiyi ma da rabani zakiyi da yarinyar, ni duk wannan ba itace matsalata ba kawaidai kice mata tadawo gida kar fushina yabita" dan sauke ijiyan zuciya Ammi tayi tace "yarinyar nan kawai sabida kaine mahaifinta saisa muka barmaka, wlh na sanar da Baffan ta saidai duk abinda zai faru yafaru, aure na Allah ne ba nakaba, da iyaye ke aurar da yara da tuni kowa yayi, Allah shine komi ke hannunsa, kaida yakamata ka godema Allah dayabaka irin wannan yarinya a'a sai tsalle tsalle kake" katse wayan Baba yayi danshi dama da Ammi basa jituwa kona sakan daya.

Around 8 nadare Hawwa taga Ni'ima na online ta karanta duka messeges nata amman bata kulata ba, watsapp call ta danna mata but harya katse bata dauka ba abin ya bala'in damunta voice note ta danna tace "Ni'imyyyyy sorry please kidena fushi, wlh I know kema na sanar dake abinda yafaru ni da Baba you will not be happy with abinda yayi, banson na tadamiki da hankali koki hanani zuwa wajen Ammi saisa ban sanar dake ba sorry, ina Yass dina da Meen" ta aika mata voice note din tarike wayan tana kallo ganin yaje but still ba asaurara ba kuma tana online abin yafara damun Hawwa sosai bahaka Ni'ima ke fushi da ita ba saidai tai masifa dukansu basu iya gababa saidai suyi fada ayi zage zage da baki a shirya, dukji tayi ba dadi haka ta tasa wayan agaba tana kallo kusan 20min kuma tana online chan saita sauka ijiye wayan Hawwa tayi ta kwanta kan gadon Ammi tana sauke ijiyan zuciya.

Yau Saturday Baffa (mijin Ammi) na gidan tun goma dayazo baibarta tahuta ba da labarai da surutai dan yana mutuwan son Hawwa, tana yawan turamai kudi akai akai kaman yanda takema Ammi ta, surutunsa yasa tadan manta da damuwanta sai dare kuma tashiga kiran Ni'ima harsaida Ammi talura tace "banji kinyi waya da Ni'ima tunda kikazo ba da tuni tace abani waya tai magana dani, Ni'ima dana sani da saita kawo karinki kin shiga hanya da daddare" dan murmushi Hawwa tayi tace "tana hospital ne Ammi shift take covering, chatting mukafiyi this days Ammi" dan murmushi kawai Ammi tayi bata sake magana ba tace "bari nakaima Baffan ku shayi" tafice.

Washegari Sunday around 11 tafito su Hamza na samata komi a booth, Baffa yace "Hawwa ayi tuki ahankali kinjini" murmushi tayi tace "toh Baffa na" Ammi tace "Allah kiyaye hanya, dan Allah banda gudu" Gyadamata kai Hawwa tayi su Ramla suka rungumeta tamusu sallama tafito, text tama Ni'ima tace "gani nashiga hanya zan dawo office gobe".

Karfe biyu dawani abu anadai neman karfe uku Hawwa ta shigo Abuja hanyan hospital din su Ni'ima tawuce direct ta shiga tai parking ta kashe motan, wayanta tadauka tafito abayane ajikinta baki tawuce ciki office din Ni'ima tawuce tareda knocking tana budewa wata nurse ce aciki tana ganin Hawwa tai murmushi tace "wajen Ni'ima kikezo? Bakuyi wayaba ai batanan yau is her off" amutunce Hawwa tace "okay okay nagode" tajuyo tafito motanta tashiga tafita daga hospital din wlh she's so worried rabon datai magana da Ni'ima tun Friday wani irin fushi Ni'ima keyi da ita haka, hanyar gidansu Ni'ima tayi har zuwa layinsu mai kyau, gaban gidansu ta tsaya tai horn maidaidaicin gidane mai kyau ga babban bakin gate nasu, lekowa mai gadin yayi Hawwa tadanmai murmushi tana jiran taga yabude gate saitaga yabude karamin gate da fara'a kan fuskanshi yace "Hajiya barka da yamma" gyadamai kai tayi tace "ya kuke" yace "Alhamdulillah" saikuma ya tsaya sakaka yana kallonta Hawwa tace "budemin gate ko basanan ne"? Bazai taba iya maimaita abinda Ni'ima tacemai ma hakan yasa dasauri yace "eh basanan tun safe suka fita" danjimm Hawwa tayi kaman daga sama sukaji muryan Yasmeen ta tsandala ihu tana kuka wayyo kafanta dasauri maigadin yakalli gate saikuma yajuyo yasauke kanshi kasa, Hawwa dake juyo muryan yaran tace "kace basanan ba muryan Mims naji na kuka ba" dan sosa kai yayi da hannu kanshi na kasa yakasa kallonta yace "ahhhmm Madam tacemini duk randa nakara barinki kika shiga gidan abakin aikina kiyakuri Hajiya" dasauri da kunya yajuya ya shiga gidan tareda maida gate din yarufe Hawwa tai shiru tana wajen she don't even know wat to think, her mind just went blank wlh takai minti ashirin awajen kafin tadan fuzar da

iska taja motan tabar wajen.

EPISODE 2️⃣6️⃣

Batason ta shiga gidan da force, she knows Ni’ima, ba hakanan zatabada sakon nan ba, she have to respect her home, layinsu ta wuce duka zuciyanta ba dadi harzuwa gida tundaga nesa da Baba yahango motanta yamike tsaye yana murmushi hankalinshi ya bala’in kwanta, tana parking ya hade fuska kaman bashi ke murmushi ba ganin tadawo, kashe motan Hawwa tayi tafito batare data kalli inda Baba yakeba dan yanzu saidai su dinga bura’uba da Baba amman bata auren mutumin nan wlh, Booth tabude tasauko da akwatinta kasa ta goya na baya tarufe motan ta gunguro jakan daidai tazo inda Baba yake batare data kalleshi ba murya ciki ciki irin na yaron dake fushi da iyayenshi din nan tace “Assalamu Alaykum Baba ina yini” dan kyafkyafta idanu Baba yayi yace “sannu uwar zuciya ladingo mai fada da mahaifinta, sannu da zuwa jeki huta ni da kene agidan nan” wucewa tayi abinta tana shiga gidan suka hada idanu da Umma data haderai ganinta kaman bakin ciki zai kasheta tadauke kai itama haka Hawwa tawuce tabude dakinta ta shiga da komi, kayan jikinta tarage tafito tai alwala takoma daki tai salla sannan ta kwanta akasan tadauki wayanta tashiga kiran Ni’ima koma menene they need to iron it out, tabama Ni’ima sama da 15missed call babu wanda tadaga, bala’in damun Hawwa abin yake, she’s confuse ma, basu taba kalan fadan nan ba itada Ni’ima, Ni’ima bata iya gaba ba nor shariya, toh wat is happening da Ni’ima is not talking to her? Whatsapp tashiga tashiga typing. “Best enough please, talk to me Dan girman Allah, I’ve been saying sorry amman kinki kulani, daman akwai abinda zanyi da u will not understand me? Baba ne yace nabarmai gidafa, I’m sorry ban sanar dake ba naje gidan Ammi, banson kice nazo wajenki ne kuyita dawainiya dani, naje hospital yau ina shigowa garin nan bakinan nazo gidanki i learned that u don’t wanna see me, I’m very very worried, Best I’m sorry, sorry, sorry” Hawwa tashiga tura mata sorry sunfi guda dari cus ta bala’in damu sabida Ni’ima is already part of her, this few days dabasuyi magana ba ko chatting she’s feeling kaman wani part of her is gone, duk uban sorry nan amman har 8 nadare Ni’ima bata bude chats din ba, ashe harda gidan Ammi kesa abin baiwani dameta ba amman yanzu data dawo nan ita kadai sai Hawwa tashiga bala’in damuwa, sai tunane tunane take, taba cracking what could make Ni’ima this angry? Bata taba kawo Baban Yaseer ba cus tadauka Ni’ima ta turoshi yabiyota hanya, tai tunani tai tunani duka amsan da brain dinta ke bata is takama tashiga hanya da daddare batare dataje wajen Ni’iman ba

abinda yasa take fushi kenan, ko abinci bata nema ba tunda tashigo garin nan cus bamata da apatite na ci haka tai bacci da yunwa.

Around 5 ta farka sabida aiki wayanta tadauka ta danna abinda tafara gani is text message from Ni'ima dasauri tawani zabura ta tashi ta zauna bacci nafita daga idanunta tabude message din da sauri.
"Inada magana dake Hawwa, let's meet a Dims Eatery by 4:30 na yamma today" harwani ijiyan zuciya Hawwa ta sauke tamata reply okay good morning, saikuma ta kalli time da Ni'ima ta tura mata sakon around 2nadare, Ni'ima datasani lokacin nan bacci take Allah sa she's fine babu wani abu dake damunta, kokuma is Ni'ima sick? Shine take boyemata cus bataso ta damu? Or is she pregnant? Dan cute murmushi Hawwa tayi kadan tace "ai kinsha miya da yawa is good kiyi ciki ama su Yaseer kanni" ta ijiye wayan dan damuwanta yaragu sosai tafito taje tai wanka tai brush da alwala tadawo daki simple riga tasa tai salla tana kan dadduma har 7 sannan ta tashi tafara shiryawa.

Riga da wando tasaka, navy blue wando ne palazo da riganta shima navy blue but mai designs na flowers daya saukanmata har cinya ta makala botura rigan yamata kyau cus ita tadinga da kanta zaka dauka wasu expensive kaya ne nan ko yadi ne tasayo a wajen yan material a kasuwa tadinka abinta, sky blue veil tadauka tai rolling tai pinning tasa links na hannun rigan masu shegen kyau tashafa lip gloss lips nata na shinning sosai, hada yan abubuwan datake bukata tayi a jakanta tadauka tasa cover shoe mai dan tsini kadan mai shegen kyau na zara, tasaka agogo tafesa turare tai wani kalan calm kyau kaman ka sace tana sassanyan feminine scent, tafito ta kulle kofa tana kamshi tayi waje, Baba baya waje maybe yana masallaci har yanzu, motanta tawuce tai warming ta chanza ruwa ta maida bonnet din tarufe sannan tashiga mota tabar anguwan saida tasha mai agidan mai sannan tawuce office by 8 tana ciki. Rannan sunsha aiki kan wasu victims da akai kidnapping sai around 4:20 sannan ta iya fitowa, salla tayi a mosque nasu da gudu gudu tawuce mota ta shiga taja tabar premises nasu tanama Ni'ima text tace "yanzu aka banni nafito I'm driving already you will see me nan da 20min" ijiye wayan tayi tana kallon hanya tana murmushi yau zasu shirya da Best, dadan holdup a hanya saida ta bata 30min around 5:00 takai resturant din tai parking, babban restaurant ne hadadde, Ni'ima na zaune asaman terrace dan wajen tabiya kudi tamusu booking, shiru tayi bata ko motsi kallon Hawwa takeyi dataga tana sauri sauri tafito daga mota sannan ta rufe kofan, kallonta Ni'ima take batako kyaftawa yau for the first time tana ganin some things da bata taba luradasu da ba, Hawwa nada kyau sosai tafita kyau sosai, bazama ka kwatanta ba, yanda take saurin nan her boobs are shaking haka jikinta ma, babu wani abu da Hawwa bata fita dashi ba, ga diri danma bata taba saka kayan

da ake gane shape nata, Hawwa akwai boobs manya masu kyau a tsaye ga shape, itako nata sun soma kwantawa kai sunma kwanta yara biyu to sun sha yanbiyu wasa ne ba dole Baban Yaseer yace yanasonta ba, gata doguwa and naturally dogayen mata nada farin jini da grabbing attention da maza ko ita tana tareda Hawwa ansha complementing tsayin Hawwa maza na admiring hakan, gata da gashi ga dadin murya na fitina ga iya turenci ga iya magana ga natsuwa ga wayau with lot of maturity, bazaka taba kama Hawwa na murmushi anyhow ba ako'ina dan tafi Hawwa fara'a sosai, gata da ilimi, ga Allah yamata gata she's so bright and she's a lucky mutum, imagine she's no body but Allah supported her tasa kanta a makaranta da kudin dinki, tana fara aikin police akai promoting nata sabida sunga how intelligent and smart she's ba dole Baban Yaseer yasota ba, Hawwa tahadu in every aspect wlh boko da islamiyya ga wayau ga hankali ga jarumta ga hazaka, ga addini yawan salla da azumi kai ga komima, idan Hawwa tasami miji kowaye yanzu saita kamashi with her charming and seductive nature, kai ko ayawan addu'a da salla sai Hawwa ta kwacemata Baban Yaseer, banda haka Hawwa zatai everything possible not to live marriage idan tai aure dan tadade bataiba, how can she allow Baban Yaseer ya aureta? Bayan tasan Hawwa tafita komi cus tafi kowa sannin qualities na Hawwa, Hawwa is desperate for a Man idan tai grabbing Baban Yaseer ai tata takade, kwace mata miji zatayi ya manta dasu, gatada karfin sha'awa Aliyu yasami haka ai shikenan kuma takade tana cikin tunane tunanen nan taji ringing a wayanta firgigit ta farga daga tunanin ganin Hawwa ke kiranta yasa ta katse wayan tamata text kizo terrace ina sama.
Tana zaune awajen Hawwa ta shigo bayan an bude mata kofan shigowa terrace din hada ido tayi da Ni'ima data kafeta da idanu tana zaune kan kujera tana sanye da black abaya saitaga Ni'iman ma dukta rame tai wani iri kaman mara lafiya, dawani sauri tai wajen jakanta ta ijiye kan table da wayanta kai tsaye tai hugging Ni'ima tace "Besttttt" ijiyan zuciya Hawwa ta sauke kusan 2min amman Ni'ima batasa hannunta tai hugging nata back ba, sakinta ahankali Hawwa tayi takalli fuskanta tace "are you sick? Face naki gabaki daya ya chanza, what is wrong with you?" Dan gajeren murmushi Ni'ima tamata ta nuna mata kujera tace "sit please" dan jimmm Hawwa tayi tana kallonta kafin tawuce tazauna kan kujeran, Ni'ima tadan kalleta dan hakanan bamatason tana kallon Hawwan yanzu cus is making her feel insecure and so little tace "mezakici order?" Girgiza mata kai Hawwa tayi tace "kin manta yau Monday ina azumi" gyadamata kai Ni'ima tayi batace komiba tana kallon gefe, wani iri Hawwa taji tanaji ganin yanda Ni'ima is acting wired ko kallonta ma batason yi kaman ta tsaneta, no let them iron koma menene she hates fight, ahankali tace "Ni'ima wat is wrong? Dan Allah kifadamin? Why don't you want to look at me? Fushi kike dani"? Dago kanta Ni'ima tayi takalli Hawwa adake tace "Hauwa'u!" Faduwa gaban Hawwa yayi dan yau ne rana na farko da Ni'ima zata kira sunanta haka amman tadaure tace "na'am Best"

murmushi Ni’ima tayi wanda is so obvious you can see how hurt she’s, da kyar take murmushin ma tana kallon Hawwa ido cikin ido tace “Baban Yaseer na sonki Hawwa!” Dooom!!! Haka Hawwa taji gabanta yabuga, still cikin karfin hali Ni’ima tace “nasan bai sanar dake ba saisa ni nake sanar dake, inaso na tayashi tambayanki hand naki in marriage” tai dan shiru takara murmushin da da kyar take murmusashi tace “zaki aure Baban Yaseer Hawwa!?”.

EPISODE 2️⃣7️⃣

Mikewa da bala’in sauri Hawwa tayi tana kallon Ni’ima cus yanzu take understanding the whole reason na shareta da Ni’ima tayi tama kasa magana sai kallon Ni’ima take dake kallonta itama idanunta sun kada sunyi ja tace “kibani amsa I want to know zaki aure Baban Yaseer ohh zaki aure Aliyu ko bazaki taba aure ba”? Kai tsaye Hawwa adan zafafe tace “da yanzu this instant Allah zai karbi duka ran mazan duniyan nan yarage Baban Yaseer tal kuma kwal aduniya bazan taba auren sa ba saidai nakoma ga Allah haka!” Tafadi da zafi sabida tambayan ya bata mata rai barinma data gane it has something to do with fushin da Ni’ima keyi, with so much sincerity tace “bantabama Baban Yaseer kallon abinda zan aura ba saidai kallon Babban Yaya agareni, mijin kawata kuma” sosai Ni’ima ke kallonta batako kyafta idanu, Hawwa tace “I will never, ever, marry mijinki koda ranki ko ba ranki cus I consider it cin amanan kawance! Ni’ima kada ki karamin irin maganan nan, bazan taba auren mijinki ba” dan tuntsurewa da dariya Ni’ima tayi kaman mahaukaciya mai ciwo tana kallon Hawwa saikuma tai shiru cikin wani kalan siga da ita kanta Hawwa bata gane ba Ni’ima tace “nima bazan taba so naraba mijina dake ba Hawwa!” Takalli Hawwa sosai tace “namiki tambayan nan ne kawai sabida na sauke hakkin ki da hakkin Aliyu” tasauke ijiyan zuciya kafin ahankali tamike tsaye itama tana kallon Hawwa kaman yanda Hawwa ke tsaye tana kallonta tace “I have few things to say to you Hawwa” ta sauke ijiyan zuciya tace “Hawwa mun taso tare, no one knows me better than you do, I am always honest with my feelings kinsani” tai dan shiru sannan tace “Hawwa ke babban kawata ce, haka mijina ma mijina ne! Mijina daban yake akan kowa da komi! Thinking of sharing him with you ma is shattering me, Hawwa bazan iya baki aron Aliyu kona kwana daya ba ballema na ana maganan rayuwa har mutuwa that’s aure, I can’t ke I don’t even wanna picture you as matar Aliyu, matar mijina!” tasakeyin shiru sannan tasauke kanta kasa kafin chan tadago takalli Hawwa dake kallonta looking confuse and scared and everything ma, Ni’ima tace “ni da ke ba yara bane, we are not more teenagers, I don’t wanna end up

fighting you over man, ni da ke munsan wats good for us, inhar Baban Yaseer yayi developing feelings for you relationship dina dake have to come to an end!" Dasauri Hawwa ta kalleta kirjinta na girgiza lips nata narawa magana ma baya fitowa sabida yanda maganganun Ni'ima ke dakan kunnenta abazata, gyadamata kai Ni'ima tayi tace "Hawwa stay away from me kifita daga rayuwana dan Allah!" Bugawa kirjin Hawwa yafara kaman zai fashe, Ni'ima tace "baki bani Hawwa!" Sake bugawa zuciyan Hawwa tayi, Ni'ima tace "karki kara tako kafanki zuwa gidana!" Shaking at this point zuciyan Hawwa yafara, Ni'ima tace "kada ki kara zuwa nemana a asibiti!" Hawaye fara tsatsowa daga idanun Hawwa sukayi, Ni'ima tace "delete number mijina daga wayanki, koda wasa kada ki sake ki kira mijina for anything, delete my number also!" Ni'ima tace "don't ever call me again or watsapp me ko message me, I'm blocking you anyway!" Tasauke ijiyan zuciya tace "amutunce nakeso muyi parting ways with dignity and honor like the matured girls we are saisa ma harna kiraki to tell you to your face" Ni'ima tai shiru tace "Allah baice dole sai anyi kawance har karshen duniya ba, haduwan school, ba dangin iya bare na kaka, kawancen mu muka daurama kanmu ba wani yadaura mana ba mumukaga zamu iya, yanzu kuma naga bazan iyaba is that simple Hawwa, dan haka stay away from me! It's OVER!"

Yanda kalaman Ni'ima ke hitting kan Hawwa kaman ana daukan guduma ana bugamata aka, she's feeling like she's dreaming this is not real, ba Ni'ima ke mata all this maganganu ba, Ni'iman ta dake sonta, Ni'ima dake tayata kuka idan she's sad, Ni'ima dake lallashinta, Ni'ima dake kula da ita, is this Ni'ima ko watace tasaka facemask takoma Ni'ima? Best dinta ke cewa su rabu?
Juyawa Ni'ima tayi tasa hannu tadauki jakanta tace "kinfi kowa sanin yanda nakeson Aliyu, mijina is a no no! Akan Aliyu zan iya jama kowa layi!" Tai shiru sannan tace "Hawwa najamiki layi kema yau get out of my life" daukan jakan tayi tajuyo takalli Hawwa da idanunta suka cika tap da hawaye da basu riga sun zuboba tasa tace "Ma'assalam Hauwa'u" tajuya tayi tafiya one two zata wuce tafita Hawwa tasha gabanta daidai hawayen na zubowa daga idanunta tasa hannu ta gogesu da sauri, asanyaye tace "Ni'ima!" Haderai Ni'ima tayi idanunta sunyi jajir hakanan kawai yau for the first time saitaji tafin hannun Hawwan ma taushin tsiya kaman na Baby so that means har taushin hannu Hawwa tafita, kishi ne ya turnuke Ni'ima sosai sai kawai take ganin so many many things da Hawwa kedashi that are better than hers, kabar da hannun Hawwa tayi daga jikinta da sauri dan har zafi taji kaman Hawwa tasamata garwashi ajiki Ni'ima tace "karki sake tabani" tabi ta gefenta ta wuce tsayuwa Hawwa tayi kaman gunki idanunta sun cika da hawaye bazata iya decribing yanda takeji ba yanzu, juyawa tayi da sauri gudu gudu tashiga sauka daga bene hawaye na fitowa daga idanunta tayi waje tana kallon Ni'ima dahar takai parking space dasauri tafito wajen bata damu da manya manyan motocin dake

wajen ba dan manyan mutane na zuwa restaurant din sosai Ni’ima na kokarin ciro key a handbag dinta tabude mota Hawwa tazo wajen da gudu ta rungume Ni’ima tabaya tabude baki tana kokarin magana kawai emotions got her wlh tafashe da kuka! She can’t describe it but tanason Ni’ima so sosai! Bawai irin son da akema namiji ba dan some people think maza kawai akeso no, tanama Ni’ima wani so da kauna na jini dan Ni’ima ta taka rawan gani arayuwanta sosai.

Tama kasa magana sabida kuka she’s not even thinking of inda suke, ko mutane ko jam’an wajen, she’s strong, she’s hard, kowama yasani but akan Ni’ima she’s not, she even forgot wat strong is dataji Ni’ima nacewa zata rabu da ita, kusan 30seconds tayi abayanta tariketa tana kuka, yau kawai kaman Allah nabama Ni’ima revelation kan Hawwa dan kawai jitayi komi na jikin Hawwa taushi kaman ba jikin yar 30yrs ba kaman jikin new born baby haka taji fatanta, juyowa Ni’ima tayi a fusace ta hankadeta saida Hawwa tai flying ta bugu da wani mota dake wajen next to na Ni’ima, tai kara awahale ta kalli Ni’ima idanunta sunyi jajur tana kokarin tashi daga jikin motan dan kaman bayanta ya karye haka taji, Ni’ima tanunata da yatsa da zafi sosai kan tone nata tace “Hawwa ke na tsaneki yanzu don’t you get it? Narike inata holding nashi in banaso na gayamiki but kin nace, I hate you Hawwa! I hate you! Jikinki da hannunki feels like garwashin wuta ajikina, karki kara tabani” daidai lokacin taga key motanta ta ciro tajuya tabude motan zata shiga Hawwa ta tashi daga jikin motan da kyar bata damu da ciwon da jikinta keyi ba kawai saitai kneeling tareda rike rigan Ni’ima muryanta na rawa same thing da jikinta rawa suke sosai tana kuka wiwi tace “Ni’ima I don’t know ta yanda zanzo na fara rayuwana without you, ke kadai gareni, rayuwana yariga yasaba dake, ke kadai gareni, I have no one to talk to, I will never ever betray you Ni’ima, I’m not ready to let go of our friendship, Best remember our lives, we’ve come a long way don’t abandon me, dan Allah kiji tausayina Ni’ima don’t abandon me, you’re my special thing, Ni’ima kiyakuri kiyafemin, don’t abandon me, I’m your friend Ni’ima” juyowa Ni’ima tayi aharzuke tace “friendship din banza da wofi what is friendship? Uban friendship! Ke uwar friendship, durun uwan best friend, tare aka haifemu da bazan rabu dake ba? Ke ki kyaleni we are not related, dole ne? Better accept that weren’t not friends anymore, let it sink in your head move on, I’ve move on too” tashiga fizge riganta zata shiga mota Hawwa taki saki tana girgiza ma Ni’ima kai hawaye na fitowa daga idanunta sosai jikinta na rawa like a little gurl, tana kuka tace ““Ni’ima you are the only person I have, Sisters dina are not close to me duk na girmesu, ko sunaso suzo kusadani Umma bata barinsu, banda Mama, there’s no one arayuwana banda ke, you’re the reason I’m not lonely nor depressed, kika barni Ni’ima yazanyi? Who will look after me? Who will love me like you? Wazaimin fada idan naji ciwo? Wazai bani

magani? Wazai kirani? Ni’ima I’m sorryyy” ahaukace Ni’ima tace “au bazaki sakeni ba Malama”? Gyadamata kai Hawwa tayi tama kasa magana sabida kuka, idanun Ni’ima sun rufe tasa kafanta tashiga tattake hannun Hawwa da takalminta Ganin taki saki yasa tasa wajen heels na takalmin ta take hannun Hawwa da karfi hakan yasa dasauri Hawwa ta saketa sabida zafin da hannunta yamata tana kuka ta shiga mota tai reverse tabar wajen Hawwa tabi motan da kallo zuciyanta nawani kalan tsinkewa tana yarfe hannunta dake jini.

FRIENDSHIP BREAKUP HURT 😔

KISHI IS REAL! BAKOWA KEDA KARFIN CONTROL KISHI BA 😭

ABINDA NI’IMA TAYI TA KYAUTA???

WAI IS IT THIS EASY AYI BREAKING UP???

SHIKENAN NO MORE HAWWA AND NI’IMA SABIDA NAMIJI??

KAI MAZA BAKUYIBA BABAN YASEER SINGLE HANDEDLY RUINED THIS BEAUTIFUL FRIENDSHIP 😭

BUT BABAN YASEER KO NI’IMA KO HAWWA WAYE KEDA LAIFI???

EPISODE 2️⃣8️⃣

Sosai take yarfe hannunta sabida yanda yake mata zafi jini na diddiga takasa motsi daga wajen tana kuka har saida security guard sukazo wajen daya rikeda bag nata da phone yace “Ma’am is everything okay your hand is bleeding we believe this is your own” yamika mata jakanta da wayanta, hannunta mai lafiya takai ta goge fuskanta tass but dudda haka idanunta sunyi jazur alamun kuka

sannan takai hannun daman kasa tana kokarin mikewa dan bayanta ciwo yake mata da dabara ta iya mikewa tsaye but tsabagen yanda batada karfi kawai ta luuuuu tai baya runtse idanunta tayi gam kawai ta sadakar tafadi charab taji an tareta tafada kan hannun dataji daya a waist nata daya a shoulder ta, ga kamshi mai bala'in dadi dake ratsa hancinta, almost 10secs tayi batai motsi ba kuma ba'a saketa ba kafin gently tafara bude idanunta dahar yaji yaji suke mata sabida kuka ta sauke rinannun idanun nata acikin na Khaleel dake kallonta awkwardly gadan toothpick abakisa tana iya hango kirjinshi sabida yanda baisa boturan gaban shirt nashi ba as usual, wani irin zabura tayi tafita daga jikinshi cikeda tsana tajuya ta karbi wayan nata da bag daga hannun security zata wuce cikin yar iskan voice yace "so you're into gurls? I see no wonder kike tsani maza" tsayawa tayi tana kallon gefenta zuciyanta namata radadi, Khaleel yazo gefenta yakai hannu yana zare toothpick daga bakinshi cikeda neman tsokana irin na yan iskan yara yakai hannunshi gaban fuskanta yana waving yace "I feel sad she shatter your heart" yamata wani dan iskan kallo yanadan murmushi, Hawwa kawai ta tawuce da sauri tana share fuskanta dan yau batada karfi, daga murya Khaleel yayi yace "seeing you like this is so satisfying" bude motanta tayi ta shiga ta tada motan taja da mahaukacin gudu tabar eatery kuka kawai take hannunta na mata radadi har lokacin jini na fita though ba sosai kaman d'a ba.

Ana magrib a masallaci takai gida Baba bayanan yana masallaci, fitowa tayi ahankali cus bayanta namata ciwo tarufe motan tashiga gida, daki tawuce ta zauna gaban madubinta tana jawo drawer tadauki spirit tazuba a tsakiyan hannu kara tayi tana fashewa da kuka sosai sannan tasa auduga ta goggege ciwukan hannunta, bottle water dake wajen tadauka tana kallo sai alokacin ta tuna tana azumi goge fuskanta tayı da bayan hannu takai ruwan baki tasha, ta lallaba tamike tafito tadauro alwala tadawo tahau kan dadduma tai salla, ta kwanta kan dadduma tana kallon saman dakinta bini bini tana goge hawayen dakebin fuskanta, saikuma chan tamika hannunta tadauki wayanta tai dialing number Ni'iman amman baya shiga busy busy taje watsapp tamata message baya shiga taga bata ganin DP dinta yau, blocking dinta kenan tayi.

Rawa hannayenta suka fara cus in wildest dream nata bata taba tunanin Ni'ima can block her ba, tadauka duk maganganun datake dazu fushi ne, blocking dinnan hit Hawwa daban kawai tafashe da kuka tayi harta godema Allah, kawai saitaji rayuwan yamata daci, bazatai karyaba harda Ni'ima as part of the reason da bata damuwa da rashin aure, sabida tana debe mata kewa, waya, chatting, labarai abinda yafaru wajen aiki da sauransu, zuwa outing all those abubuwa makes her forget about actual problem nata, kanninta duka sunyi aure banda ita, gabaki dayan layinsu itace babban dabatai aureba kannin kanninta sunyi aure, hannunta dake mata zugi da Ni'ima ta taka da takalmi tadaga ta kalla sai kawai ta

lumshe idanu hawaye na zubomata daga ido masu zafi tawani kanannade kanta a dadduma kaman macijiya ahaka aka kira isha'i ta lallaba tayi tareda shafa'i da wuturi

Wayan takara dauka tasake dialing number Ni'ima but busy wayan nata tadaura akan fuska tafashe da kuka mai zafi hawaye na diddiga akan screen na wayan for all this years da abubuwan dake faruwa da ita bata taba feeling broken ba like yau, yau jitayi da defense system nata da will of power nata da komima ma yayi breaking she's weak, cire wayan tayi daga kunnenta tai dialing number Ammi ringing daya Ammi tadauka tace "Hawwa yaya how is your Monday? Kindawo daga aiki? Ya Baban naki ince bai cigaba da rigima dake b……." Rage murya tayi sabida yanda takejin sheshekan kukan Hawwa
Lumshe idanu Ammi tayi rabon dataji kukan Hawwa haka tun zamanin rasuwan mahaifiyarta cikeda so tace "Baba ne" girgizamata kai Hawwa tayi tace "Ammi Ni'ima tarabu da… da….d….." takasa magana ma tsabagen kuka zuciyan Ammi bugawa ya shiga dan wlh tanason Hawwa sama da nata yaran ma bata wasa da ita, dasauri Baffa dake gefenta yace "Malam yasake mata wani abu ne?" Girgizamai kai Ammi tayi tamai alamu daya dakata tana sauraron yanda Hawwa kemata kuka batama iya magana ahankali Ammi tace "Hawwa ya isa, kukan ya isa haka? So kike hankalina yatashi nashigo hanya da daddaren nan?"
Girgizamata kai Hawwa tayi Ammi tace "calm down Hawwa komi yayi zafi maganinsa Allah, kowace kaddara daga Allah yake, it's okay Hawwa na, it's okay kinji, ya isa hakanan ya isa"
Akwai wani kalan natsuwa da kalaman Ammi ke bata ahankali tasoma rage kukan Ammi tace "meya faru tell me everything" da kyar ta iya fadama Ammi komi dudda kuka nafin karfin maganan nata but still Ammi manage to understand komi, wlh deep down tasan za'ai haka, ahankali ta zauna abakin gadon idanunta sun ciko da hawaye da sauri Baffa ya girgiza mata kai alamun kartayi she will break Hawwa even more, hadiyesu tayi tace "Ni'ima is angry I understand don't pay attention to much to maganganun ta, itama ko'ina take im sure tanachan tana kuka kalan wannan dakikeyi, kunyi building strong relationship da Ni'ima da banjin zaiyi breaking hakanan ba just give her some time Hawwa, and stop crying"
Ya isa ya isa, Ammi tai maganan cikeda tausasa zuciya maganganu masu dadi tashiga gayama Hawwa ahaka bacci yayi awon gaba da ita anan kasa kan dadduma. Ammi ta katse wayan takalli Baffa dayaji komi tace "nakira Ni'iman?" Gyadamata kai yayi dialing number Ni'ima tayi wayan yayi ringing harya katse ba'a dagaba saita sake kira but busy itama ansata a blacklist takira kusan 5times but haka zata sake kira Baffa yace "ya isa! Basai kin sake kiranta ba, bakomi rayuwa ce, bari zan ma abokanen aikina magana idan zan iya samana Hawwa wani aikin ağarın nan saita

dawo nan zaria ta manta da damuwanta”
Around 5 ta Hawwa ta tashi cikinta namata ciwo dana yunwa dana MP, bayanta shima na ciwo, kayan aiki ta da bata cire jiyaba tacire ta daura zani tafito, wanka tayi da brush da alawala tadawo ta shirya yau cikin simple office gown black tasa tai salla, tadauki black shades tasa cus idanunta sun kumbura sosai tawuce tafito Baba na masallaci, warming Mota tayi kafin taja motar tabar anguwan, Awani eatery ta tsaya tasai abinci, koda ta shigo office nata tabude abincin tagumi tayi tana kallon food din, saiga hawaye sharewa tayi dasauri takai hannunta tasake daga wayanta tai dialing number Ni’ima but busy tayi blocking nata true true, ijiyan zuciya ta sauke gwanin ban tausayi ta debi rice din takai baki da kyar ta hadiye baya mata dadi bakinta is just dry, rufe takeaway tayi ta ijiye agefenta tai shiru tana kallon waje daya tunani kawai take, rannan takasa komi har saida aka bata break cus tace batada lpy and kowa yagani kam she looks sick da kyar take tafiya DIG yace taje taga Dr tahuta cus Hawwa is strong bata fashi, she’s serious da aiki he needs her healthy.

Around 1 takoma gida Baba na zaune awaje ya ganta

Da sauri ya yunkuro yana kallon yanda tai parking tafito ahankali tana daukan jakanta da kyar, ganin yanda fuskanta yayi jajir hakama hancinta yasa dasauri yayi wajenta kafin tama iso yace “meyasameki awajen aiki Hawwa?” Ahankali asanyaye tace “banda lpy ne Baba” dasauri ya shiga kama crutches nashi a hammata yakai hannunshi yana taba goshinta yace “subhanallahi sannu Hawwa kinsha magani konasa asayo miki”? Ahankali tace “eh nasha” cikeda damuwa yace “assha sannu, sannu kinji, kawo jakan muje ciki” yakarbi jakan yana ratayawa a kafadansa sukai ciki…

Har gaban dakinta saida yaga tabude ta shiga ciki sannan yawuce kitchen da kanshi ya shiga bude bude yadebo mata shinkafa da miya a kwano da zafinsa yafito yazo gaban dakin yana bugawa yace “nashigo”? Ahankali ba karfi a muryanta tace “eh” kofa yabude ya shiga da plate na abincin a hannunsa tashi zaune tayi dan tana shiga kwanciya tayi ko kaya bata cireba yabata abincin yace “ci, ci idan zazzabin bai kwanta ba saina kaiki asibitin su Ni’ima” sunan Ni’ima da Baba yakira kawai saiga hawaye sha hankalin Baba yatashi da sauri yaja kujera ya zauna gaban fadin yana ijiye crutches dinsa yace “Hawwa menene eh? Meke damunki? Wlh na hakura tunda kin nuna baki kaunar Alhaji Kabiru nimadai naga yamiki tsufa nafasa bari ki aureshi kinji, kiyakuri kome nagaya miki kwanakin baya eh Hawwa na, ya isa kukan, dena dena” yakai hannunshi yana sharemata fuska ta bala’in bashi tausayi, yashafa kanta yace “to ya isa ci abincin abinki ko kadan ne” yanda Baba yadamu yasa tadebi kadan takai bakinta da kyar tahadiye, yanda

yaga tanayi yasa yace “kawo abincin bari naje nasayo kaza sai asoya miki kici abarbada cabbage da yaji da tumatir haka mahaifiyarki keson kaza” murmushi tamai kadan, tashi yayi yana dafa bango yasa mata filo akan gadon yace “kwanta da kyau kinji” kwanciya tayi yace “karki rufa jikinki na zafi” gyadamai kai tayi Baba yadauki abincin yana kallonta yawuce yafita yana gyaramata labule.

EPISODE 2️⃣9️⃣

Baccin ma dataso tayi batayishi ba yaki zuwa, wajajen 4 ta tashi ta chanza kaya zuwa abaya tadauki car key tafito Baba na zaune a tsakar gida yana wanke kaji shi kadai gaban pampo ganinta yasa yace “ina zaki ya jikin”? Ahankali tace “bari nadan sayo magani Baba” da dan damuwa ya gyadamata kai yace “toh shikenan kije karki jima” gyadamai kai tayi tafice shiga mota tayi ta tada tawuce gidansu Ni’ima babu wani nisa sosai daga layinsu shiga layin tayi har zuwa gaban gidan tai parking tafito tashiga da sallamanta, Mama na zaune a tsakar gida tana gyara wake itada yar makotansu da aka aiko yaranta duka sunyi aure yar aikin ta kuma ta aiketa tana ganin Hawwa tai dan murmushi tace “ahh yau su Hawwa ne agidan” shigowa ciki Hawwa tayi cike da girmamawa tace “Mama ina yini” murmushi Mama tayi tace “lafiya lau ya kike Hawwa yasu wajen Baban naki” ahankali Hawwa tace “lpy lau” tazauna awajen tai shiru takasa magana kaman wata marainiya, Mama ta kalleta sosai tabata tausayi dan tausayi duktai wani iri, yarinyar dake zaune Mama ta kalla tace “tafi Husna ki gaida Mamanki kice mata zan shigo anjima” tashi yarinyar tayi tafita, Mama ta kalli Hawwa tace “sabida Ni’ima kikazo ko?” Gyadamata kai Hawwa tayi, Mama tasauke ijiyan zuciya tace “Hawwa dagake har Ni’ima ba yara bane, tariga ta sanar dani komi dake faruwa, she’s just trying to protect her home so I think is best idan kinyi respecting decision nata and give her space datake so, idan tanaso kudawo da kawancen zata nemeki, don’t blame her rayuwa yazama abin tsoro, sai ana sara ana duban bakin gatari fa, kibarta and move on ba dole Hawwa, tunda abu yakai ga haka kifita daga rayuwanta kinji” sosai Hawwa ke kallon Mama dake maganan irin ko ajikinta dinnan, wani iri Hawwa taji hawaye na taruwaa idanunta, Mama tace “kidena nacin nan dan Allah antaba kawance dole? Yo amintan dole ne? Idan kuma kin nace sai kinyi to kema Hawwa ki yarda da mijin da Baba yamiki mana Malam Kabiru kiyi auren kowama yahuta kinayi nasan Ni’ima zata dawo gareki, kinji kiyi tunani akan abinda na fadamiki” Hawwa takarayin shiru zaune awajen akasan simenti, Mama tace “tashi to kitafi” ko motsi Hawwa takasa yi, Mama ta tabe baki tace

“Allah kyauta, tashi kije dan Allah nima kada ki sake zuwan gida, wacce ta hadamu tace batayi, kowa nasa yasani aduniyan nan ba’a kuma dole, just don’t take it personal, Ni’ima is protecting her space ibada take, a musulunce miji yafi kawa sau dubu ko nine mijina zan zaba bawata kawaba ana zaune lafiya, yanda kikeda wayau da ilimin nan ko kece a situation din Ni’ima haka zakiyi wlh put yourself in her shoe, y’ata ta samu gidan hutu yo idan kawa zata mata summun bukumun basai aja mata layi ba kowa yayi takansa? Kingani saida safe bari nahadama Malam abincin dare” tawuce kitchen abinta, Hawwa kawai tafashe da kuka da kyar ta dafa bango ta mike bayanta har yanzu ciwo yakemata fita tayi ta shiga motanta, taja ahankali tabar unguwan takoma gida.
Baba bayanan but tana shiga dakinta taga ya ijiye mata kula zama tayi ahankali tabude kulan kaza ce ta soyu ansaka kulikuli da yaji gasu cabbage, tana ganin girkin tasan Baba yadafa mata dama yace dayana saurayi yayi sana’an balangu da su gasassun kaji, hannu takai ahankali tadauki daya takai bakinta daidai nan Baba yayi sallama ya shigo yana rikeda leda ganinta zaune gaban kulan yasa yayi murmushi yace “yauwa Hawwa gashinan naje bakin hanya na sayomiki chivita na grape mai sanyi, ranan nan na dandanashi yamin dadi zakiso shi”

Yazo yazauna kusada ita yana ijiye karafunan a gefe lumshe idanu Hawwa tayi jin Baba ya zauna kusada ita tabude su tana ganin yanda duk yadamu yana bude mata juice din, this is the first time takejinta so vulnerable she’s tired of being a strong girl, komima na duniya yamata ahankali tadaura kanta jikin hannun Baba gently tasaka hannunta takama hannunshi ta kankame sosai a kirjinta tafashe da kuka mai tsuma zuciya, bala’in tashi hankalin Baba yayi dasauri yajuyo yace “Hawwa, ke, Hawwana? Me akamiki mesa kike kuka haka? Hawwa” sheshekan kuka take jikinta har rawa yake tarike Baba sosai takasa magana dasauri Baba yadago kanta saikuma yajuyo da kyau idanunshi sunyi jaa yace “zonan Hawwa zo” yajawota yasata a kirjinshi tai hugging Baba so tight this is abinda bata tabayiba hugging Baba saidai maybe datana yarinya, bayanta Baba yashiga bubbugawa yace “ya isa Hawwa ya isa, zakisa hankalina yatashi, koma menene ke damunki baifi karfin Allah ba, ya isa Jiddalo na, ya isa, yi shiru yi hakuri kinji, kinada matsala awajen aikinki ne?” Girgixamai kai tayi alamun a’a tana tsagaita kukan tana sauke ijiyan zuciya ba kakkautawa a kirjin Baba, ahankali yace “to menene ke damunki”? Murya chan kasa tace “Baba aure nakeso nayi nagaji da yanda kowa keyi dani sabida banyi aureba” ahankali Baba na buga bayanta yace “karki damu zaki aure, anmini kwatancen wani Malami na Islamic chemist ranan asabar tunda ba aiki zan kaiki muje muji ko aljanu gareki dake hanaki aure, kokice baki sonsu kosu sugudu zamuji dalili kidena damun kanki namiki alkawari bazan kara takura miki ba, lafiyanki yafi komi mahimmanci agareni Hawwa na, kiyakuri kinji yarinyana yar albarka kiyakuri da rayuwa, komi tsari ne na ubangiji kizama

mai juriya da hakuri akwai Allah Hauwa’u kinji” gyadamai kai Hawwa tayi, Baba yayi shiru chan yadago ta daga jikinshi yace “zafin jikinki ya baci kinsha magani kuwa?” Gyadamai kai tayi ahankali Baba yace “to zai sauka, sha lemon kici naman bari naje masallaci, kada kuma kisake kuka kinajina” gyadamai kai tayi yadafa gadonta yana mikewa daukan crutches din tayi tabashi ya karba yafice tabishi da kallo saikuma ta kalli abincin bata iyaci, wayanta ne yahau ringing da mugun sauri takai hannunta ta dauki wayan Ammi tagani a screen sanyi jikinta yayi tadauki wayan Ammi ma sake kwantar mata da hankali tayi sun sade suna waya ahaka bacci yayi gaba da ita koda Baba yadawo ganin tayi bacci yawuce yana jawo mata kofa duk ya damu ganin bataci abinci ba. <This message was edited>

EPISODE 3️⃣0️⃣

Washegari around 5 ta farka da ciwon kai har bata iya bude idanu da kyau, gashi tai staining kayanta da wajen abinda bata tabayiba, ta tashi tacire kaya da zanin gadon batada karfin wanki a basket na laundry tasa, tasake kwanciya ko daga kafa tayi saitaji akanta, tana ahaka Baba yayi knocking da sallama da katuwan muryan nan nasa yace “zan shigo” kofan yabude ya shigo dakin yaganta kan gado hankalinshi yakara tashi ganin sosai Hawwa fa batada lpy, batama iya bude idanu, cikeda damuwa yace “Hawwa na” yazo wajen gadon yana dagota jikinta kaman fire Baba yace “subhanallahi, Hawwa zoki lallaba kiyi wanka muje asibiti, kokuma bari kiga nakira Ni’ima” wayansa yaciro daga aljihu yashiga kokarin kiran Ni’ima Hawwa na kallonshi da kyar harya katse bata dagaba yace “bata dagaba bari kinsan asuba ne hala bata tashi ba, bari nasake kira” yasake dialing number saiya cema Baba busy kusan sau 4 yana trying yace “busy busy yake gayamin” dan murmushi kadan Hawwa tayi ganin shima Baba tai blocking nashi, cikeda karfin hali muryanta baya fita da kyau tace “Baba karka damu bari naci abinci zan lallaba naje asibitin nasu adubani” gyadamata kai Baba yayi yajuya yace “shirya wankan bari nahada miki ruwa” sosonta yaduka yadauka yafita yana dungura sanda yashiga kitchen Umma na kitchen din ta banka uban tsaki ko kallonta baiyiba, ruwan da aka ijiyemai nashi na wanka yajuye mata yadauka yafito yatara na sanyi ruwan yayi dalam dalam dan jikinta akwai zafi sosai yakaimata bayi sannan yadawo dakin yabuga mata yace “fito Hawwa” fitowa tayi da hula akanta ahankali take tafiya tana dafe kanta da hannu daya hannu daya tana dafe bango, Baba yakama hannunta gwanin ban tausayi ya jinginata a bangon wajen yaci bari nakawo miki kujera, kujera ya dauko yasamata abayin sannan ya shigar da ita yarufo mata kofa, bata taba sani ana irin ciwon kan nan aduniya ba,

kowani motsi tayi sai kan ya amsa, tadan jima tabude kofan Baba na jiranta, brush yabata daya koma daki yadauko mata tayi yariketa yakai daki ya zaunar kan gado, Allah sarki da kanshi yabude sip yazaro mata yar doguwan rigan da yagani na atampa green, ya ijiye mata kusada ita, tabishi da kallo yanda yake dingisawa yadauko mata mayyukanta yakawo gadon ya ijiye duka kusada ita murya chan kasa yace “sa kaya ganinan zuwa” yawuce yafita, da kyar ta tashi tadauko su pad, pant bra tashiga shiryawa ahankali tasaka green atampan da Baba yadauko, dogon riga very simple yet stylish dinki dan har collar gareshi rigan, ta zauna ahankali kome zatayi kaman kanta zai fadi, dan karamin gyalenta green ta dauka ta yafa tasake kwanciya agadon Baba yashigo da shayi a hannu yazo gadon yazauna kusada ita yace “zoki sha muje” hannu tadagamai alamun bazata iyasha ba, tana lumshe idanu saikuma dan gajeren bacci yayi gaba da ita wuraren 7 ta farka, jikinta har kyarma yake sabida zazzabi kaman ana tsinka hanjin cikin jikinta, idanunta sunyi jajir, gyalen tasake dauka tayafa dan bazata iya daurin dankwali ba ta lallaba ta mike tana daukan wayanta da handbag da car key a hannu tasaka flat shoe black tafito, Baba na compound tafito yamike dasauri yataho da sauri yana kallonta yace “kin tashi” dan murmushin karfin hali tamai tace “bari naje asibitin su adubani” Baba yace “zaki iya tuki kuwa da ciwon kan nan”? Murya cha kasa tace “zan iya Baba karka damu” har mota yarakata ganin hankalinshi bai kwanta ba da fitan ita kadai yasa ahankali tace “Baba ko Ni’ima zata iya dawo dani kazauna kaji” gyadamata kai yayi ya maida mata kofan yarufe ta tada motan taja Baba yabi motan da kallo.

Ahankali take tukin, da kyar take iya bude idanu har jiri jiri take gani amman sabida karfin hali haka tashiga hanya jikinta kaman wuta, ko kadan bata gudu sosai cus jiri take gani, har layi take, hospital nasu na yan sanda takeso taje tunda Ni’ima tace tadaina zuwa hospital nasu wanda shine hospital datake using idan batada lpy, sunkai wajen traffic light na zone 3 ta tsaya tana jiran yakai turn nasu tawuce, dan tsayawan kawai yasa taga idanunta sun fara ganin duhu, kawai idanunta suka fara kukkullewa suna firfir, internally taji kaman an kunna wani engine na vibration a jikinta, kawai jikinta yafara rawan da bata iya controlling tana fisfisgewa tafara convulsing.

Bakin rigiman Noor yasa yau yatashi da wuri cus tace shizai kaita school, tunda suka shiga motan nan surutu takemai, ganin an kirashi yafara waya yasa ta barshi tawuce window tamike tsaye tana kallon hanya ganin sun tsaya chak, motan dake next to them a layi yar corolla data tsufa ba irin tasu ba ta kalla, ihu tayi tace “Dady loook someone is sick, Dady someone is shaking, I think is Fairy Angel Anty, Daddy!” Yarinyar tai ihu dayasa Khaleel yadan dakatar da wayan dayake yazo wajen yace “Princess menene”? Leko da kanshi yayi shima idununshi suka sauka kan Hawwa dake

convulsing ita acikin mota ita kadai kanta na karkacewa yawu nabin gefen bakinta, daidai tawani mike ta sandare ta danna gear motanta yayi gaba yana arnen gudu jikake kakakakaka!!!! Motanta yana dukan motocin dake gabanta with speed…
Dawani irin gudu Khaleel yabude bayan motan yafito yanabin motanta da gudun bala'i acikin traffic din nan some people ma nafitowa dan some people ma haka dan anga Hawwa na convulsing, every gudu da Khaleel yake he's telling her in his mind don't die! Don't die! Saida motanta yahada 5good cars suna gudu saida sukakai jikin wani trailer ne akai gwarap! Dole motocin suka tsaya hakama nata ya tsaya but still pushing nata keyi sabida kafanta, glass na gaban motanta ya tarwatse, lafiyayyen accident Hawwa ta hada, Khaleel yana zuwa wajen motan nata dake hayaki sosai yashiga budewa jama'a nataruwa ana tayashi budewa ana zuwa wajen sauran motocin yana kallonta Khaleel yana kokarin bude motan yanda har airbag na motan yafito, bude motan yayi nasaran yi yashigo jini nabin hannuwanta da goshinta ya zare sitbelt dinta, Hawwa tafado jikinshi tana convulsing, dasauri yariketa yana zare kafafunta daga gear, lips nata na jini sabida yanda take biting nasu zata cigaba dasauri Khaleel yakai hannunshi yasa abakinta ta shiga tattaunewa, daidai Salman da bodyguards nashi da mopol dinshi na zuwa wajen, rike Hawwa yayi gam ajikinshi yace "Salman pay all damages, I'm taking her to the hospital!".

EPISODE 3️⃣0️⃣

Washegari around 5 ta farka da ciwon kai har bata iya bude idanu da kyau, gashi tai staining kayanta da wajen abinda bata tabayiba, ta tashi tacire kaya da zanin gadon batada karfin wanki a basket na laundry tasa, tasake kwanciya ko daga kafa tayi saitaji akanta, tana ahaka Baba yayi knocking da sallama da katuwan muryan nan nasa yace "zan shigo" kofan yabude ya shigo dakin yaganta kan gado hankalinshi yakara tashi ganin sosai Hawwa fa batada lpy, batama iya bude idanu, cikeda damuwa yace "Hawwa na" yazo wajen gadon yana dagota jikinta kaman fire Baba yace "subhanallahi, Hawwa zoki lallaba kiyi wanka muje asibiti, kokuma bari kiga nakira Ni'ima" wayansa yaciro daga aljihu yashiga kokarin kiran Ni'ima Hawwa na kallonshi da kyar harya katse bata dagaba yace "bata dagaba bari kinsan asuba ne hala bata tashi ba, bari nasake kira" yasake dialing number saiya cema Baba busy kusan sau 4 yana trying yace "busy busy yake gayamin" dan murmushi kadan Hawwa tayi ganin shima Baba tai blocking nashi, cikeda karfin hali muryanta baya fita da kyau tace "Baba karka damu bari naci abinci zan lallaba naje asibitin nasu adubani" gyadamata kai Baba yayi yajuya yace "shirya wankan bari nahada miki ruwa" sosonta yaduka

yadauka yafita yana dungura sanda yashiga kitchen Umma na kitchen din ta banka uban tsaki ko kallonta baiyiba, ruwan da aka ijiyemai nashi na wanka yajuye mata yadauka yafito yatara na sanyi ruwan yayi dalam dalam dan jikinta akwai zafi sosai yakaimata bayi sannan yadawo dakin yabuga mata yace “fito Hawwa” fitowa tayi da hula akanta ahankali take tafiya tana dafe kanta da hannu daya hannu daya tana dafe bango, Baba yakama hannunta gwanin ban tausayi ya jinginata a bangon wajen yaci bari nakawo miki kujera, kujera ya dauko yasamata abayin sannan ya shigar da ita yarufo mata kofa, bata taba sani ana irin ciwon kan nan aduniya ba, kowani motsi tayi sai kan ya amsa, tadan jima tabude kofan Baba na jiranta, brush yabata daya koma daki yadauko mata tayi yariketa yakai daki ya zaunar kan gado, Allah sarki da kanshi yabude sip yazaro mata yar doguwan rigan da yagani na atampa green, ya ijiye mata kusada ita, tabishi da kallo yanda yake dingisawa yadauko mata mayyukanta yakawo gadon ya ijiye duka kusada ita murya chan kasa yace “sa kaya ganinan zuwa” yawuce yafita, da kyar ta tashi tadauko su pad, pant bra tashiga shiryawa ahankali tasaka green atampan da Baba yadauko, dogon riga very simple yet stylish dinki dan har collar gareshi rigan, ta zauna ahankali kome zatayi kaman kanta zai fadi, dan karamin gyalenta green ta dauka ta yafa tasake kwanciya agadon Baba yashigo da shayi a hannu yazo gadon yazauna kusada ita yace “zoki sha muje” hannu tadagamai alamun bazata iyasha ba, tana lumshe idanu saikuma dan gajeren bacci yayi gaba da ita wuraren 7 ta farka, jikinta har kyarma yake sabida zazzabi kaman ana tsinka hanjin cikin jikinta, idanunta sunyi jajir, gyalen tasake dauka tayafa dan bazata iya daurin dankwali ba ta lallaba ta mike tana daukan wayanta da handbag da car key a hannu tasaka flat shoe black tafito, Baba na compound tafito yamike dasauri yataho da sauri yana kallonta yace “kin tashi” dan murmushin karfin hali tamai tace “bari naje asibitin su adubani” Baba yace “zaki iya tuki kuwa da ciwon kan nan”? Murya cha kasa tace “zan iya Baba karka damu” har mota yarakata ganin hankalinshi bai kwanta ba da fitan ita kadai yasa ahankali tace “Baba ko Ni’ima zata iya dawo dani kazauna kaji” gyadamata kai yayi ya maida mata kofan yarufe ta tada motan taja Baba yabi motan da kallo.

Ahankali take tukin, da kyar take iya bude idanu har jiri jiri take gani amman sabida karfin hali haka tashiga hanya jikinta kaman wuta, ko kadan bata gudu sosai cus jiri take gani, har layi take, hospital nasu na yan sanda takeso taje tunda Ni’ima tace tadaina zuwa hospital nasu wanda shine hospital datake using idan batada lpy, sunkai wajen traffic light na zone 3 ta tsaya tana jiran yakai turn nasu tawuce, dan tsayawan kawai yasa taga idanunta sun fara ganin duhu, kawai idanunta suka fara kukkullewa suna firfir, internally taji kaman an kunna wani engine na vibration a jikinta, kawai jikinta yafara rawan da bata iya controlling tana fisfisgewa tafara convulsing.

Bakin rigiman Noor yasa yau yatashi da wuri cus tace shizai kaita school, tunda suka shiga motan nan surutu takemai, ganin an kirashi yafara waya yasa ta barshi tawuce window tamike tsaye tana kallon hanya ganin sun tsaya chak, motan dake next to them a layi yar corolla data tsufa ba irin tasu ba ta kalla, ihu tayi tace “Dady loook someone is sick, Dady someone is shaking, I think is Fairy Angel Anty, Daddy!” Yarinyar tai ihu dayasa Khaleel yadan dakatar da wayan dayake yazo wajen yace “Princess menene”? Leko da kanshi yayi shima idununshi suka sauka kan Hawwa dake convulsing acikin mota ita kadai kanta na karkacewa yawu nabin gefen bakinta, daidai tawani mike ta sandare ta danna tootle motanta yayi gaba yana arnen gudu jikake karakakakakap!!!! Motanta yana dukan motocin dake gabanta with full speed… Dawani irin sauri Khaleel yabude bayan motan yafito yanabin motanta da gudun bala’i kaman bashiba acikin traffic din nan some people ma nafitowa dan some people anga Hawwa na convulsing, every gudu da Khaleel yake he’s telling her in his mind don’t die! Don’t die! Saida motanta yahada 5good cars suna gudu saida sukakai jikin wani trailer ne akai gwarap!!! Dole motocin suka tsaya hakama nata ya tsaya but still pushing nata keyi sabida kafanta, glass na gaban motanta ya tarwatse kwasha kwasha kanta na jini hannayenta na jini, lafiyayyen accident Hawwa ta hada, Khaleel yafara reaching wajen motanta yana zuwa wajen motan nata dake hayaki sosai yashiga budewa jama’a nataruwa ana tayashi budewa ana zuwa wajen sauran motocin yana kallonta yana kokarin bude motan yanda har airbag na motan yafito yatareta tagaba, bude motan yayi nasaran yi yashigo jini nabin hannuwanta da goshinta ga some kwalabe ajikinta, ya zare sitbelt dinta, Hawwa tafado jikinshi tana convulsing kumfa nafitowa ta gefen bakinta da yawu, jini nabin gefen goshinta, dasauri Khaleel yasa hannunshi yariketa, yakai hannunshi ya zare kafafunta daga tootle flat slippers nata nafita daga kafafun, lips nata na jini sabida yanda take biting nasu zata cigaba dasauri Khaleel yakai hannunshi yasa abakinta ta shiga tattaunewa tana datse hakoran akansu, daidai Salman da bodyguards nashi da mopol dinshi rikeda bindigoginsu sunzo akahau kallonsu jama’a while ana ciro sauran mutanen da Alhamdulillah babu wanda ya mutu saidai ciwo, rike Hawwa yayi gam ajikinshi yace “Salman pay for all damages she caused, I’m taking her to the hospital!”.

EPISODE 3️⃣1️⃣

Wucewa yayi two bodyguards na binshi abaya daya rike da jaka da wayan Hawwa da Salman yabasu su biyoshi, dayan babu komi a

hannunshi, suna zuwa wajen rolls Royce dinshi suka budemai baya shiga ciki yayi yana rike Hawwa ajikinshi Noor tafashe da kuka tana kallon yanda jikin Hawwa ke fizgewa, Khaleel yace “sauke glass na motan kasa she need breeze” saukewa yayi, driver yayi kwana kawai suka fara gudu a lane din kafin su sami uturn su dauki wani hanya, hannun dogon long sleeve dinshi Khaleel yakai bakinta gently ya goge yawun dake fitowa daga bakinta yana kallonta damuwa sosai akan fuskanshi kaman zai kirata da idanu yace ta farka ta farka tsabagen yanda yake kallonta, Noor na kallonsu tace “she’s biting your hand Dady” murya chan kasa yana kallon Hawwan dake jikinshi yace “she’s sick that’s why” dasauri Noor tace “Dady I love her alot can I take her pain away?” Shiru yayi yana kallon fuskan Hawwan yace “pray for her” yanda Oga yace aje hospital yasa driver yakaisu hospital din Excellency daya gina, hamshakin hospital ne, kallon Hawwa Khaleel yake bayako kyafta idanu, suna parking ana zuwa, karbanta akai daga jikinshi sukai ciki da ita.

Sauka yayi daga motan yabama bodyguard nashi hannu alamun yabashi wayan da handbag din Hawwa ya karba yace “drop Noor a school” yakalli Noor saikuma ya matso ya manna mata kiss a goshi ahankali tace “Dady will my FAA be fine?” Gyadamata kai yayi yace “she can fight! She will fight the sickness trust me” washe baki Noor tayi tace “My FAA is very strong right Dady” gyadamata kai yayi, ahankali tace “Dady please stay with her don’t fight like that day at super market” shiru yayi saikuma yace “you talk too much go to school” yarufe mata kofan yawuce yashiga cikin hospital din zuwa dakin emergency da aka kwantar da Hawwa, wayanta dake hannunshi ne yashiga ringing dasauri yadaga yaga suna Baba, jimmm yayi he remembered Salman yagayamai mutumin baida kafa he’s crippled that means he’s a sick old man idan yatadamai hankali fa? No! Yafadi ahankali.
Yana tsaye awajen rike da wayan harya katse, daidai Nurse tazo wajen da form a hannu ta mikamai tace “Sir can you fill the form or you have to call her family” sabida yagaya musu hatsari tayi yakawota, paper yakalla da nurse din kaman wanda baiso yayi magana yace “I will call the family”, sannan yadanna screen na wayanta ganin babu key yasa yashiga call log nata number daya gani da Ammi yayi dialing ringing daya Ammi tadaga tace “Hawwa na kin dena damuwan ko” shiru Khaleel yayi baisan yanda ake communication da normal mutane ba sai masu kudi yan league nashi muryan matan is so calm, “Hello Hawwa” Ammi tasake magana, dan gyaran murya Khaleel yayi kaman wanda aka bama big task adan hankali yace “she just had an accident Ma’am she’s in the hospital they’re call for her family” “Innalillahi wa innailaihi raji’un, Hawwa tai accident, tana ina kace? Wai Hawwa na? Jidda ake magana?”

Dan sosakai Khaleel yayi yajuya kozaiga security nashi yabasu wayan suyi yatuna yasasu sukai Noor school, murya yar kadan kaman wani bawan Allah yace “yes Ma’am” sai kawai yaji Ammi tafashe da kuka sosai dasauri yacire wayan daga kunnenshi yana dan yatsine fuska irin mehaka takeyi saikuma yaji muryan namiji Babba na Hello Hello maida wayan yayi kunnenshi yace “yes” Baffa yace “bawan Allah awani hospital take? Ya condition nata yake, idanunta biyu ne kahada mu da ita muyi magana” kai tsaye Khaleel yace “she’s very sick, she’s unconscio…..” ai kafin yakarasa maganan yaji kukan mutane dayawa, Baffa yace “ya sunan asibitin”? Ahankali Khaleel yace “Leadway” “to mungode gamunan zuwa, mu muna zaria zankira Babanta yanzu zai taho”
Baba na zaune a kofar gida yaga number Ammi na kiranshi kin dauka yayi chan saiga number mijinta Baffa hakan yasa yadauka yana kokarin mai sallama Baffa yace “Malam yanzun nan aka kiramu da number Hawwa” faduwa gaban Baba yayi sosai bana wasaba yace “Hawwa, Hawwa? Batajin dadi ai taje asibitin su Ni’ima” Baffa yace “wanda yakiramu yace tayi hatsari amman ka kwantar da hankalinka tana asibitin Leadway nan aka kaita katashi kaje ana neman yan uwanta na jini badai musan me ake ciki ba” salati Baba yafara yana sallallami baima tsaya yakarajin wani bayani da Baffa keyiba da sauri yamike yakoma ciki yana salati kaman wanda ya haukace duka kudadensa dabaya kashewa ya tattaro yafito yana salati kawai. “Innalillahi wa Innailaihi Raji’un, Ya Allah Hawwa na, Ya Allah y’ata, marainiyata Ya Allah, Innalillahi Wa Innailaihi raji’un, Allahuma ajirni fi musibati, Lahaula walaquwata illabillahil aliyul azeem” salati kawai Baba yake ko kallon Umma dake tambayanshi lafiya baiyiba yafito luckily saiga keken daya sauke mutane zai juya taresa Baba yayi yashiga yafadamai sunan asibitin yashiga still salati yake.

A gate na asibitin aka sauke Baba ya shigo baya hayyacinsa dauriya kawai yake irin na maza da crutches nashi yake dungurawa yana hoping yana shiga yana kallon asibitin da tunda yazo duniya baitaba ganin asibiti mai kyau irinsa ba yana kara tsorata yana addu’a Allah yarufa musu asiri, Khaleel na tsaye a reception din yana waya Baba yashiga kiciniyar turo Glassdoor dakeda karfi da aka rubuta push ajiki, tsabagen yanda baida karfi kuma yarude baisan sanda karfenshi ya turgude yafita daga hannunshi ba Baba yafadi tim karafunan ma na zubewa dan takalminshi na kafa daya dayake sawa shima yafita yayi tsalle zuwa wani waje, dasauri Khaleel dake waya yadago jin kara ganin tsoho mai kafa daya yafadi hakama crutches nasa yasa dasauri yacire wayan daga kunnenshi yayi wajen kafin others suzo yarigasu yabude kofan yafita da sauri, one thing about him tun yana yaro yanada tausayin masu nakasu any disabled person have a special place a zuciyan Khaleel.
Ahankali yaduka agaban Baba yakai hannayenshi yakama kafadan Baba da jikinshi ke rawa yana ambaton Allah har lokacin sama,

cikeda tausayi yace “sorry” tsayuwa yayi da kyau yana jingina da bango yana kallon fuskan Khaleel dahar ya duka yana kwasanmai crutches din yataso yabashi da sauri, ahankali yace “sorry, are you hurt anywhere”? Yashiga duba Baba yana kakkabemai gaban riganshi yasake komawa yadaukomai slippers nashi wari daya ya duka gabanshi ya ijiyemai Baba yasaka, Khaleel yasake tasowa for the first time yayi hausa ganin kaman mutumin bai gane turenci ba yace “kaji ciwo? Akwai inda kema zafi?” Girgizamai kai Baba yayi yace “thank you Allah maka albarka babu inda kemin ciwo y’ata ne dai ke ciwo” Kaman zaiyi kuka yace “kirana akai y’ata Hawwa tayi hatsari tana asibitin nan ko kasan inda ake tambaya? Ni wama yakawota nan? Bamuda kudin biyan irin wannan asibitin, Innalillahi wa Innailaihi raji’un Allah karufamini asiri” Baba yana maganan yana kalle kalle he’s just distabilize, ahankali yasa hannu yamai pushing door din, Baba yasake kallonshi yace “nagode kaji” yashiga ciki Khaleel yabishi, sannan yamai pointing dakin da Hawwa take ciki yace “kaduba wanchan dakin” dasauri Baba ya kalli Khaleel saikuma ahankali yace “nagode ko yaro ya sunanka”? Dan kyafkyafta idanu Khaleel tayi sau biyu yakai hannunshi ya shafa kanshi kaman mara gaskiya ahankali yace “Ibrahim Khaleel” ahankali Baba yace “nagode Allah maka albarka Ibrahima bari naje” gyadamai kai Khaleel yayi ahankali Baba yawuce Khaleel yabishi da kallo saikuma yawuce yafita dasauri.

Baba na kaiwa wajen dakin ya hango Hawwa kwance ga bandage a goshinta da hannunta shima ansa bandage ga ciwo a lips dinta sosai an samata drip kala uku all at once bude dakin yayi yashiga yana salati da sallallami yarike hannun Hawwa kawai saiya fashe da kuka yama kasa magana, shigowa dakin akayi wata nurse ce tace “sannu Sir kaine mahaifinta”? Dagowa Baba yayi yana share hawaye yace “eh” tace “Baba muna bukatan information nata dakuma signature” ijiyan zuciya Baba yasauke yana karban takardan gabanshi na faduwa yace “toh Allah karufamana asibiti nawane duka abubuwan nan? Nawa zamu biya?” Dan murmushi nurse din tayi tace “karka damu Baba bawan Allah daya kawota yabiya kudin komi tatas” Dasauri Baba yace “ohh Allah waye shi? Yana ina nagode mai”? Murmushi nurse din tayi tace “ai naganku tare just now kuna magana awajen kofa” baki Baba yarike yace “Ibrahima? Yanzu shine daman amman shine bai sanar dani ba kuma harda nunamin dakin, to Allah yamai albarka, Allah yarabashi da iyayenshi lpy, bari nayimai godiya sainazo na cike” yamika mata paper zai tashi dasauri tace “yatafi ai” yadai ijiye wayanta da jakanta dani, ijiyan zuciya Baba yasauke saikuma ya shiga rubutu, tass Baba yayi komi yabata tafita chan takawomai wayan Hawwa da jakanta Baba ya karba yana tofamata addu’a, Ammi tashiga kiranshi dagawa yayi Ammi na kuka sosai tace “Malam kakai wajen Hawwan yaya take”? kaman ba Baba ba yace “ya isa ya isa dena kuka gatanan dai Alhamdulillah banga likitan tukunna ba amman ance convulsion tayi a mota harta jawo hatsari wani bawan Allah

yakawota asibiti yabita kudin komi” cikeda damuwa Ammi tace “Alhamdulillah Alhamdulilah nima ina hanya” Baba yace “Allah yakawoku lpy” wayanshi Baba yadauka yashiga kiran Ni’ima ya sanar da Ita kawarta tai hatsari amman baya shiga hakan yasa ya nemi number Baban Yaseer yakira ringing daya yadaga anatse yace “Baba barka da warhaka” cikeda damuwa Baba yace “Aliyu Hawwa tayi accident gatanan a asibiti rai a hannun Allah” yanda zuciyan Baban Yaseer yabuga yakusan fitowa yace “wat?! Baba Hawwa tayi hatsari!”?

EPISODE 3️⃣2️⃣

Ni’ima na kwance adakinta dan tun rannan maganan kirki baya shiga tsakaninsu, shima Baban Yaseer ya tattarata ya ijiye a gefe dan baison wahala da hayaniya, idan yashigo dakin yazo daukan kayane, yanda ya tattarata ya watsar abin bakaramin cimata rai yakeba, duktai wani iri kaman ba itaba, batada aiki sai shan kayan matan da Mama ta aiko mata dashi sabida duk randa zasu shirya yadawo yaga chanji, tana kwance awajen taji muryan Baban Yaseer ya ambato sunnan Hawwa, mummunan faduwa gabanta yayi dasauri ta zabura tamike tsaye tasauka daga gadon tai wajen kofa tasa hannu tabude tafito tahaderai tai folding hannu a kirji tana kallonshi, daidai lokacin Baban Yaseer yana sauke wayan daga kunnenshi da bala’in damuwa yakalleta yama manta basa wani maganan kirki fada suke yace “Hawwa had an accident Wife, Innalillahi! Suna asibitin Leadway, je dauko mayafi lets quickly go, ya Allah please keep Hawwa safe for me, please please please, yi sauri wife dauko mayafi” yayi maganan duk yadamu baimasan meyake fita daga bakinshi ba, tunda Ni’ima ta ayrı Baban Yaseer bata tabajin bakin ciki kansa kaman na yanzu ba, yanda yakeyi wlh koda tana labour room zata haihu bataga kalan rudewan nan atattare dashi ba, kirjinta kaman ana sassake kitsen wajen sabida suyan dayake mata na azaba, azuciye tashigo cikin falon yana kallonta danya dauka akwai wani abu dazata dauka awajen, batai wata wata ba tasa hannu tadauki car key shi dake kan table tarike gam a hannunta, Baban Yaseer yakalleta dasauri, Ni’ima tace “we are not going” da mahaukacin damuwa akan muryan Baban Yaseer yace “me kikace?” Kallonshi tayi afadace ta matso dab dashi tana hucin kishin fitina ganin yanda baya hayyacinsa sabida kawarta tace “Hawwa ta mutu ma idan zata mutu is not my business tunda ba yar uwanmu bace ko munhada jini da ita ba, kuma bazaka ba wat is your business with her? Nagadai kawata ce ba taka ba? Kataba ganin ina shigema abokananka maza? Baruwanka da Hawwa” baki Baban Yaseer yabude zaiyi magana Ni’ima taci

numfashinsa tace “Aliyu stay away from my friend! Hawwa kawata ce she has no business with you! Baruwanka da ita! Wayataba cewa dole sai miji yadauki responsibility kawar matansa? Get a hold of yourself kadaina bin kawata kuma ba zakaba!” Tun bayan abinda yafaru ranan yadan bata space cus yasan she’s not okay, amman yaudai no, damuwan daya ciki ma jin Hawwa tayi hatsari bazai taba iya tsayawa gardama da ita ba he just want to see kanshi gaban Hawwa, hannu yamika mata strictly yace “give me my car keys” faduwa gabanta yayi yanda yahade rai yana tabashi key bama ta maganganun datamai yakeba ta masoyiyarshi dake asibiti yake baidama lokacin biyemata suyi fada hakan yakara tunxurata cikeda karfin hali tace “bazan bayarba, nace bazaka je ba, uban me kahada da Hawwa? I’m tired of yanda every little thing you will be running to her rescue, rannan haka kafita tsakar dare without thinking twice Aliyu kabar ni da yaranka biyu cikin gidan nan katafi wajen wata, wat if mu wani abu yasame mu? Wat if barayi sun shigo? I’m your wife you know nikeda hakki akanka ba Hawwa ba, bakada wani business or what so ever da abokiyata, wlh bazan bada key nan ba” cikin kakkausan murya Baban Yaseer yace “this is the last time zan miki magana, hand over my car key! I don’t have time for argument ko bala’i dake, ruhina, zuciyata da kuruwata basa nan suna wajen Hawwa da gangan jikina kawai kike magana, give me the damn car key Ni’ima” yanda kalaman Aliyu ke samata bakinciki kaman ta hadiye zuciya ta mutu awajen, ita Aliyu ke gayama magana haka, jitayi koma mexai faru yafaru kaman zata haukace da bakin ciki tace “wlh saidai kome zakayi kayi bazakaje asibitin nan ba, bazakaje wajen Hawwa ba, ina matarka kana gayamin kuruwanka na wajenta da gangan jikinka nake magana” kawai tafashe da kuka mai ciwo tace “macuci, maciyi amana kawai, mayaudari, kawata zaka so har kana haukacewa akanta haka dame Hawwa tafini? Baban Yaseer kaci amanata wlh kaci amanta, Allah ya kashe Hawwa! Allah ka dauki ranta afito da gawanta daga asibitin na……n” hannu dayaga ya kaimata mari a fuska sai kuma ya tsaya chak hannun na gab da landing a fuskanta tareda sauke hannun kasa yana huci sosai jin addu’an datama Hawwa, hannunshi tabi da kallo daya dunkule da yanda yake huci tace “ni zaka mara sabida Hawwa eh Baban Yaseer? Ni matar ka? Ni Ni’ima zaka kusan daurama mari sabida kawata? Baban Yaseer ni”?.

Bai tankataba cus baiso fushi yadebeshi yayi wani abun dazaiyi nadama nan gaba, baiyi believing in hurting women ba, but harga Allah Ni’ima is pissing him off, baima fahimci this whole anger da fushi da wani tantrums nata ba akan zancen nan shi baice zai auri Hawwa ba out of goodwill bawai dan bazai iyaba no sabida kawai bayason yabata beautiful years of friendship nasu, and again bai sanar da Hawwan ba, Hawwa have no idea yana sonta so what is all this haukan da Ni’ima keyi? Hannunshi yasa yakamo nata azuciye

zai karbi key din Ni’ima tashiga kokawa dashi tana kaimai duka da hannu daya tana haki. “Wlh bazan bayarba saidai ka kasheni ka amsa” murde hannunta Baban Yaseer yayi Ni’ima tai kara tace “Aliyu you’re hurting me sabida Hawwa, wannan rawan jikin da haukacewan sabida best friend dina kakeyi, Aliyu I hate you, how could you? Why will you fall in love with Hawwa? Meta fini dashi? Yarinyar datai kwnatai sabida bakin jini? Yarinyar da Babanta ke rokon mutane suzo su aureta, rawan jikin menene kakeyi dame Hawwa tafini”? Hannunta ya murde da karfi ya karbi key sannan yanunata da hannu amasifance yace “Hawwa tafikida komi! Tafiki hankali! Tafiki natsuwa! Tafiki ilimi! Tafiki kyau da iya murmushi! Tafiki kunya! Tafiki iya girki! Tafiki kwazo! Tafiki kwarjini da haiba! Daga ranan bikinmu rannan dana fara haduwa da Hawwa naji inama ita na aura bakeba! Haryau har gobe I wish inama Hawwa na fara sani not you! I wish itane matana! Hawwa will never act like this! Hawwa carry kanta with dignity! She respects kanta! She knows what she’s doing unlike ke, look at the way kike behaving kaman dakikiya! I explained something for you but brain dinki yakasa comprehending ko ascertaining duka abinda nace, bayan you forced me to speak cus kece kikaje kikamin bincike who sent you to check my phone? Kina bincikamin waya who do you think you’re? Kece ke aure na? Kinama Hawwa wishing mutuwa kawarki that did everything in her power for you! Kin dauka inda inaso na aureta bazan iyabane? Kira daya zanma Baba angama magana, I explained everything for you but still jibi yanda kikeyi? What is all this classless attitude? For wat exactly? I hate razz woman idan kika zama one I will terminate aurenmu cus ban iya ihu ko fada ba, bakina baida kyau, don’t push me, if you push me wlh wlh saina auri Hawwa kuma agidan nan zata zauna! Don’t push me to the wall Ni’imatullah!” Kadakai yayi yawuce yafita abinshi Ni’ima tafashe da kuka sosai awajen kaman ta kashe kanta yau tayi dana sanin sanin Hawwa, ita Baban Yaseer zai kira dakikiya Innalillahi, batun yau yafara son Hawwa ba?.

EPISODE 3️⃣3️⃣

Khaleel na zaune a premises na asibitin kan wani hadadden kujera dake under wani shade na flowers yana jiran suzo su daukeshi dan sunce sun kusa akwai traffic a hanyan school na Noor sabida accident din nan, kuma hakanan baiso yakoma ciki sabida Baba tunda yagane Baban Hawwa ne yakejin nauyinsa hakanan, motan Baban Yaseer daya danno kai cikin hospital din Khaleel yabi da kallo, wanda kallo daya yama motan yagane motan sabida plate number shi kanshi baisan how come ba but yatuna rannan yakalli

plate number motan kuma yazauna akanshi baimasan me dalilin da plate number wani random mutum zai zauna akansa without permission ba, haderai yayi tamau yabi motan da kallo, parking Baban Yaseer yayi nesada inda Khaleel yake zaune yakashe motan yafito yana sanye da riga da wando na shadda mai ruwan goro dayamai kyau, yakafa hula akanshi, haskenshi yafito bau ga bakin glass akan idanunshi, zagawa yayi zuwa bayan motan yabude yafito da manya manyan ledojin for you supermarket yayi shopping yarufe motan yawuce yana tafiya anatse, abu Khaleel yaji ya tsayamai a wuya sai kawai yatashi da hannu yakira security asibitin yazo da gudu yace “Yallabai gani” cikeda isa yanuna Baban Yaseer yace “seize ledojin da mutumin chan yazo dasu” dasauri security yakalli Baban Yaseer saikuma yakalli Khaleel daya haderai sosai yadan rage murya yace “Oga mezan gayamai? I can’t seize abinshi” ihu Khaleel yamai ranshi abace yace “tell him we give our patients food, we don’t accept akawo musu anything daga waje it’s a law daga yanzu go!” Khaleel yafadi aharzuke security yajuya yatafi da sauri shikuma ya tsaya awajen yana kallonsu dudda baiji meyake fadiba but dan bacin rai daya gani akan fuskan Baban Yaseer yamai dadi dan murmushi yayi yana tsaye awajen saiga Baban Yaseer yajuyo, dauke kai Khaleel yayi abinshi haushin sa yakeji kawai yaciro waya ma abinshi, haka Baban Yaseer yabude mota yadawo da komi ya ijiye sannan yawuce Khaleel yajuyo ya watsamai kallo mara kyau daidai motanshi na shigowa wucewa kawai yayi yashiga ya zauna sukabar hospital din sai alokacin hannunshi yafaramai zafi ya kalli hannun, dan tsaki yayi ya yarfe hannun yadan kishingida da kujera bacci yakeji sosai, yau kwata kwata bai sami baccin da ranshi keso ba.

Gida suka wuce ana parking yafito yayi flat dinsu yabude kofa Momy yagani zaune tareda Momy Sam matar kanin Excellency wacce take baturiyan bahaushiya, mahaifiyar ta yar Nigeria ce yar kano bature ta aura ta haifesu saisa duk sukai kaman da baturen but hausa rass abakinsu, suna magana yashigo wajen Mommy yawuce ashagwabe yazauna kusada ita babu batun gaidasu yamika mata hannunshi kaman dan yaro yace “Moma zafi” duk randa shagwaban shi yatashi Moma yake kiran Mommy, dasauri Momy tace “Subhanallahi, Khaleely tayaya kaji ciwo haka? Menene amfanin guards dinka dazasu barka kaji ciwo haka? Why are they getting paid”? Afusace Mommy Sam dan duk jirgi daya ya kwasosu tace “fire them they don’t know their job, Khaleely ne zai kulada da kanshi? They’re very useless, Sorry Son” tai maganan tana kallon Khaleel dake abu kaman yaro yana kallon ciwon dakemai zafi, duk Mommy tarude ta tashi da sauri ta dauko first aid kit tazauna kusadashi spirit tadauka da sauri tana gutsuran auduga tasa aciki takai zatasa a hannun wlh kaman dan yaro, kaman Noor karama ya fizge hannun yace “Momy ni banson spirit zafi yakeyi” kaman Mom zata fashe da kuka dukta susuce tace “yakuri ka daure nasa maka kaji Khaleely, wai yama akayi kaji ciwo eh? All this workers namu

sunsan babu abinda na tsana irin naga mistakenly kaji ciwo? Ya akayi kaji ciwo haka”? Turo baki yayi batare dayayi magana ba, Mom Sam ta taso itama tazo wajen tadafa kadanshi tace “muga hannun” nunamata hannun yayi ahankali cikeda dabara tace “toka daure give your Mom to treat it kaga yanda ta damu” kallon Mom yayi datai kaman zatai kuka kaman wani babban abine ya sameshi tsabagen yanda take sonshi, ahankali yace “small zakisa Mom” dasauri tace “eh naji, kadan zan sama” bata hannun yayi tasa kadan Khaleel yayi ihuu zokaga yanda suke lallashin sa ohh ikon Allah kaman kwai, sannan tashafa healing balm yamike ahankali, Mom tace “zokai breakfast” ahankali yace “I want to sleep I’m sleepy Mom” bangarenshi yayi Mom ta kwalama PA kira, dasauri PA tazo tana sanye da suit baki, Mom tace “cikin 3 girls din nan dasuka rage akaimai daya” Gyadamata kai tayi PA tayi tace “yes Ma” tajuya itakuma Mom suka cigaba da hira, fitowa PA tayi da Zainab dasai murna take cus bata dauka zai kara nemanta nabiyu ba aka kaita side nashi har zuwa sama, knocking PA tayi gaban dakinshi shiru hakan yasa tabude kofa takalli zainab tace “shiga” shiga ciki Zainab tayi itakuma PA tawuce.

Fitowa Khaleel yayi daga wanka daure da towel a waist ruwa na bin chest nashi yakalli Zainab dake tsakiyan dakin tsaye, suna hada ido ta sauke kanta kasa dasauri jikinta har bari yake sabida dadi, awulakance yadauke kai wucewa closet yayi dan yaji sanda ake knocking bai wani jimaba yafito sanye da boxer yana kamshi yagaji bacci kawai yakeso fadawa gado yayi yana sauke ijiyan zuciya yana kallon sama hakanan kawai deep down he’s wishing ta farka yanzu, yadan lumshe idanu gaban boxer dinshi a mike idanunshi a lumshe har lokacin yace “ke come here” dasauri Zainab tai wajen gadon kaman tana magana da sarki tace “g….ga…..gan….gani” dan lallataccen tsaki yayi batare daya bude idanunshi ba yace “ride me” jikinta har rawa yake ta shiga cire kaya tazo tahau kanshi har lokacin idanunshi a lumshe, har cikin ranshi ya furta “don’t die i still have business with you” riding dinshi Zainab keyi amman he’s not even feeling anything kawai yayi shiru kaman matacce kusan 10min kawai ya kifar da ita yafara he don’t even know why yaketa gannin that accident mara kunyan yarinyar nan consistently……

Su Momy na zaune a falo suka fara juyoshi yana ihu, Mom tai murmushi tace “muje falo na kinsan Khaleel baisan menene shiru ba shikuma arayuwansa” tabe baki Mom Sam tayi tace “idan da sabo ai nasaba hakama Sameer duk ubanninsu suka gado ai” dariya sukayi daga Mom har ita tace “yara ace this is just wat is making them happy, zamaninmu is not like that ooo” dariya Mom tayi tace “is from abincin dasuke ci, see en let’s give them happiness” Mom Sam tace “sonake Sam yayi aure kaman Khaleel banson matan banza, shikuma matan banza yafiso” Mommy tace “samowa zakiyi kimai da yaronka yayi iskanci awaje gwara yayi agida, look at abun kaman irin ragon layya ko nama, danka na son wannan tinkiyar I

don’t mind konawa ne wlh zansa kudi na sayo na kawomai yacisu ya koshi koyayar koya zubar idan yagama ci duk ba matsala ta bace haka nake kallon duka matayen Khaleel kaman tumakai danasa kudi na sayo nabashi yayi bukatanshi da su idan baiso ya zubar ko ya yasar Safara” tasauke ijiyan zuciya tace “all this shaye shaye is time zasu dena yarane, last month Khaleel yayi 32yrs birthday nashi fa, he’s still a child, at the age of 24 nafaramai aure cus I caught him watching all this videos na banza, I give d’ana freedom yayi anything dayakeso agaba saisa me and Khaleel share a deep bond sosai I understands him sosai sama da babanshi, idan lokaci yayi zakiga da kansu zasubar shaye shayen kuruciyane wlh, kinga Khaleel babu wani abu nashi daban sani ba, I choose the gurls all of them for him , I’m his everything” gyadama Mom kai tayi tace “wlh zanma Sam auren nan shima” Kusan 1hour suna juyo ihun Khaleel ko ajikinsu chan suka jishi shiru PA tawuce dan dauko yarinyar dan baya kwana da kowa agadonshi, knocking tayi gaban kofan batare data budeba tace “kifito” tashi Zainab tayi daga kasa tana kallon Khaleel dayayi rub da ciki abinshi, kasanta har zafi yake mata ya kumbura sabida yanda shi babu yi ahankali a lamarinshi tawuce tafita. <This message was edited>

EPISODE 3️⃣4️⃣

Shiga cikin hospital din Baban Yaseer yayi anan reception yaga Baba zaune dasauri yayi wajenshi adan rude yace “Baba” dasauri Baba yajuyo jin muryan Baban Yaseer yace “na’am Aliyu harkazo? Ga dakin nan likitoci na ciki cewa sukai na fito, ina Ni’ima”? Boye komi yayi yace “tana asibiti, nariga na gayamata zatazo da zaran tasami chance” Baba yace “Allah sarki Ni’ima nasan tashiga cikin tashin hankali” Baban Yaseer yace “Baba an ina tayi hatsarin”? Tagumi Baba yayi ahankali yace “wlh bansani ba ko inda motanta yake ma bansani ba ta lafiyanta nake yanzu, kwananta biyu batada lafiya tun ranan litinin da yamma, yauma cewa tayı bari taje asibitin su Ni’ima adubata saidai aka kira su Ammi wai me waya tayi hatsari nikuma suka kirani su Ammin suka sanar dani” anatse Baban Yaseer yace “kada kadamu Baba zan kira wani Abokina dake aiki da road safety naji idan zan sami any details na hatsarin da inda motarta yake” Baba yasauke ijiyan zuciya yace “tom shikenan” Baban Yaseer yadaga wayanshi yakira yadan matsa daga inda Baba yake kusan 20min yayi sannan yadawo yace “Baba ance motoci biyar ta deba ta hada da trailer amman Alhamdulillah babu any casualty babu wanda yarasu saidai sunji ciwo, ance wanda yakawota asibiti yasa agent ne ko PA wani dai nasa yasaka yabiya duka masu motocin har trailer kudin gyara motan su da kudin zuwa

asibiti” Baba yakama baki da mamaki yace “iyye awannan zamanin abiya kalan kudin nan? Wannan bawan Allah akwai kyan zuciya da imani dakuma adalci da taimako” Baban Yaseer yace “ba shakka, kowaye gaskiya yayi kokari Allah sakamai da Alhairi”.

Duk suna zauna awajen dan an hanasu shiga dakinta har around 12 na rana saiga Ammi tashigo reception din tareda Ramla dake goye da katuwar jaka abayanta dukansu idanunsu ja, Baba na ganinta yashiga kokarin mikewa hakama Baban Yaseer Ammi ta taho wajen dasauri Baba yayi wajenta hankalin Ammi atashe tace “ina Hawwan Malam? Ina Hawwa na? Ina tak….” Sai kuka kaman ba Baba ba yace “ya isa ya isa, gatachan adaki ance kar adameta kar a shiga saita farka, zauna, Ramla kema zauna” ahankali Baban Yaseer yace “ina yini Ammi” gyadamai kai tayi tana goge fuskanta da bakin hijabi tace “lafiya lau Aliyu sannu, bazakaje aiki ba ka zauna anan” adan hankali yace “bari mugani zuwa ta farka yanzu banda natsuwan yin aiki” ijiyan zuciya Ammi tasauke wlh har ranta batason zamanshi anan, cikeda hikima tace “to dan Allah tayani kai Ramla gida ta ijiye kayanmu tadafo wani abu takawo incase Hawwa ta tashi tanason abinci, Ramla dakin Antyn ku zaki ijiye kayanmu” Dasauri Baba yace “dakin nata abude yake, kaita Aliyu akwai kazanta adaki zaki iya dumama mata shi Ramla” hannunshi Baban Yaseer yasa ya karbi jakan dake hannun Ramla yace “muje” binshi tayi suka fice wajen yarage daga Ammi sai Baba.

Aliyu na ijiye Ramla yajuyo cus bazai iya jiranta tayi wani girki ba ayanda yadamu din nan tsayawa yayi yay salla yafito yana ciro wayanshi daga aljihu inda yaga Ni’ima tamai sama da 20 miss calls thank God wayan na silent maida wayan yayi back yashiga mota yatada.

rannan da zaiga auren Hawwa ba, today started so bad for him, ciwon Hawwa saikuma hatsarinta, saikuma Ni'ima da abubuwan datayi, baitaba tsammanin ending na yau will be this good ba, lallai bahaushe yayi gaskiya dayace idan kasan mafitar rana bakasan mafadan ta ba. Gyaran murya yayi yanuna kirjinshi yace "harga Allah na yarda da Ibrahima! Na aminta da Ibrahima! Nakuma natsu da Ibrahima, danhaka ni mahaifin Hawwa nabawa Ibrahima auren y'ata Hauwa'u dayazo nema ayau!" Malam Sama'ila yace "Allahu Akbar" duk akai Kabbara awajen, Malam Sama'ila yace "idan ba damuwa ga masallacin mu nan, muyi sallan magriba tunda lokaci yayi sai adaura auren" kai tsaye Excellency yace "bismillan mu" duk aka tashi aka wuce out of respect Excellency ya jera da Baba dake dogara sanda suna zance freely kaman sunsan juna babu wani zancen nuna kaskanci, hakanan abin yama Khaleel dadi inda Pops yafi Mom kenan, yanada saurin accepting mutane unless baice yana sonsu ba, hakama yanuna bayason abu to wlh Pops shima zai nuna bayaso kodako menene abin.

Alwala akayi yau masallaci ya cika makil har gaban layi akai salla aka bada Sanarwa za'a daura auren Hawwa, dumbannin jama'an unguwa suka sheda aure tsakanin IBRAHIM KHALEEL DA HAUWA'U AKAN SADAKI MILIYAN HAMSIN DA DARHAMIN GWAL DARI!
Zokaga yanda mutanen anguwa suka haukace news na flying kaman kite Hawwa tayi aure, ashe wani jinkirin alkhairi ne, ta auri dan masu kudi, ai shi Khaleel din shine d'a daya tilo wajen mutumin the richest man a Nigeria menene menene, tashi Excellency yayi ya karbi speaker ya sanar yama masallacin nan donating miliyan dari! Saikuma yabama mutanen ungunwan matar dansa tundaga kan yaro da babba, tsoho da tsohuwa Miliyan dari arabama kowani household, haukacewa Umma tayi acikin gidan dan tanajin announcement daga speaker tace "ina matarsa zai aurar da diyarsa banda darajan dazai fadamin saidai naji a speaker? A inama tasami mijin? Kodai hada baki akayine? Ta ina Hawwa zatasan yaron Alhaji Mangal damuke gani a TV ta ina? Kai karyane da wata akasa auren nan bazai taba lasting ba" kaman mahaukaciya takasa rike bakin cikin tashiga kiran yaranta mata wanda all of them are happy for yayarsu suna cewa zamasu zo gobe kawai ta katse wayan tana zage zage har Ammi dake waya da Ramla dake bata labari saida tajuyo ta Ammi tace "kisa sakata a kofa kada ki bude sai Malam ya shigo" dasauri Ramla tace "ita ta isa ta tabani wlh saina mata tsinannen duka Ammi" Ammi tace "ke!" Dasauri tace "yakuri naji zansa sakatan Ammi".

Adai area nan nasu duk wanda yasan Hawwa yasan Ni'ima duk wanda yasan Ni'ima yasan Hawwa, Mama na zaune a tsakar gida da Ni'ima daketa bambami tunda tazo gidan Mama dazu akai sallama aka shigo gidan matan makotansu ne suka shigo yima

Mama Allah sanya alheri ganin Ni’ima ma azaune a compound din yasa sukace. “Ayiririri ga Babban kawan Amarya, yoo ba dole aganki yau ba ana daura auren kawarki labari yabaza gari anachan ana rabon kudi” daga Mama har Ni’ima confusion look suke musu ita Ni’ima ma bata magana Mama da gabanta yashiga fadi tace “wace kawar Ni’ima kuke magana akai Jamila?” Dasauri Jamilan tace “kaji Maman Ni’ima kuma, tsufa kika farayi ne? Ni’ima nada wata kawa data wuce Hawwa ne? Hawwa yar sanda mana yar wajen Baba gurgu muke magana gashichan an daura aure ana biki a unguwansu sai tafiya ake layin nasu” atare daga Mama har Ni’ima suka kalli juna Ni’ima tabuga wani ihu tana mikewa tana daura hannu aka. “Wayyooo na shiga uku na lalace, na bani, Mama na bani” dan duk atunaninta Baba ya aurama Baban Yaseer Hawwa tunda tamusu rashin mutunci dazu, ahaukace Mama taja hijabi daga igiya tace “sa hijabi Ni’ima muje zama bata ganmu ba, dena ihu kidau makullin mota sabida muyi sauri” su Jamila da mamaki da confusion suke kallonsu Hijabi Ni’ima tasaka ko silipas bata tsaya sawa ba suka wuce su Jamila suka fice daga gidan babu zancen kulle gidan ma ta shiga mota Mama ma na shiga suna tada aiko Samari sai gudu suke kaman ranan idi ana tafita layin koda sukakai tundaga bakin titi an cika tap parking motan tayi agaban wani pharmacy suka fito da karfin yaji da balam bala’i suka shiga kutsawa cikin mutane har zuwa cikin layin daga inda security suke tsaitsaye da bindigogi suma suka tsaya suna kallon Baba tare da wasu manyan mutane suna magana suna gaisawa, sosai Ni’ima ke kallon fuskan kowa one by one bataga wanda tasani ba chan idanunta ya yasauka kan Khaleel da she’s sure shine wanda tagani dazu daidai wasu gayu dake tsaye dasu sunahau gisting.
“Kai Baaba shinefa yaron Senate President shi kadai mutumin ya haifa, just farkon shekaran nan Forbes sukace baban shine number 5 richest man in the whole world, wai bakasan Mangal BeWeeCee ba?” Daga Mama har Ni’ima dakejin hiran faduwa gabansu yashigayi cikin karaman murya Mama na whispering tace “ke Ni’ima ba Baban Yaseer ta aura ba kinaji ana maganan Alai Mangal” daidai lokacin gayun dame bada labari yace “sadakinta Miliyan Hamsim da Darhamin gwal dari fa kai Baba gurgu da yarsa sun gama da talauci har abada, talauci bye bye” sake faduwa sosai gaban Ni’ima yayi, daga motan Baban Yaseer har gidan nasu da dan albashinsa 350k networth dinshi gabaki daya baikai sadakin Hawwa bama Innalillahi wa Innailaihi raji’un.
Gayun sukace. “Mangal din fa yabama masallaci miliyan dari a gyara, sannan yabama anguwan miliyan dari wai arabama kowa babba da yaro, tsoho da tsowuha sabida sun bama dansa yarsu, kai Baaba yauna kara yarda wani jinkirin alhairi ne, yaushe su Gwaggo suka gama Gulmanta agidanmu ranan da safe kan Hawwa ce kadai yarda batai aure a unguwan nan ba Kannin kannenta sunyi aure amman gashi yau dalilinta kalli anguwan mu yatashi da miliyan dubu dari biyu ba in total, Allah kaimana arziki!” Sake faduwa sosai gaban Niiima yayi yana wani jigijim! Jimdum! Dumjum! Dumdum!

Lankwashewa kafafun Ni’ima yayi tai baya zata fadi Mama ta tareta tana salati sun shiga shock, dasauri Mama tace “kinga gobe zanje asibitin nabama su Baba hakuri da Hawwan Ni’ima, kokin hanani billahilazi sainaje, nine mahaifiyar babban aminiyan Amarya ko miliyan goma Alhaji Mangal yabani mena manta tuni zanja jari, jari, gobe da safiyan Allah zani ko asibiti ko nan gıda duk inda suke! Allah yasa banwani mata magana mara dadi ba kuma nasan ba lallai tafadi ma tazo wajena ba, gobe zanje na sasanta komi na shiryaku nasan da gudu zata karbeki da gudu ayanda Hawwa ke miki soyayya, gaba zuciya tuni anyi an wuce, kawancen shekaru ashirin da yan kai, Ni’ima ina chan zan kiraki kizo kibada hakuri! Goben nan zaku shirya!”.

EPISODE 4️⃣0️⃣

Ni’ima nawani irin numfarfashi ta kama Mama tace “Mama ina ganin jira” dasauri Mama tariketa gam ajikinta tace “zomu bar nan wajen” Mama na rike gam da ita suka shiga fita daga wajen batama gani da kyau she’s just feeling suffocated, gaban wani shago suka tsaya Mama ta zaunar da ita da sauri tana jinginata da bango tashiga shagon tasayo ruwa tazo tabata da kyar Ni’ima ta kurba kawai taji ruwan na mata daci abaki tofarwa tayi akasa kaman taci magani takalli Mama tace “Mama jinake kaman an daura dutsen ukudu akan kirjina, Mama ni Hawwa zata maida mahaukaciya? Ni Hawwa zata rainama wayau? A ina tasamo mai kudin nan bata taba bani labarinsa ba? Mama yaushe suka hadu? Yaushe har akazo ana maganan aure har ina ganinshi asibiti dazu danaje? Mama ita harta isa taboyemin abu nata eh”? Taba wani irin huci ta bubbuga kirjinta tace “Mama ni mijin nawa ya sakeni yau ita a aureta yau ni za’a watsama kasa a idanu? Mama tayaya Hawwa zata fini eh? Tayaya zata fini”? cikeda rashin jin dadi itama Mama tace “Allah yasani banso ba, ke kinga yanda nake alfahari da mai kudi kike aure kuwa Ni’ima? Dukfa cikin kannenki kin fisu goshi, kece mai auren mai kudi, kece wacce tai makaranta, mijinki yabaki mota kina gidanki flat mai kyau kina aiki a hospital, Amman yau duk sai naga Aliyu jaririne a inda masu kudi suke, yo ai duka duka arzikin Aliyun ma baikai miliyan hamsin na kudin sadakin Hawwa ba” wani irin shedanin radadin zafi Ni’ima keji aranta har wani sosa gaban riganta take ta saman hijabi, tadauka she will be happy tunda

Hawwa tai aure at least yanzu Aliyu nata ne ita kadai but kuma ganin yanda mijin Hawwan yahadu ga dukiya, ga kyau, ga gata saitaji kaman ciwone gareta ya warke amman wani ciwon yafito dayamafi nada azaba, tana kallon Mama tace “Mama tayaya Hawwa zata fini aduniyan nan eh? Tayaya Mama? Akanme zatayi s’a haka ta auri dan gidan Mangal, Mama kuma bata taba fadamin tamasan yan gidan Mangal ba wlh, ai badaga sama yafado ba sun hadu ne somewhere somehow amman taboyemini dayike makirace ita yar boko datai kwantai, yaushe suka hadu har suka fara soyayya? Mama ni Hawwa zataciwa amana eh? Ni zata ha’inta ta yaudara? Babu wani abu nawa da bana gayamata fa Mama, amman ni taboyemin, ashe saisa tace ko mijina kadai yarage aduniya bazata aureshi ba sabida tasami wanda yafishi akomi, Mama did you realize abinda Hawwa tamin ko? Hawwa play with my intelligence, she belittle me, tabuga wasa dani tanunamin tafini iya mind games” tashiga shesheka tana huci jikinta har kyarma yake, Mama na kallonta itama duniya ta mata zafi tace “munafuka ce, ke bakisan yanzu kasami mai kudi boyewa ake ba’aso asani ba, ai Hawwa bata sonki kwadayin Baban Yaseer yasa ta tsaya arayuwanki” cikin wani irin murya Ni’ima tace “Mama tayaya zan bata auren nasa gidan Mangal da dan su tsaneta eh? Mama tayaya zanyi? Inaso na gayamusu yar iska ce Hawwa maza takebi duk yan sandan office dinsu sun kwanta da ita, Mama help me, yazanyi Hawwa bata chanchanci irin gidan nan ba, tafi dacewa da gidan wahala da gidan kaskanci, Mama bai kamata Hawwa ta auri mijin dayafi nawa karfi ba wlh Yazanyi Mama? Mama banso tasami cigaba arayuwa Mama ni auren ma banso tayi tamutu ahaka, sonake Hawwa ta wulakanta na ganta on her knees tana begging dina for something, Mama ta yaya zan lalata auren nan” kanta Mama tashafa tace “yanzu ai saikin fara koma mata sannan zaki iya bata auren, kibari nafara zuwa na sulhuntaku tukunna, kidena damuwa shikuma Aliyu zan kirashi ya maidaki” Gyadamata kai Ni’ima tayi, Mama tamike tace “muje” tashi tayi sai alokacin tamasan bata saka takalmi ba haka suka wuce ta shiga mota ta tafi.
**

Wuraren 11 sukakai gida, ganinsu sun shigo tareda Excellency yasa Momy tace “ahh tare kuke ne? Son ina kaje yau? Bakai baccin kirki ba Noor nata tambayanka tayi bacci yanzu” goro Excellency yamika mata da yawa da sweets a leda yace “aure mukaje muka dauramai Madam” da sauri Momy takalli Excellency dake zama looking confuse shikuma Khaleel yawuce side nashi abinshi babu abinda ke damunshi banda gajiya, Mom tace “wai wayayi aure Dear?” Khaleel dake wucewa abinshi yanuna mata yace “danki mana he just called me ina chambers yanaso nasameshi an address dazai turamin aure zaiyi shine naje da Mahe dasu Lawali and Co.” Maganan sauka kawai yake akan Mommy kaman saukan aradu tace “akanme zaka biyemai Alhaji? Kasan Khaleel is still a boy baitaba zaban mata da kanshi ba baimasan ya ake aure ba, I always do everything for him

bayan nayi screening yaran, bama wannan ba, waya aura?” Excellency na daukan remote yana chanza channel zuwa news yace “that police officer, Miss Hawwa” dawani irin sauri Momy tace “inashi ina Hawwa? Ina Khaleel ina police woman? Idan tazo tana dukanmini d’a fa?” Dawani irin sauri Excellency yakalli Mommy yace “akanme kike magana haka Madam? Akwai wacce ta isa aduk fadin garin nan ta daki d’ana?” Cikeda damuwa Mommy tace “dole nayi magana haka Khaleel baida irin training da aka mata a police school, ba yarinya bace idan bata girmeshi ba zasuzo age mate I don’t want yarona to suffer” jawota jikinshi Excellency yayi cikeda so ganin hankalinta yatashi yace “ke Madam relax, yaranki just want to have fun ne, please let him have his way, kome yakeso let’s support him, karmu batamai rai, stop thinking of beating or anything, with all the security na gidan nan akwai wacce ta isa ta taba yaronmu? All I see is Khaleel is just a little bit fascinated about the gurl kinsan baitaba ganin Smart, young intelligent bold and fearless Muslim police officer ba” da sauri yace kawo kunnenki da sauri Mommy ta mikamai Excellency yace “yaronki just wants to have fun and play with the girl ne, we have the Momy babu wacce Khaleely na bazai iya samu ba, allow him, kinganshi kuwa yau he looks so happy and excited that happiness was worth everything to me, so don’t ruin that for him and don’t think much, let’s watch him have his way kome yakeso mubarshi yayi” dan ijiyan zuciya Mommy tasauke tace “toh ina matan? Ya baku taho da ita ba”? Ahankali Excellency yace “I don’t know, gobe da safe ma tambayi Khaleel din koma meyakeso it’s okay, lokacin sa ne zamaninsa ne mubar danmu ya huta, yanzu dai aikamai yarinya muje mu kwanta ki matsamin jiki” dan murmushi tayi kadan hankalinta ya kwanta tace “dukku yaranku suka biyo” dariya Excellency yayi yace “kyau kenan d’a ya gado ubansa” ya kashe mata idanu tana kwalama PA kira tasa akaimai yarinya.

Daidai yafito daga wanka aka bude kofa wata tashigo kallonta yayi yadauke kai yazauna kan chair yana zuba wine a cup yabude towel nashi yace “come here” zuwa tayi yace “kneel” kneeling tayi ba musu jiki na bari gani take wannan da aka kawota for the 3rd time she don’t think zai saketa yanzu, yace “suck” gindinshi tashiga sha ya lumshe idanu yana kurban alcoholic wine nashi fuskan Hawwa yake gani datanamai rashin kunya, bude idanunshi yayi kadan yamika hannunshi yadauki wayanshi yabude yashiga gallery hotonsu da akamusu na pool yake kallo yanadan lumshe idanu sabida yanda ake tsotsemai gaba, yadade yana kallonta sannan yayi dan murmushi ya ijiye wayan ya fizge abin nashi yamike kawai yajuyata yashige, shifa he’s doing this sabida kawai yanason sex ne, he loves yayita cin vijay not because he loves any of this creatures da Mom ke kawomai, da ace akwai yanda ake cire vijay a ijiye basai yaga creatures dinba dayafi zaban haka, ihu yafara sosai yana buga yarinyar da kyau datakeji kaman zai xazzago mata da mahaifa yakai kusan 3hrs har kuka take but maka mata yake sannan ya feso yadago kawai ya tureta abuge yace “na sakeki leave my house na

sakeki get outttttttt!” ya hankadeta waje abuge tareda datse kofan yawuce yafada gado sai bacci PA dake waje tabude kofa dan babu wanda baya sanin sanda Khaleel ke sex agidan nan sabida ihu duk wani mai aiki a gida yasani idan yagama zakaji shiru tazo tafice da yarinya.

EPISODE 4️⃣1️⃣

Wuraren 5 Hawwa ke bude idanunta tana kallon saman dakin komi daya faru nadawo mata, hawaye masu dumi ne sakko daga idanunta, ahankali tafara mosti da idanun dake mata nauyi sosai tana juyowa kanta yayi sauki kaman ba nata ba yanzu tana iya juyawa yadena banging, Ammi ta gani a tsakar dakin kan dadduma ga charbi a hannunta tanaja maida idanunta tayi tarufe she can’t look at Ammi, knocking kofan akayi da sauri Ammi ta tashi tace “shigo” tadaga dadduma tana linkewa daidai Dr yashigo tareda Nurses yazo gaban gadon yana kallon Hawwa data lumshe idanu Ammi tace “Dr har yanzu bata tashi ba nadamu abinci fa”? Murmushi yama Ammi yana duba BP Hawwa dayasan ta tashi yace “maganin hawan jini nasa bacci amman karki damu zata tashi saitai wanka” ijiyan zuciya ya sauke yace “Alhamdulillah BP yasoma sauka” anatse yace “Miss Hawwa open your eyes” ahankali Hawwa tashiga bude idanunta tadan kalli Doctor kadan saikuma ta sauke idanun kasa kawai nauyin kowa takeji, Dr yace “ya ciwon kan? Akwai wani abu dayake miki ciwo yanzu?” Girgizamai kai tayi murya kasa kasa dabaya fita da kyau tace “no” Dr yace “okay that’s great” yakalli Ammi yace “Mama help her to change tadan gyara za’azo a gyara gadon akawo mata abinci kuma, an mata booking massage Yallabai yace bayanta na ciwo, masseuse zasu mata massage din, zatasa hospital clothes bama barin patient namu nasa kayan gida” gyadamai kai Ammi tayi tace “to” Nurses suka ciremata drip din suka fice Ammi taje gaban gadon tana kallon Hawwa da idanunta ke kasa ta kauda kanta gefe dasauri jin Ammi tazo wajen, Ammi dake kallonta tace “Jidda na ya jikin? Babu abinda ke miki ciwo kuma”? Gyadama Ammi kai tayi ahankali batare data kalleta ba tace “eh” cikeda so Ammi tace “tashi muje to kiyi wanka ki chanza” Ammi takai hannunta tadagota tasowa tayi da karfin hali ta sauka daga gadon Ammi tariketa har bayi tabata gadon Ammi tahada mata ruwan wanka, tadawo dakin tabude jakan kaya da Baba da Ramla suka kawo musu jiya taciro brush da zani, saikuma pad datasa Ramla tasa ajakan tadauki daya da wando takoma bayin ta ijiye mata tasake fitowa ta yaye zanin gadon daidai nurse tashigo da wani ta shimfida mata da hospital gown mai kyau na yan gayu sannan tafice saikuma masu abinci suka kawo mata

fruits da oat, dasu chips da egg da salad da sausage ga bread saikuma maganin dazata sha a gefe cikin wani glass covered container Ammi sai kallo take komi na masu kudi daban ne. Kusan 15min tayi abayin Ammi takoma wajen bayin tace “kin gama Hawwa”? Ahankali tace “eh” Ammi tabude tashiga tana kallon yanda taki yadda su hada idanu, maidata gadon tayi tana kallon yanda white and blue flowers hospital gown din yamata kyau ta zaunar da ita tana daga tray na abincin tana ijiye mata tace “yi maza ci kafin sudawo” yatsine fuska tayi batada apatite ko kadan kauda kanta tayi asanyaye tace “Ammi bazan iya ci ba” sosai Ammi ke kallonta saikuma ta matso ta zauna abakin gadon anatse tace “Hawwa” asanyaye Hawwa tace “Naam” batare data kalli Ammi ba, lumshe idanu Ammi tayi tabudesu tace “look at me Hawwa” girgizama Ammi kai tayi dasauri lips nata suka shiga rawa tace “Ammi bazan iya ba” wani iri Ammi taji, hannunta tasa tadauke tray na abincin ta ijiye akan table na dakin sannan ta matso dab da Hawwa ahankali tace “Hawwa look at me” daidai lokacin hawaye yasauko daga idanunta tace “Ammi bazan iya kallonki ba, Ammi banmasan ta yaya zan kalli keda Baba ba” sai takai hannayenta biyu tadaura kan fuskanta tafashe da kuka mai tsuma zuciya she’s hurt, Ni’ima hurt her beyond duk yanda zatayi bayanin tace “wlh, wlh, wlh Ammi ni ba yar iska bace bantaba amfani da kaina ba, Ammi that’s not me, bazan tabama wani fyade ba” hawaye Ammi tashare daga fuskanta Hawwa tabata tausayi sannan takai hannunta takama hannun Hawwa tasauke takai hannunta tajuyo da habanta fuskan Hawwa yajuyo Ammi tanuna kanta tace “Hawwa ni mahaifiyarki ce kina gani aduniyan nan akwai wanda yasan yarsa sama da mahaifiyar ta? I know you Hawwa, nasan tarbiyan da muka miki, I know who you are? Dagani har Babanki babu wanda yama dauki maganar da Ni’ima tayi da mahimmanci, Hawwa yau koda haka kike ko kinfi hakama muna sonki and we will always love you, Hawwa ke y’ata ce inasonki aduk yanda kike aduk yanda kika zama, kinji yarinyana, ki manta da duk wani abu data fada, come here” dasauri ta rungume Ammi tana sake samin wani karfin guiwa iyaye daban suke idan suka nuna they’re with you and they stand with you kafi jinka very strong kankame Ammi tayi tana kuka harwani rera kukan take kaman marainiya tace “Ammi menama Ni’ima? Why all this hate? Sabida ni Ni’ima tazageku ta ma Baba rashin kunya, Ni’ima tamin gori tama Baba gori, Ammi me namata eh”? Tawani ja numfashi tana rera kuka tace “bazan taba auren mijinta ba, Ammi sabida bansami miji ba banda aure shikenan na zama dustbin? Kowa yadauko shiritanshi akaina? Ammi inaso nai aure nahuta maybe only then Ni’ima zata yarda dani I’m not after Baban Yaseer, Ammi babu abinda kemin dadi“ cikin dan fushi kadan Ammi tace “zaki kashe kanki akan Ni’ima ne? Hawwa that girl obviously doesn’t deserve you, abu dayane bazanyi supporting naki ba shine kisamakanki damuwan Ni’ima, Hawwa don’t kill yourself akanta, Ni’ima don’t deserve you Allah use this chance ya nunamiki waye ita, so is time kifita daga rayuwansu both ita da

mijinta and move on, toxic people ne dukansu biyun, kiji sauki kidena tunanin komi, I didn't train you to be weak or to be crying for any girl, Hawwa you are a strong girl wacce guguwan iskan mountain baiyi putting baki down ba saida kikai destination naki, shit happens in this life, friends comes and goes, relationship ends that doesn't mean bazamu cigaba da rayuwa ba, close chapter Ni'ima and move on learn from your mistakes, no more room for wacce wishes you death, your secrets should be for your stomach idan ba ni ko mahaifin ki ba babu wanda ya isa yaji sirrin ki, move on and be a better person kinji, kihakura da Ni'ima, tace taja miki layi kema kijamata layin kinjini" gyadama Ammi kai tayi ahankali tana kuka har lokacin, Ammi ta matso ta manna mata kiss a goshi sannan tadauki tray na abinci cikin masifa tace "nayi tir da dabi'un Ni'ima ayahya taje zata gani indai duniya ne fadi gareta, Allah zai saka miki" tashiga bata oats tana sha, masu massage sukazo akama bayanta massage dataji kaman an mikar da ita an ciremata duk wani bending da ciwon jiki, no wonder massage keda tsada ashe haka akeji, duk wani tsamin jiki saida suka fitar bacci yayi awon gaba da ita haka nurse's sukazo suka kara mata fixing drip din tana bacci mai nauyi.

Tun asuba Allah sanya alkhairi akema Baba, kafinma yasamu yabar masallacin was around 8:20 sai farin ciki yake nanma wasu suka sake tsareshi anan waje anamai Allah sanya alheri wani kara son Baba ma akayi a unguwan Baba tsabagen murmushi kumatunsa har ciwo yake sai wajajen 9 yawuce gidansa da sallama ya shiga cikin gidan Maman Ni'ima daya gani a tsakar gidan kan kujera yasa yaci tura ya tsaya, Mama ta washe baki tace "ahhh Malam ka shigo barkanmu da safiya ai tundazu nazo nake jiranka" dan jim Baba yayi saikuma yakaraso ciki yace "Malama Maimuna ya kwana biyu ya yara ince dai kinaji daga garesu"? Murmushi Mama tayi tace "kowa na nan lpy, satin daya gabata ma Usaina ta haihu an samu Abdulwahabu" anatse Baba yace "Masha Allah, Allah ya raya" ya kwalama Ramla kira data fito daga dakin Hawwa tace "gani Baba" Mama yanuna mata yace "kaita ciki bari na zaga nazo" Mama ta mike tabi Ramla ciki tanabin dakin Hawwa dakenan tsaftsaf da kallo shikuma Baba yawuce makewaya.
Fitowa yayi ko kallon Umma dake kitchen baiyiba itama haka yawuce dakin Hawwa inda Mama take, kujera yaja yazauna yakalli Ramla yace "jeki hadamana kari Ramla" gyadamai kai tayi shikuma yakalli Mama kai tsaye yace "ya akayi Maimuna wannan dakike nemana"murmushi sosai tayi tace "na farko dai Malam naji labarin dakebin gari sai shigowa makota suke sunamin Allah sanya alheri diyata Hawwa an daura aurefa shine nake kiran Ni'ima dan abankinta yakamata naji wannan labari amman saiba abakinta nakeji ba, nan fa Ni'ima tafara koro zance aiko saida namata tatas dan har mari na yanka mata, akan namiji zatai kalan haukan nan shine fa na zuro hijabi da sassafen nan nazo nabaka hakurin abinda

Ni’ima tayi kuyafe mata Baba bakaga yanda ta damuba dan Allah ayakuri kaga tsakanin harshe da hakori ma ana samun sabani balle kawaye” Baba yace “wannan haka yake” Mama tace “Baba toh dan Allah kuyakuri mune iyayensu karmu zuba musu ido su lalata mana zumunta mu daidaitasu Baba, Ni’ima tayi nadama kwarai kawai shakkan ku take dakuma tana tsoro kar Hawwa taki yafemata amman dazaran kasa baki kowa yasan Hawwa zata hakura Malam”Mama tai shiru tana jiran amsan Baba, dan murmushi Baba yayi yace “Masha Allah naji duk bayanin dakikayi Maimuna” yasakeyin shiru yace “dan yafiya wlh na yafema Ni’ima, ni uba ne akan mene zan riketa azuciya bayan nima yarana zasu iya kuskure da shirme kaman nata, idan zancen yafiya ne nayafema Ni’ima har ranan gobe kiyama” dasauri Mama tace “Alhamdulillah,Alhamdulilah Alhamdulillah, shikenan yaranmu sun shirya” ta washe baki, Baba yayi shiru saikuma yakalli Mama yace “Maimuna dubeni nan, ni ubane kaman yanda kike mahaifiya, hakkine akanmu idan mukaga abinda zai cutar da yaranmu mu kauda abubuwan daga hanya” Baba yayi shiru yana lumshe idanu yana tuna yanda Ni’ima take ikirarin kashe Hawwa yace “idan Hawwa zata yafema Ni’ima bazan taba hanata ba amman idan Hawwa zata dawo da Ni’ima rayuwanta saina hanata!”Faduwa gaban Mama yayi dasauri takalli Baba bakinta tafara rawa, Baba yadan kada kafa yace “wato Maimuna jiya na karanci abubuwa da dama akan idanun Ni’ima, tundaga kissan data dinga ikirari zatama Hawwa, da fatan mutuwa data dinga mata, da yanda dudda mijin natane mai laifi ina shiyabi Hawwa? Shi yake sonta Hawwa bata sonshi amman batai kan mijinta ba kan Hawwa tayi, ga diyata agadon asibiti rai hannun Allah Ni’ima bataji tausayin ta ba karasata takeso tayi” yayi jimm yace “Maimuna ansan mata da kishi amman naga ko kishiyan ka ce take gadon asibiti zakadan tausaya karage wani abun” Dasauri Mama tace “Malam kishi kala kala ne, akwai masu zafin kishi kafahimta” adan zafafe Baba yace “Maimuna fahimtan danayi yasa nike miki bayanin nan, koda yaran nan sun shirya madaman Aliyu na kaunar Hawwa Ni’ima bazata taba kaunar Hawwa ba duk karyace! Ni’ima tariga ta tsani Hawwa! Naga kiyayya a idanunta kibar maganan nan kawai!”.

EPISODE 4️⃣2️⃣

Rasa tacewa Mama tayi amman taki giving up ina sai inda karfinta yakare kawancen nan saisun dawo dashi, ijiyan zuciya Mama ta sauke tace “Malam duk naji bayaninka kuma banki ba hujjujinka masu karfi ne, konine naga wacce ke shirin cutar da yarana zan dakatar, amman kuma ka kalli abin ta wannan fuskan mana, ina

duk ba Aliyu ne sanadi, dalili, da haddasanan fadan ba? Malam ai komi yakare yanzu, Hawwa tayi aure, babu sauran fada kuma” Baba yayi murmushi irin na manya yace “ke mace ce Maimuna bazaki taba gane yanda zuciyan maza yakeba, idan namiji ya daurama kansa soyayyan wata har abada soyayyan nan baya fita daga ransa, daukeni a misali har gobe ina matukar kaunar marigayiya mahaifiyar Hawwa, shi son gaskiya baya mutuwa, inhar Ni’ima natare da Hawwa dole zata dinga ganin dabi’u wajen mijin nata dazai dinga konamata rai daganan kishi ya motsa afara tunanin illata wani ko kisan kai, maganin kar ayi karma afara naga Ni’ima, Ni’ima taganni, ayayyafe amman adawo tare ban aminta ba, kawai ahakura Aliyu yariga yabata komi, Hawwa takamu da hawan jini hakkinane na kareta gwara ta nisanci mutanen da zasu bata matsala arayuwanta wato Ni’ima da Aliyu dan haka kiyakuri kawai Maimuna, ahakura da kawancen tunda yazo irin gabar nan, zanje nayi kari daganan naje asibiti” yayi maganan yana mikewa bayason zancen bakaramin daurewa yayi yamata maganan hankaliba amman ya tsani Ni’ima da dabi’un datayi, yarinyar ta basa tsoro baitaba sanın haka Ni’ima take ba, tashi Mama tayi dasauri tace “dan Allah Malam ayakuri, Malam kabar yaran nan sudawo tare sunason junansu Malam” dakin Umma Baba yafada Umma ta watsama Mama harara dan basa shiri sabida uwar kawar Hawwa ce rai ba dadi Mama tawuce tabar gidan.

Kari Baba yayi tareda Ramla sannan ta shirya suka fito tare wajajen 11 daidai motar Baban Yaseer na parking Baba ya tsaya turus yace “je gida Ramla natashi tafiya saina kiraki” komawa ciki tayi, Baban Yaseer yafito yazo wajen Baba cikeda mutunci suka gaisa Baba ya zauna kan kujera shikuma ya zauna a tabarma yadan sosa kai yace “Baba zan fara da baka hakuri bisa ga abinda yafaru jiya, Baba kayakuri yawancin maganganun da Ni’ima tayi na tabbatar cewa karya tama Hawwa, kowa yasan hakan ba halin Hawwa bane, Baba dan Allah kayakuri” murmushi Baba yayi yace “bakomi nahakura komi yawuce” ijiyan zuciya yasauke yace “saikuma ahhhhhmmm” yadanyi shiru yana sosa kai Baba yace “ina jinka” kanshi ya sauke kasa yace “Baba inaso kabani daman auren Hawwa! Baba ina matukar son Hawwa, namaka alkawari Baba zan kula da ita nakuma riketa amana Baba, Baba dan Allah dabi’un Niima kada su sa ka ki bani wlh Baba zan kula da Hawwa namaka alkawari babu abinda Ni’ima zata iya mata”
Ijiyan zuciya Babayasauke anatse yace “Aliyu” dagokai Aliyu yayi yakalli Baba yace “Na’am Baba” Baba yayi murmushi yace “Aliyu kai d’a nagari ne da babu iyayen dabazasuyi alfaharin samunka amatsayin d’a ba, Kanada hankali natsuwa da kirki babu wanda bazaiso yahada zumunci dakaiba” yayi shiru chan yace “Allah yana jarabtanmu da abubuwa da dama, wani zubin yana nunamana duk yanda mukakai ga son abu bamu samuba sabida banamu bane” faduwa kawai gaban Aliyu keyi Baba yace “ina sonka Aliyu sosai amman y’ata Hawwa bataka bace, jiya nadaurama Hawwa aure da

Ibrahima, Hawwa tariga tazama matar wani!” Faduwa gaban Aliyu yayi dasauri yakalli Bab idanunshi har twitching suke sabida bugawan kirji yama kasa magana Baba ya lumshe idanu yabude, Baba yace “kayakuri Hawwa tayi aure, inaso kaima kaje ka gyara rayuwanku da Ni’ima, ku daidaita kanku, ku shirya ku kula da yaranku, yanzu Hawwa tafita daga tsakiya, babu wani abu dazai kara jawo muku fada, inaso naga ka koma yanda kake d’a da Ni’ima gwanin ban sha’awa, ku manta da komi acigaba da rayuwa anama juna fatan alkhairi kaji Aliyu”baki Aliyu yabude zaiyi magana saiga hawaye mai zafi sun sauko daga idanunshi dasauri yakai hannu ya share yajuyar da kai yana huci zuciyanshi na kuna yanason Hawwa sama da tunanin kanshi, waye Ibrahima? Yaushe Hawwa ta sansa? Ko sanarwan da Baba yayi sanarwa a masallaci ne yasa aka samo Ibrahima? Zafi yaji ranshi namai hawaye suka kara zubowa ya share da sauri still yakasa magana, ba karamin tausayi yabama Baba ba, kana gani kasan Aliyu na son Hawwa sosai, ahankali yace “kayakuri Aliyu, nasan yanda so yake, baya neman shawara idan zai kamaka, amman kayakuri, ka rungumi kaddara, ka gyara aurenku da Ni’ima ka rungumi iyalinka kaji” gyadama Baba kai yayi yakasa motsi Baba yayi shiru yana kallonshi yakai kusan 20min ahaka sannan yatashi muryanahi narawa sosai kaman zai fashe da kuka yace “natafi Baba” Baba ya gyadamai kai duk jikinshi yayi sanyi but this is the right thing, yawuce yatafi Baba shima yayi shiru, saida yaga barinshi unguwan ya kwalama Ramla kira suka tafi abinsu.

Da kyar cikin ikon Allah Baban Yaseer yakai gida gateman dinsu na gaidashi ko iya amsawa baiyiba yawuce yabude flat nasu yashiga yashiga bedroom nasu yazauna yafara fuzar da iska da baki sosai, hawaye masu dumi suka shiga zubomai yasan da Ni’ima duk batai haukan nan ba wlh Baba zai iya bashi Hawwa, yanzu ga shi Baba yaki, yasan rigiman Ni’ima yasa Baba yaji gwara ya aurar da Hawwa ga kowama ko wutan da Ni’ima ta kunna tamutu, iska yakara fuzarwa hawaye masu zafi suka zubomai baitaba sani rana zaizo dazaiji yanajin tsanan Ni’ima ba sai yau jiyayi ya tsaneta completely, bazaima so yaganta ba ko ya kalleta sai iya shaketa, yana ahaka wayanshi yahau ringing share fuskanshi yayi ya daga wayan Ni’ima yagani na kiranshi harta katse wayan bai daukaba tanamai kira na biyar ya daga yakai kunne baiyi magana ba, murya chan kasa tace “Baban Yaseer dama nakira nacemaka kayakuri ne da duk abubuwan dana maka natuba dan Allah let’s forget the past and move on for the sake of yaranmu” Wani kaluluwan abu Baban Yaseer yaji yana tasomai yana zuwa wuya Ni’ima tace “Babyna kaji nasan bazaka iya fushi dani for long ba please kayakuri” kasa rike abun dake wuyan nashi yayi cikin tsantsan tsana yace “bazan taba dawo dake ba, and for yarana ko da ke ko bake zasu rayu, na tsaneki Ni’ima na tsaneki da ko muryanki banso na sake ji, I hate you with everything in me, na tsaneki” yazare wayan ya katse ya jefar yazauna akasa yana dafe kanshi yashiga kurma ihu sosai kaman mahaukaci he’s so heartbroken, gateman yazo yana buga

kofansu yana “Alhaji lafiya, Alhaji Alhaji”.

EPISODE 4️⃣3️⃣

Ammi na zaune wuraren 11 tana duba wani littafin azkar while Hawwa na bacci sosai mai nauyin gaske taji kamshi ya daki hancinta mai dadi har saida tadago kanta ta kallo kofa Khaleel ta hango jikin kofan dago kan datayi yasa ya matsa da sauri gefe, shiru Ammi tayi saikuma ta kalli Hawwa dake bacci mai nauyi massage din yamata dadi ga drip ana samata ta lullube mata tundaga ciki har kafafu da bargo daga cikinta zuwa kai abude kanta babu dankwali tayi kyau sosai, she’s sure shine yaron jiya shine mijin Hawwa kunya yakeji ne kome? Lallai yaron kam akwai kunya yana abu saikace barawo, Ammi tayi murmushi tana tashi ta taho wajen kofan tabude tafito, Khaleel na tsaye jikin kofan yana sanye da riga da wando masu kyau milk adan hankali yace “good good morning Mom” saikuma yajuya zai tafi dasauri batare daya jira amsan Ammi ba, ahankali Ammi tace “Ibrahim” chak ya tsaya yadan juyo kanshi akasa, dan murmushi kadan tayi tace “bazaka duba matar taka ba? Dan zauna da ita nima kafafuna sunyi tsami bari nadanyi tafiya cikin asibitin kadan” kafin yayi magana ta wuce yabi Ammi da kallo saida yaga tafice sannan yajuyo ya kalli dakin kafin ahankali yabude kofan ya shiga maida kofan yayi yarufe ya tsaya jikin kofan yana kallon Hawwa dake bacci mai nauyi hakanan kawai yaji kirjinshi na bugawa sosai dum dum dum! Gently yadaga kafanshi yataka zuwa gaban gadon ya tsaya tareda folding hannu a kirji yana kallonta, she looks very sick and beautiful a hospital gown din, har lokacin akwai bandage a goshinta but an cire na hannuwanta ga ciwuka a hannu, ahankali yadaga hannunshi yakai gently yadaura kan left hand dinta wani kalan shock yaji baisan sanda yarike hannun gam ba tareda sauke ijiyan zuciya sannan ahankali yakai yatsanshi yana shafa ciwon hannun wanda yasan Ni’ima ne tamata cus yana mota data tattake mata hannu haka murya chan kasa yace “why will you love a girl this much?” Yabi hannun da kallo that felts super soft kaman hannun little Noor ga nails nata so long and white and clean looks so sexy, mirginowa Hawwa tayi kanta zai fadi daga filo dasauri yakai hannunshi yatare fuskanta yafado cikin palm dinshi tana sauke ijiyan zuciya daya huro a hand nashi cikin muryan bacci tace “Ammiiii” wani irin lankwasa kai Khaleel yayi yana kallon fuskanta dake cikin hannunshi
Her face is so damn soft, baitabajin wani excitement dan mace ta shiga jikinshi ba but right now he’s feeling so good, tsareta da idanu yayi yana kallonta ya duko a tsaye fuskanta na cikin

hannunshi, kaman mai whispering yace “Hawwah!” Kar Hawwa tabude idanunta saida gabanshi yayi wani mummunan faduwa yanda take kallonshi da very very bright eyes saikuma tamaida idanun tashiga kullewa suna juyawa, muryan Baba yaji awaje dawani kalan sauri yazare hannunshi fuskan Hawwa ya kife anan kasan filo daidai Baba na bugo sallama yana shigowa tareda Ammi da Ramla dakuma wasu mata guda uku, biyu daga cikinsu goye da yara abaya daya babu yaro abayanta somehow somehow they look like Baba, Ammi ta wuce tana gyara fuskanta, Baba yace “Ibrahima kana nan? Ka kannin matarka Hawwa ku gaisa Khadija” Babban wacce ita kebin Aminu Khadija tace “ina yini Yaya Ibrahim” akunyace Khaleel ya gyadamata kai, Hafsa tace “ina yini Ya Ibrahim yamai jiki” Maryam tace “ina yini ya Ibrahim” Ramla itama tace “Ya Ibrahim ya jikin Ya Hawwa” kaman bai iya magana baisaba da mutane haka ba ana kiranshi Yaya Yaya yace “da…da sauki” yakalli Baba akunyace yace “Baba zan tafi zan dawo anjima” Baba yace “muje na takamaka” shida Baba suka wuce suka fita suna fita Khadija da Hafsat da Maryam da Ramla suka shiga tafi saikuma sukahau rawa, Hafsa tace “wlh mijin Ya Hawwa yahadu Wayyoo Allah na I’m so happy for Yaya Hawwa” Ammi tace “kunga karku tadamin yarinya da surutu” duk dariya sukayi sukahau hira.

Around 4 DIG yazo hospital din tareda Abraham da Hayatu Baba yamusu iso suka gaisa sosai, suka ijiye kudi da basket na so many goodies sannan sukama Baba sallama suka tafi.

Shima Aminu around 4 yashigo asibitin Baba yadingamai fada akanme zaibar school yazo….

Wuraren 7 Khaleel yashigo asibitin Salman na binshi da shopping na kayan kwadayi daban daban yarike hannun Noor data isheshi da maganan Hawwa ga teddy a hannunta looking so pretty sukai ciki, tundaga glass na kofan ya hango Hawwa zaune kan gado an ijiyemata table da abinci daban daban kekai Ammi na kaimata abinci abaki tana kaudakai tana yatsine fuska idanunta sun kumbura na kuka da bacci, ga Baba shima tsaye kansu suna fama dataci abinci murya chan kasa Khaleel yace “she’s such a child” dasauri Noor tace “Daddy mekace?” Kallon Noor yayi baiyi magana ba tace “Daddy let’s go inside I want to see FAA” dan ijiyan zuciya ya sauke yasa hannu yayi knocking tareda bude kofan Noor tasaki hannunshi tai ciki da gudu tace “My Fairy Angel Anty” Hawwa tadan bude idanu tana kallonta kawai Noor tahau gadon ta gefen Ammi ta tattaka tafada jikin Hawwa ta rungumeta tsamtsam da karfi Hawwa itama ta rungumeta yarinyar is freaking cute and adorable.
Baba yace “Ibrahima shigo ga wuri” yabashi plastic chair shi Baba yakoma kan dogon kujera ya sauna su Salman suna shigo suna ijiye jakunkuna suka fice ahankali Khaleel yace “ina yini Mom” murmushi Ammi tamai tace lafiya lau Ibrahim, aran Hawwa tace

“Ammi na ne Mom” da sick eyes tadan kalleshi tana rungume da Noor tana mamakin meya kawo dan iskan yaron nan asibitin nan taki gaidashi, tasowa daga jikinta Noor tayi tace “FAA ya jiki? That day of accident my Dady was taking me to school I saw wat you were doing” Noor tashiga gwadama Hawwa, tace “I told my Dady, Dady yafita yadinga bin car naki da gudu he removed you from the car you were biting my Dady hand” tanuna hannun Khaleel dake zaune da sauri yajuyar da hannunshi Baba yace “aiko naga ciwon dama Hawwa ce ta jimaka?” Kin magana Khaleel yayi, Noor tace “we brought you here FAA are you fine now? U will not fall sick again ko?” Gyadamata kai Hawwa tayi ahankali tace “yes” dasauri Noor ta rungumeta tace “I love you FAA” tashi Baba yayi cikeda hikima yace “bari na karbi sako wajen mai keke” Dasauri Ammi ta tashi tace “muje na bika nafadamai abinda zai fadama Ramla” kawai suka fice.

Itama Noor dasauri tasaki Hawwa ta sauko daga gadon tai wajen Khaleel dake kallonta tace “Dady I forgot my second teddy in car I brought it for FAA” ahankali yace “meet Salman to take you” dasauri tai wajen kofa tajuyo takalli Hawwa dake binta da kallo tace “FAA I’m coming” Gyadamata kai Hawwa tayi tawuce tafita dakin yarage daga Hawwa sai shi, kafa daya yadaga yadaura kan daya yayi shiru yana kallonta, yanda Hawwa taji ajikinta ana kallonta yasa tadan juyo ta kalleshi hada ido sukayi zata ballamai harara komi daya mata nadawo mata arai, da yanda yayi attempting tabata but yanda taji shiya ceceta, plus dazu Baba nata cewa Ibrahima yakawota asibiti yabiya kudin komi da motocin data bata yasa softly da dan kyar tace “thanks” tadanyi shiru ta dai daure tasaki muryanta tace “thank you for saving my life” tasakeyin shiru ahankali tace “once nakoma aiki i will find a way to pay you back every penny daka kashe” tasakeyin shiru chan tace “all this daka kawo kasa atafi dasu banso, i hate favors barinma na mutane like you! So I will pay back everything” Murmushi kadan yayi batare dayayi magana ba wato tana sick bed still masifa take, Noor tadawo dakin ta tafi wajenta da sauri tabata teddy tace “FAA take, Dady said you will soon move to our house kikazo i will give you more and more teddy kinji” dan murmushi kadan Hawwa tamata tace “thank you beautiful Noor” tana mamaki uban me zai sake kaita gidansu dayake gayama yarsa zata” kusan 10mins yayi sannan yakalli Noor daketa zuba yace “let’s go” kiss ta manna ma Hawea tace “bye FAA” murmushi sosai Hawwa tayi tace “bye Noori” wucewa tayi wajen Khaleel yarike mata hannu sukai wajen kofa hakanan Hawwa samin kanta da kallonshi tayi, the way he walks, he way he held Noor’s hand, everything looks soo….ta tsaida tunanin, saida yakai daidai kofa ya tsaya Noor ta fita dan juyo da kanshi yayi karaf suka hada ido dasauri Hawwa ta dauke kanta, cikin dan iskan murya Khaleel yace “see you soon cry cry Kulu” dawani irin sauri Hawwa tajuyo ta kalleshi kaman zakanya, gira daya yadaga mata yace “see you very very soon Kululu” kawai yasa

kai yafice daga dakin Hawwa tawani yunkuro tace “sunana Hawwa not Kulu or kulul whatever” Khaleel na jinta yayi murmushi yawuce abinsa.

EPISODE 4️⃣4️⃣

Yau Hawwa ta tashi da karfinta sosai tun asuba Dr yazo yace “za’a sallameta yau but sai Ogansu Mai asibitin yazo” aka ciremata bandage na goshi da hannuwa ciwukan sun warke tanada jiki mai kyau sosai, wanka tayi tasa wani simple gown da aka kawo mata na atampa red dayamata kyau sosai, ta rame idanunta kana gani zai nuna maka tayi ciwo but takara kyau skin nata sai glowing yake na drip datasha, tun wajajen 7 Aminu yazo dan daga masallaci yazo basai Baba yazo ba daya shigo dakin Ammi bata ciki taje karbo magunguna daga pharmacy sai Hawwa dake zaune ta kishingida hannunta rikeda wayanta tana dannawa tana replying messages na DIG dasu Hayatu, ganinshi yasa ta dago kanta dasauri yayi wajen gadon yana murmushi yace “ya karfin jiki Ya Hawwa?” Murmushi kadan tamai tace “Alhamdulillah I’m fine yaushe zaka koma school why did you even come back”? Zama yayi gefenta yace “yayata that is the strongest person I know a duniyan nan tana rashin lafiya why won’t I come?” Shiru Hawwa tayi tana kallonshi tadan harareshi kadan tace “mutum sai dadin baki” dan dariya yayi yace “Ya Hawwa nasha fruits dinnan”? Gyadamai kai tayi yadauka da sauri yana sha Ammi tashigo tace “Aminu jinya kazo ko cin dadi jiyafa haka komi kuka raba naka yamafi na su Khadija” murmushi yayi yace “Ammi to nine babba” hararanshi Ammi tayi ta ijiye magungunan tace “maza gamaci mu hada komi Dr na zuwa za’a sallamemu wai” tai maganan tana mikawa Hawwa red veil nata Hawwa tasa hannu ta karba tayafa saman kanta daba dankwali, duk suna zaune har wajajen 9 wayan Hawwa dake hannun Aminu yana connecting hotspot nata danashi yahau ringing dasauri yabata wayan yace “Abraham office” hannu tasa ta karba tana kwanciya ta danna wayan tana sawa a speaker daidai lokacin ana knocking tareda turo kofan Abraham yace “Hello Miss Hawwa how are you feeling” magana kasa fita yayi daga bakin Hawwa sabida Khaleel data gani ya shigo yana sanye da labcoat ajikinshi an rubuta Dr Khaleel Mangal, ga stethoscope a wuyanshi hannunshi rike da file na Hawwa dakuma office pad da pen idanunshi kyar akanta ga Dr daya saba duba Hawwan tareda shi sai Nurses guda uku daidai Abraham yasake cewa “Hello Hawwa are you there?” Firgigit Hawwa tadan farga daga kallon Khaleel, adan rude tace “uhn” Aminu yasauka dagakan gadon cikeda murmushi yace “sannunku ina kwnan ku” gyadamai kai Khaleel yayi kanshi akasa yace “good

morning Mom” kafin ta amsa yayi wajen gadon daidai lokacin Abraham yace “huhh wat a relief! I’m so glad you’re okay I’ve been so worri……” wayan Khaleel yasa hannu ya dauka tareda katsewa Aminu yadaura hannu a bakinshi yana makale dariya Ammi tadanyi murmushi kadan tace “muje waje Aminu” suka wuce suka fita, wani kalan kallo Hawwa tama Khaleel irin who gave you the authority to end my call amman mutanen data gani wajen yasa tadaure tadauke kai batai magana ba, professionally Khaleel yace “can I have your hand Mrs Lee?” Wani kallo Hawwa tamai shekeke irin is something wrong with this guys head, dayan Dr yace “Dr Khaleel she’s the patient I consulted you for kace nakara mata dosage na wannan medication din nan and BP ya sauka sosai” “hand” Khaleel yafadi fuska ahade har wani daci daci Hawwa keji abakinta yanda zata bama dan iskan nan hannu da kyar kaman ta kurma ihu ta bashi hannun tadauke kai tana kallon gefe, daura mata abun auna BP Khaleel yashiga yi sannan ya makala stethoscope a kunne da gangan yawani zauna abakin gadon yana facing nata arude tajuyo zatai magana yace “shiii idan ana auna BP ba’a magana” hadiye maganan Hawwa tayi wannan wani irin mutum ne, pulse nata da heartbeat ya saurara sannan ya zare stethoscope din yakalli Dr yace “she’s good” yakalli Hawwa yace “any complain Mrs Lee”? Dauke Kai tayi tareda girgiza mai kai bataso ta disgashi gaban abokan aikinshi ganin he’s not jobless ashema yayi school, gyadakai Khaleel yayi yace “in that case I can discharge you” yashiga rubuce rubuce a iPad din da pen sannan yabama Dr yace “zaku iya tafiya” wucewa sukayi suka fice saida Hawwa taji an rufe kofan sannan tajuyo hada idanu sukayi yana mata dan iskan kallo azuciye tace “katashi daga kusadani” cikeda kakkausan murya yace “anki” iyyee wow just wow irin kallon da Hawwa kemai kenan ganin karfin halinshi, rage murya sosai yayi yace “idan kika kara kuka kika sa kanki damuwa BP ki yatashi sabida that mad, crazy, babaric woman of yours mai kama da gumakan Egypt mesuem I will reap your heart off your chest kimutu gabaki daya nayi donating all organs naki to mabukata, starting from heart, liver, kidneys with this eyes etc” wani irin kallo Hawwa kemai baki bude ikon Allah, tadaure tarufe bakin tace “you’re nobody in my life dazakamin detecting what I should do and what I shouldn’t, you’re nobody to me Pops boy!” the way she talks shit! he can’t even explain but he enjoys it, dan matso da fuskanshi dab da nata yayi dasauri takoma baya gabanta na faduwa sanin su Ammi na waje tace “me..me….mehaka?” Ahankali Khaleel yace “I want to actually shows you who I’m in your life” dasauri yakawo fuskanshi kaman zai mata kiss Hawwa batasan sanda ta mika duka hannayenta biyu ta daura a kirjinshi ba hakan yasa ya tsaya chak kirjinshi ya buga dum! Hawwa tace “is this abinda ku kema patient naku a hospital dinnan? I will sue you Allah” dan murmushi yayi cikeda tsokana yace “koni i will sue you for touching my chest, index finger naki on my breast kina tabawa!” Abala’in haukacewan sauri Hawwa ta janye hannunta dagakan kirjinshi jikinta yahau rawa tama kasa

magana, she just hates dan iskan yaron nan, did he say breast uban wani breast zata taba ajikinshi? Murya chan chan kasa Khaleel yace “do you have crush on me? Cus you were trying to take advantage of your handsome Dr duk kin gama mammatse mini this” yataba nonuwansa yana mata very cute smile da white hakoranshi ke showing yamata wani irin kyau a idanu.

EPISODE 4️⃣5️⃣

Bugawa kirjin Hawwa yayi sabida yanda murmushi taga yamai kyau da sauri ta dauke kanta tayi folding hannuwanta a kirji tace “ewww Allah ya kyauta you don’t even belongs to league na men da Hawwa fancy, babu abinda zanyi da womanizer, drunkard and a playboy like you!” Shiru Khaleel yayi yana kallonta kaman mai nazarin wani abu saikuma yatashi daga bakin gadon jakan daya gani a tsakar dakin yadauka yace “we will see about that if this womanizer, drunkard and what’s even the last one dakika fadi Kulu”? Aharzuke Hawwa tace “nace maka ba sunana Kulu ba” dan murmushi kadan yayi baice komiba yawuce kofa, Hawwa data kara kulewa sabida yanda taga ya maidata mahaukaciya tace “ina zaka da jakana? Zaka kara da sata akan qualities din naka ne”? Tsayawa yayi saikuma ya juyo ya kalleta yabude baki zaiyi wata magana kawai saiya daga mata gira daya yamata dan iskan murmushi yabude kofa yafito dasauri Aminu yazo zai karbi jakan yace “kawo Ya Ibrahim nadauka”girgizamai kai Khaleel yayi yace “no dauko sauran saika sameni a mota awaje” yawuce Ammi tabishi da kallo kawai taji yafara kwanta mata arai itama ta tashi tashiga dakin Aminu ya kwaso sauran kayan yafito, Ammi takalli Hawwa data kirne fuska tace “lafiya naga ranki abace” dasauri ta gyara fuskanta tace “bakomi Ammi” hannu Ammi tamika mata tace “tashi mutafi gida to” ahankali ta sauko daga gadon Ammi narike da hannunta suka fito Khaleel na tsaye tareda Aminu yagansu sun fito duk yanda yaso yadena kallon Hawwa data haderai tadauke kai yakasa daga Ammi har Aminu saida sukaga kalan kallon da yakema Hawwa kaman zai hadiyeta da idanu, har wajen motan sukazo Hawwa tace “ina keken Aminu”? Dan sosakai Aminu yayi zaiyi magana Khaleel yace “I’m taking you home dakaina” yasa hannu yabude musu bayan mota yace “Mom shiga” ahankali Ammi ta shiga shikuma Aminu ya zagaye shiga gaba abinshi Hawwa ta kalli Khaleel da idanunta dahar sunyi ja, Ammi ta leko ta window ganin yanda take hararan Khaleel tace “shigo mana Hawwa” danne komi tayi sabida Ammi ta shiga taki rufo kofan yadanyi murmushi yasa hannu yarufe yashiga gaba ya kunna motan he can’t even remembers d last time dayayi driving haka yaja motan su Salman na binsu abaya cikin wata

Lexus.

Gyadamata kai tayi, Hawwa tace “gobe zanje office I will see what I can do about license naki Ogana has good connection he can help, I know what nursing means to you bazan bari kiyi loosing nashi ba okay” Gyadamata kai Ni’ima tayi, murya chan kasa Ni’ima tace “zaki tayani kiran Baban Yaseer kibashi hakuri ya maidani gidana? Banda ko sisi banda aiki yanzu I need him please kitayani kiransa” abu Hawwa taji ya tsaya mata a wuya takasa motsi takasa cemata eh ko a’a, Ni’ima tace “please feel free ni da ke are one kinji Best” hannunta Hawwa ta kalla saikuma tadauki paper bag din tana dubaw,a Ni’ima na kallon jakan Hawwa tashiga ciro abubuwan ciki tana neman wayanta, wasu expensive designers perfumes ne sai box na polo diamond watch da another box na LV brackets sai kuma cute note, ganin bataga wayanta ba yasa tace “Innalillahi na manta ban karbi wayana daga hannunsa ba” abu Ni’ima ta danne dataji ya tsayamata a kirji tace “wane?” Yatsine fuska Hawwa tayi kadan tace “Khaleel” murmushin dole Ni’ima tayi tace “ohh wai mijinki, shiya baki gifts haka”? Gyadamata kai Hawwa tayi not paying attention to her sabida yanda taji ranta yabaci yagama tabata yatafi da wayanta, hannu Ni’ima tasa tadauki note din ita adole sun dawo kaman da tace “read note daya miki mana bari na karanta miki” tai murmushi tace “yarubuta my first gift with love to Mrs Lee Kulu Yar Sanda” dan tsaki Hawwa taja tace “dan rainin wayau” Ni’ima tace “he’s so romantic gurl common ina kukaje”? “Hawwa!” Ammi ta kwalamata kira dayasa Ni’ima ta tashi dasauri tace “bari natafi har yanzu Ammi fushi take dani gobe zanzo maybe by then yakawo miki wayan sai mu kirashi”gyadamata kai Hawwa tayi ahankali tace “take care” Ni’ima tace “I love you Best” baki Hawwa tabude zatace love you too kaman yanda sukeyi da saita kasa furtawa murmushi tamata ahankali mai taushi tace “thank you agaida Mama” juyawa Ni’ima tayi tayi zaure tana tafiya ahankali hoping Hawwa zata kirata ko agogon nan ne tabata amman taji shiru tace shikenan Hawwa ta chanza ba haka Hawwa takeba da ba, ko waya Hawa tasaya zata iya sadaukar mata amman yau ko kudin ma datace batada su Hawwa bata bataba, ga gifts tagani but Hawwa couldn’t give her a thing.

Komi Hawwa ta kwasa ta shiga daki da sallama Ammi ta kalli Ramla tace “fita zanyi magana da Yayarki” fita Ramla tayi ganin yanda ran Ammi yabaci tana fita Hawwa tayi wajen Ammi dasauri tace “Ammi dan Allah kiyakuri yazanyi I have to talk to her amman naji maganan ki bazan maida ita kawata kaman d’a ba!” Kabar da hannunta Ammi tayi daga jikinta cikin tsananin fushi tace “you are very very very stupid Hawwa!”Dasauri Hawwa ta kalli Ammi dan

bata taba zaginta ba, rai abace Ammi tanuna kanta tace “is something wrong with your brain? I expected you kice kinji kin yafe let’s end things kaman yanda ita tai initiating at first ki sallameta but kin tsaya kina hugging Ni’ima are you mad?” Baki Hawwa tabude tace “Ammi wlh bah……” “yimin shiru!” Ammi tafadi tana mata ihu, Hawwa tayi shiru tasauke kanta kasa Ammi tace “imagine kun fita keda mijinki yabaki gifts wannan kawar kike nunamawa har tana tayaki karanta note din da mijinki yarubata miki, you are telling her zaki ma Oganki magana kan licence dinta, zaki tayata kiran Baban Yaseer what is your business with Ni’ima and her affairs sai Ni’ima ta kasheki zakisan ta tsaneki ba kawar arziki bace?”
Ammi tai ihu she don’t care at this point uban kowa yaji Baba yashigo dakin yace “da kyau Zainabu wanke miki ita tunda kunnen kashi gareta” Ammi tace “Uwarki ce Ni’ima ko ubanki da bazaki iya hakura da ita ba can’t you leave with out her? Wlh kika kira Baban Yaseer kokikai magana kan licence dinta sainayi mummunan saba miki, Hawwa kika kara jawo Ni’ima jikinki wlh saina zame hannuna a lamarunku tunda ke kinsaka differentiating good people from bad, you’re a criminologist but kin kasa karantan Ni’ima kisan criminal ce ita all she’s doing dake is friends with benefit bata taba sonki ba, yau tazo wajenki sabida tasan u might be able to get her licence back for her, tasan mijinta na sonki kina karansa kika cemai yadawo da Ita zai dawo da ita, this gurl has been benefiting from you right from day one, Ni’ima tafi kowa cin albashinki saitaci tarage sauran mu yan uwanki kike rabamana” Ammi bambami takema Hawwa bana wasaba, tace “yanda kike kashema yaranta kudi kanninki da yaran kanninki basu samu haka daga jikinki suci, duka abinda kika mata arayuwa bai hana rana daya ta kwance miki zani a kasuwa ba ta zagi ubanki ta zagi uwarki ta goranta miki yanzu shine still kike neman goyata abaya kiyi Allah baki sa’a nina tafi zaria nafasa kwana gidan nan, Ramla zoki hada kayanmu mutafi”

Dasauri Hawwa tarike kafanta tana girgiza kai tace “Ammi dan Allah kiyakuri” Baba shima yace “Zainab yakuri yamma tayi bani barinki kishiga hanya yanzu” kaman Ammi zatai kuka tace “Malam Hawwa na batamin rai, tana bakantamin rai, haba haba dan Allah gamai sonta ta tsaya tana gayamana mashayi ne menene menene, ga mara sonta takasa ganewa binta take ido rufe kaman makauniya,ana nuna mata gaskiya tana kulle idanu ina dalili kasheni takeso tayi da bacin rai da takaici nagayamaka bazan kwana ba Malam” Baba shima cikin masifa yace “shikenan kin batama mahaifiyar ki wacce ita kadaice bata fushi dake aduniya rai, matarnan ni da ita bama hammata iska muke akanki sabida yanda bataso ina fada akanki ina damunki, jibi yanda kika bakanta mata rai yau Hawwa kinji dadi ko”? Tashi Hawwa tayi sai kawai ta rungume Ammi tafashe da kuka tace “Ammi dan Allah kiyakuri trust me I don’t consider Ni’ima my friend anymore and namiki

alkawari bazan kara bari tasan sirri na ba kawai tabani tausayi ne somehow I feel responsible for her situation and condition da Baban Yaseer baiyi all abubuwan nan ba da yanzu suna tare abinsu but bazan karaba kiyakuri Ammi na forgive me dan Allah" shiru Ammi tayi saikuma ahankali tace "naji nahakura ya isa, kawai abin namin zafi arai ne yanda kike yunkurin dawo da makashinki rayuwanka" Baba yace "Allah ya kyauta ai ta kuskura tai haka saitaga bacin raina" ahankali Hawwa tace "bazanyiba Baba" wucewa Baba yayi yafita Hawwa takai Ammi gado ta zauna sai kawai ta kara rungume Ammi, ahankali Ammi tanuna mata wasu shopping bags tace "kinga abinda Ramla tayi taga opportunity" dan murmushi tayi kadan tace "yarinya ce Ammi" ahankali Ammi tace "ina kukaje?" "Wani shagon dinki aka aunani hmm" ta tabe baki Ammi tai murmushi tace "muga abubuwan".

EPISODE 5️⃣1️⃣

She wants to be Hawwarh's best friend, wannan abubuwan da ada zatai sharing da Ni'ima gwara tayi da ita, tabata labaran hakan zaisa ta manta da Ni'ima, Ammi ta karba tana budewa tarike baki tace "au dan gidansu yartawa yake cewa Yar Sanda Kulu lallai Ibrahim yacika sarkin tsokana" Ammi tabude kwalin agogon taciro tana kama hannun Hawwa ta dauramata tace "masha Allah cip cip idan gobe yazo saikisa yaganki dashi yaji dadi haka akeyi ma miji" Hawwa tadan turo baki tana tauna baki batadai magana ba gudun karta batawa Ammi rai Ammi tasamata bracelet din shima yamata kyau sannan ta bude turarukan ta feffesa mata itama Ammi ta fesa anata jikin tace "uhm ni Maman Amarya nima nayi kamshi" dan murmushi kadan tayi Ammi tace "kai gaskiya mijinki ya san kan turare Hawwa kinji kamshi" dasauri tace "Ammi nabaki ki daukesu ni dama inada turare na" dakuwa Ammi tamata tace "kwal ubaki Hawwa mijin naki yamiki kyauta zakimin, kaji yarinya inga kin bama wani saikin sani" turo baki tayi ta tashi kawai tana rage kayan jikinta Aminu yayi sallama yashigo wani waya daban yakawoma Hawwa yace "Ya Ibrahim yace nakawo miki" wayan takalla Iphone ne bamatasan wanne ba ganin Ammi na kallonta ta wutsiyan ido yasa tasa hannu ta karba tace "to" ta ijiye tawuce bayi.

Around 10 duk sun kwanta ita Hawwa sabida zatai azumi gobe Ammi kuma sabida zatai tafiya gobe, sabon wayan dataki bi takanshi tuntuni ne yahau ringing ita batamasan sim dinta ne ciki ko wani dabanba hakanan dai taji bazata dauka ba, wayan na karewa yashiga ringing again Ammi tace "wai ba ke ake kira ba Hawwa nafasan ba bacci kikeba" tashi tayi ta sauka daga gadon

tasa hannu tadauki wayan akan mirror tadawo gadon ta kwanta sannan ta danna wayan takai kunnenta sabida Ammi yasa ta kwantar da murya sosai hakan yasa muryanta yayi wani irin dadi ahankali tace “hello” lumshe idanu Khaleel yayi yana gyara kwanci afalo ashagwabe yace “I’m hungry Kulu” wani iri Hawwa taji yanda yayi magana hakan yasa tayi shiru, Khaleel ahankali tace “I don’t feel like eating abinda chef namu suka dafa, nazo kimin girki Kulu?” Runtse idanu Hawwa tayi tace “nace banson sunan nan” ahankali yace “but Hawwah is Hawwa Kulu” Shiru Hawwa tayi the way yake kiran Hawwa dadi, sabida Ammi tadaure tace “bacci zanyi zan tashi nayi azumi anjima good night” zata cire wayan daga kunnenta yace “but it’s not Ramadan, azumin me kikeyi ramuwa?” Shiru tayi ta lumshe idanu kaman bazata amsashi ba tace “nafila ina azumi Monday and Thursdays” cikin yar karaman murya yace “nima zanyi” yayi shiru jin batace komiba Khaleel yace “sainai addu’a Allah karya baki ikon bata auren mu, I want to live my life with you” yafadi ahankali baimasan mesa yake fadin hakaba but kawai yanaji ajikinshi bazai iya rabuwa da ita ba dan juyawa Hawwa tayi ganin Ammi tayi bacci ga ijiyan zuciyanta tanaji hakama Ramla yasa ahankali tace “you’re a liar! Kaida ke wulakanta mata bakasan darajansu ba, imagine locking your Baby Mama in jail, Allah bantabaji I hate someone kaman the way na tsaneka ba” shiru Khaleel yayi sai kuma chan yace “do you love my gift?” Cikeda tsana tace “I will never love anything that comes from you” shiru yayi baice komiba Hawwa kawai tazare wayan daga kunnenta daidai yasake kira kaman bazata daukaba tadauka kafin yayi magana tace “how could you send that video to Nursing Council don’t even deny it nasan aikinka ne, why would you do that to my friend?” Hamma taji yayi yace “zan fita I know you don’t have friends so bansan wat you are saying ba bye” Hawwa tace “aikin kenan party giya da mata” murmushi yayi yace “gashi na aureki” zatai magana ya katse wayan jitayi ranta yana kuna yana susa tasan yanzu club zaije maybe Allah kadai yasan time dazai dawo shiru tayi sai chan ta tuna yanda yamata kiss a kumatu a mota dasuri takai hannu tashiga share kumatunta kaman yasamata dafi ahaka tai bacci.

Washegari around 8 suka fito dudda tanajin bakin cikin shiga motan nan haka ta shiga Ammi tafara kaiwa park sannan tawuce office.

Tundaga gate ake mata yajiki ana mata Allah kyauta tana zuwa direct office na DIG tayi tai knocking yabata izinin shigowa yana ganinta yadakatar da rubutun dayake yace “Hawwa are you sure you’re strong enough kidawo aiki?” Murmushi tamai tace “yes Sir thank you” anatse yace “welcome back” gyadamai kai tayi ganin ta tsaya bata wuce ba yasa yace “akwai wani abu ne?”

Gyadamai kai Hawwa tayi cikeda damuwa, seat dake gabanshi ya nuna mata hakan yasa ta zauna akan kujeran ya ijiye pen na hannunshi yace “I’m listening Miss Hawwa” gyadamai kai tayi anatse tace “Sir I have a very serious problem I need your help” gyara zama DIG yayi dan yana bama Hawwa respect da girma dan ijiyan zuciya ta sauke tace “Sir I’ve never been to Senate President house banda time din nan damukaje aiki, I know nothing about them or household nasu” with so much anticipation DIG yace “what’s with Excellency Hawwa?” Ijiyan zuciya ta sauke cikin raunin murya sosai tace “Sir ranan danai accident ina hospital Babana yabasu aurena, sai bayan mun dawo gida anyi discharging dina ake sanardani wai wannan yaron nasa Khaleel aka auramin” tayi maganan hawaye mai zafi na sauko mata DIG kanshi was in shock yazaro idanu yana kallon Hawwa yace “you mean Khaleel Baban Noor”? Gyadama DIG kai tayi bakinta na rawa tace “I have no idea me suka gayama Babana, banso Khaleel yake yakarani acikin sahun matansa sabida yayi using dina and dump me bayan 1 or two weeks” Ko kadan DIGGG baiji dadin news dinba but still cikeda damuwa yace “Hawwa akanme mahaifinki zai bada auren ki batare dayayi bincike ba? I’m not saying that because maybe zasu miki mugunta or something no su basa wannan, kawai dansu baisan menene aure ba, baisan darajan auren ba, mata are like papers zai iya bude this page ya yaga and open another page, so why will your father get your married to such kind of man”? Bayan hannu Hawwa tasa tagoge idanunta tace “sabida he’s tired of me, yagaji da yanda nake zaman mai agida ba miji” DIG ko kadan baiji dadi ba yasakeyin shiru sai chan yace “to wani help kike magana zan miki”? Share fuskanta tayi tass kaman batai kuka ba takalleshi tace “I want you to come with me Sir muje ka gayama Babana the type of Man Khaleel is cus wai on 23RD this month za’ayi biki zan tare, I don’t want this marriage I don’t want to be victim of circumstance na gayama Babana all I know yaki yarda I’m sure ka tayani gayamai zai yarda”.

EPISODE 5️⃣2️⃣

Kallonta DIG ya tsaya yana yi kaman mai lissafi na kusan 2min sai chan ya sauke ijiyan zuciya yace “Hawwa listen ki fahimceni keba yarinya bace I will be very raw in whatever I will tell you now” yadan sauke ijiyan zuciya yace “I’m a father inada yara mata babu wanda ya isa yazo yace zai aure yarana nabashi batare danayi bincike ba, for mutanen nan suzo mahaifinki yadauke ki sharp sharp batare daya damu dako kinaso ko bakiso, ko kinsan guy din ko baki sansa ba yabada ke only mean one thing” yadanyi shiru

yana kallon Hawwa yace “just like rest of the victims parents kema maybe mahaifinki just did it for money ne so kina gani koda zanzo nace gashi gashi mahaifinki zai yarda akashe auren?” Hawwa tai shiru yace “saikuma second abu, Hawwa you’ve been in this job kinsan yanda aikin gwamnati yake, Baban yaron nan sune Nigeria gabaki daya do you want me to be on the bad side of such kind of people?? Naje nace kaza kaza ko baban ki baice ni ba ne las las zasu gano nine kinsan abubuwan da hakan can cost me?” Yasake shiru yace “banda haka this is personal matter not work related, maganan aure ake ni as Oganki ko Boss dinki baikamata na shiga ba sai inzo naji kunya nan gaba cus of What If dayawa dana hararo in the case, what if ke bai sakeki like the rest of the matan ba? What if ya zauna dake har abada? Hawwa you have power what if you somehow influence him ya gyara all those hali and changed? Idan ya chanza is a good thing since he’s not a murderer ko wani kidnapper” Ahankali DIG yace “just think it through but I don’t think is proper for me to interfere Hawwa, kiyakuri but I don’t think hurumina ne tunda har Babanki ne yabada ke da kanshi just pray and seek Allah guidance Allah sadaki da alkhairinsa” hawaye Hawwa taji ya zubomata sharrrr tai shiru a office din anatse DIG yace “so sorry Hawwa” tadade ahaka sannan ta share fuskanta tamike tace “is it okay nai resuming gobe Sir I have to be somewhere”? Gyadamata kai yayi yace “sure take your time” wucewa tayi tafita yabita da kallo tawuce tashiga motanta ta tada Maman Noor kawai tafado mata arai, she’s her only second hope. Sanin tana prison hakan yasa tawuce prison na mata, parking tayi tana zuwa ta nuna ID card nata tawuce office na prison warden din ta zauna bayan sun gaisa da Matar Mrs Adebayo tace “wakikeson gani yau Miss Hawwa”? Anatse Hawwa tace “Hadiza Muntari wacce was convicted sabida kidnapping yarta datayi that senate president case ish” dasauri Mrs Adebayo tace “ohh Hady we call her Hady anan, ai jiya an fitar da ita, wasu yan sanda sukazo da clearance from court they withdrew the case against her wlh she’s so lucky” sosai Hawwa ke kallon Mrs Adebayo Khaleel ne ya yafemata sabida jiya ta gayamai she will find evidence against him? Mrs Adebayo tace “why are you looking for her”? Murmushi kadan Hawwa tayi mai ciwo tace “kinsan nine nai investigating case din but well that aside nace ko kunada home address nata yar wani gari ce kinsani”? Girgiza mata kai tayi tace “no gaskiya yar Bidda ce but bamu da address nata” Shiru Hawwa tayi saikuma chan tamike tabata hannu suka gaisa tace “thank you very much” tawuce tafita.

Tunda tafito tana tafiya zuwa parking space ta hango Khaleel tsaye jikin motarta tsaye yana sanye da dogon wando da shirt dabai saka boturan sama ba, faduwa gabanta yayi akwai tracker a motarshi ne datake ja yanzu? How did he know tana nan? Daurewa tayi ta karasa ko kallo bai isheta ba tazo zata wuceshi tabude motan ya fizgota tadawo baya kaman paper azuciye Hawwa ta buge

hannunshi tace “don’t touch me again! Stop touching me!” dan zaro manyan fararen idanunsa Khaleel yayi yace “someone is in a bad mood today wow!” Yadanyi dariya yana kallon yanda tahade fuska tana kallonshi yace “smile it’s Sunna!” Hararanshi tayi jin abinda yace tace “so kasan sunna” tashiga fizge hannunta yaki saki sai kawai yabude bayan motanta dan tariga tai unlocking car din da key hannunta tun dazu datazo wajen, yaturata cikin motan yashigo shima da sauri ta matsa baya tamai ihu. “Wai mehaka? Leave me alone!” Dan cute smile yamata yace “sabida kinga matar nan an saketa is that why you’re in this bad mood?” Ja idanun Hawwa sukayi takalleshi azuciye tace “even if it means me bringing down the whole world searching duk lungu da sako I will do it! I will get Evidence and I will show Baba and my entire family the kind of person you’re! Khaleel just know this and keep it at the back of your mind bazan taba zaman aure dakai ba, you’re a worthless boy da baisan darajan mata ba! You don’t value mata! You treat us like trash! And I refuse to be one of your victim”Khaleel na kallonta yadan rage murya yace “konama wasu kenamawa? Why do you hate me?” Ihu Hawwa tamai tanaji kaman ta shakesa tace “I hate you sabida you’re a piece of thrash! I hate you sabida you’re a f*ck boy! I hate you sabida you’re a playboy! I hate you sabida you think life is just about women, money and parties! Kace nikamawa dazan tsaneka?” Tadanyi shiru kadan takalleshi da masifa eyes nata tace “kasan abinda ake cema ciwon y’a mace na y’a mace ce? I hate you sabida abinda kama all those women daka wulakantar” dan tabe baki yayi yace “I don’t want them why should I keep them?” Hawwa afusace tace “you don’t want them why did you marry them and ruined their life eh Pop boy”?.

EPISODE 5️⃣3️⃣

Dan shiru Khaleel yayi yana kallonta ganin yanda zuciyanta ke tafarfasa, she’s really angry today, and as far as he’s concern he didn’t ruin any girls life rather he makes their life even better and colorful, all of them and family nasu are living large yanzu, lumshe idanu yayi yabudesu kadan ya kalleta murya chan kasa yace “I can’t stay 2days without having s*x!” Wani irin yammm kunnen Hawwa yayi jin abinda yafadi tadan dauke kai daga kallonshi da sauri, murya chan kasa yace “I started getting married at 24yrs, call me anything ni ba mazinaci bane Mommy na auramin su ne nayi s*x” runtse idanu Hawwa tayi da kyar tabudesu zuciyanta na radadi yanda yake magana akan mata tace “sannu Moms boy! Mata sun dawo maka toys for your selfish satisfaction eh dan gata”? Kallonta Khaleel yayi asanyaye Hawwa taji kaman zata kama da

wuta ganin yanda hankalinshi kwance tace “okay nima so kake na shiga cikinsu tell me I will be your 10th wife ko 20th?” Anatse kai tsaye kuma yace “14th wife actually!” Wani zuciyane ya debi Hawwa batasan sanda tayo kanshi takama gaban riganshi ba fearlessly ta jijjigashi ranta na kuna tace “how dare you marry me Khaleel? Sabida kaga nakai 29yrs banyi aure ba is that why you took advantage of desperate state na Baba na and use the perfect timing ka aure ne eh talk?” Tayi maganan Hawaye na cika idanunta sosai tana kallon fuskanshi ta rike gaban shirt nasa gam gam, Khaleel yayi shiru yaki magana ganin ranta abace yake yau sosai cikeda bakin ciki ganin yaki magana Hawwa tace “how dare you take away the only evidence danake sa ran zan samu na nunama Baba wayekai eh? Khaleel I don’t deserve you, after good 29yrs banyi aure ba clocking 30 I’ve been so patient cus nasan Allah will reward me for imanin danayi, why will I end up with the worst person dana sani aduniya you!? I’m too good to be your wife, you are a bad bad badddd person Khaleel I hate that kai Baba ya auramin!” Tai maganan hawaye na saukowa daga idanunta tana kallon cikin kwayan idanunsa kaman yanda yake kallonta shima, all this while batai kuka ba sabida tanasa ran she will have something to show Baba but yau da Khaleel yayi outsmarting nata sai taji duniya yamata zafi, duka takaimai a robust chest dinshi hawaye na dauka daga idanunta tace “I hate that kai Baba ya auramin! I hate you Khaleel I hate hate hate you na tsaneka! Na tsaneka” tafashe da kuka tana kaimai duka sosai akirjinshi duk yana kallonta asanyaye, cikin kuka tace “I remembered the day daka fadamin one day sainai kuka ina begging naka for mercy agaban that super market” cikin kuka har shesheka take hawaye har gemunta tace “you won! You won! You won Khaleel, I’m sorry for everything Ibrahim! I’m sorry for being rude, for insulting you calling you jobless, I’m sorry for everything dan Allah kasakeni! Please divorce me dan Allah” tashiga kuka sosai bana wasaba, bata taba sanin zata iyama Khaleel kuka hakaba, ahankali Khaleel ya lumshe idanunshi da hannu daya ya fizgota yasata ajikinshi “leave me leave me” Hawwa tai ihu amman saida yasata ya kankameta sosai tun tana hargowa hartai shiru ajikinshi tana kuka ahankali.

Lumshe idanu Khaleel yayi yana shakan cool kamshin datakeyi dayamai dadi sosai tana kuka yakai bakinshi saitin kunnenta yana matseta ajikinshi ta yanda bazata iya fitaba murya chan kasa yace “I’m glad kinyi admitting defeat Kulu Khaleel never loose a fight! Mace bazata taba winning dina ba!” Zatai motsi yariketa gam ahankali yace “I will never divorce you Kulu! This Khaleel you hate so much saikinyi rayuwa dashi har abada!” Yadanyi dariya kadan mai sound yace “maybe da baki tsaneni ba danai letting naki go” awani irin hankali yace “and I will sex you just like yanda nakeyi da all the rest of those girl creatures, I will add you to the collection of women I slept with!” Yanda Hawwa ke fizge fizge kaman zata tashi

amman yahanata fita daga jikinshi, yakara kai bakinshi wajen kunnenta yace “kinata neman evidence akaina bayan nine keda evidence akanki” yayi wani makirin murmushi yace “imagine Baba yaga video or pictures of when you were trying to rape me kina shamin baki, grabbing my shirt just like yanda kikayi dazun nan, trying to reap off my shirt and strip me naked, how will Baba feel?” Fizgo kanta Hawwa tayi daga jikinshi ta sauka gefe takalleshi da jajayen idanunshi tace “wat are you talking about? Ko zanyi raping maza aduniya trust me i will never go for national cake irinka da karabama all matan garin nan jikinka!” Shiru Khaleel yayi yana kallonta babu macen data taba gwada kalan zagin da Hawwa kemai, she just called him national cake, dan ijiyan zuciya ya sauke, wayanta dake inda take zaune yanuna mata yace “check your phone?” Dasauri Hawwa ta dauki wayan tabude, tana dubawa taga yatura mata hoto ta iMessage guda daya inda take saman kanshi bakinta akan nashi tarikemai gaban riga duka jikinsu ajike hannunta yahau rawa takalli Khaleel da sauri cus she’s confuse, kanshi yadan sosa irin na iskancin nan yace “I have the video inhar u finally took off the shirt kina shamin this” yanuna mata nipples dinshi cikeda iskanci, yadan kalli saman motan kaman mai tunani yadaura yatsa abaki saikuma yacire yakalleta yace “I will just start crying to Baba ince yarshi beat me up ta turani cikin ruwa tafito dani kawai tahau kissing baki na and kikayi threatening dina kan cewa dole saina aureki, nazo nagayama Baba, Baba will easily believe me daman that crazy woman tace zaki iyama maza fyade so I’m your first victim” yakashe mata ido daya a iskance Hawwa na kallonshi hawaye na cika idanunta, Comfortably Khaleel yace “idan bakija bakin nan that talks like parrots kinyi shiru anyi bikinmu an kawomin ke gidana ba I will expose this” yanuna mata wayanta yace “family naki will lose all respect for you and zama dani dole, anyhow u look at it I’m still the winner, ko kinaso ko bakiso saikin zauna dani, don’t forget you started this war with me Kulu!” Glass nashi ya warware ya sanya a idanu sannan ya kalleta yace “see you Kululuwa Yar Sanda bye” yabude kofa yafice abinshi yawuce nashi motar aka budemai brabus dinshi yazauna aka ja motan harsaida Hawwa ta daina ganinshi tafashe da kuka sosai tana kallon hoton tana mamaki what happens to her? How come is this picture photo shop ko sun bata wani abu ranan ne tunda yan kwaya ne how did she kiss this man cus batasan sanda akaiba, takai 20min tana kuka amota sannan ta tada motan tabar wajen.
**''''H

Ijiyan zuciya Momy tasauke cikeda damuwa tana kallon Salman daya gama koramata bayani acikin office dinta hannu tasa ta zare glasses dake kan idanunta tashafa goshinta cikeda damuwa tace “why that police girl in all matan dake duniyan nan dan Allah? Ko yar india Khaleely yake bukata zan iya auromai why that girl? Akanme yake chasing nata up and down tell me the truth Salman sonta yakeyine?” Cikeda girmamawa yace “I can’t say Hajiya

gaskiya, but one thing is bantaba ganin Yallabai na bin mutum up and down kaman yanda yakebin yarinyar ba shi kanshi ba lallai yasani ba but he’s giving her all of his attention his time and komi Ma’am” table Mom tabuga tace “that’s wat I don’t want, yarinyar will take my son for granted wlh, zata wahalar min dashi Khaleely baitaba bibiyan any girl aduniyan nan ba saidai su suyita bibiyansa what is so special about tsohuwan yarinyar nan da he’s all over her eh? Hmm, u can go Salman just keep me posted whenever he sees her and wat they discuss about” gyadamata kai yayi yace yes Ma yawuce yafita.
Tashi tayi ta tsaya jikin window ta hango Khaleel din na buga ball da Noor he looks so happy haka Noor ma Mom ta sauke ijiyan zuciya, bude kofan office din nata Mom tayi tashiga another elevator dake wajen tasauka kasa tana tafiya zuwa garden da Khaleel ke buga kwallo Noor dake sanye da jersey na Liverpool looking so cute tace “Granny join us” murmushi Mommy tamata tace “continue playing Princess dina” takalli Khaleel dake wasa da kwallo abinsa kaman bai ganta ba tace “why do you keep chasing that Police girl Khaleely?” Batare daya dagokai ya kalli Mom ba yana bugama Noor kwallo yace “what is your business with my affairs Momy”? Dan shiru Mom tayi taji zafin amsan daya bata inda sabo sun saba haka yake musu magana agantale, ahankali tace “common My Leely I didn’t train you to be going after kowace kalan mace aduniya! You have everything na rayuwa babu wacce kakeso dabazaka iya samuba” daidai lokacin yabuga kwallo araga shida Noor sukahau suna jumping suna ihu yadagata yana ihu suna dariya sannan yasauke ta yace “go to your Nanny tamiki wanka” dasauri Noor tawuce tana gudu shikuma yadauki kwallon cikeda iskanci ya wurgama Mom tai baya baya kaman zata fadi sannan tarike ball din da kyar tana haki tace “Khaleely banson iskanci fa, karyewa kakeso nayi?” Khaleel ya kwashe da dariya sannan yataho inda take yabata sidehug yana daura hannunshi akafadanta cikin sangarci yace “Mom tsoro kike zan aur'o miki yar sanda?” Hade fuska tayi hakan yasa ya kwashe da dariya again Mom ta tsaya tana kallonshi he’s so happy this days, Khaleel yace “Mom do you think she will stop me from living my life? And enjoying myself?” Cikeda damuwa Mom tace “eh mana Khaleely girls like her sunfi karfinka” dariya yayi yace “Mommy I’m man enough to control kowace kalan mace na aura your Son is not a boy” yasaketa yawuce saikuma yadawo ashagwabe yace “Moma we will be having wedding on 23rd get ready invite all your friends, I want my side furnitures change, sannan agayara my main flat” yanuna wani arnen flat dake dayan barayin gidan dasauri Mommy tace “no Khaleel you will never leave my sight gaskiya side dinka dake cikin flat dina zaka dinga zama not bangaren chan kaji ba” wucewa yayi abinsa batare daya kulata ba yatafi sama gym dinshi yashiga yashiga yin exercise kafin daga bisani yafada shower yayi wanka yafito Sam haryazo suka tafi party abinsu.

EPISODE 5️⃣4️⃣

Ranan gabaki daya Hawwa jitayi batajin dadin komi, har Ramla saida taga Hawwa was not in good mood sabida yanda tai shiru batama iya magana da kyau, sai lissafi take how zata fita daga this mess? Idan yanuna video ko pictures yacema Baba tayi kokarin mai fyade duk zasu yarda ta ina kunya zai barta ta kallesu dagashi har Ammi that means everything Ni'ima said is true about her.
Washe gari tsaf ta shirya ta tafi aiki around 12 DIG yakirata tashigo office nashi murmushi yamata yace "okay Ogana gabaki daya yakirani yace nabaki leave sabida kiyi planning wedding naki da kyau an baki 60 days" zaro idanu Hawwa tayi tace "Innalillahi 60 days that's 2month, mezanyi da all this time Sir"? Dan murmushi DIG yamata yace "Hawwa have you seen abinda nafada miki jiya? Imagine danaje wajen Babanki to, wannan da Ogana ne yakira yace abaki 2months wedding leave abinda 3weeks ake bayarwa but naki is different, so zaki iya tafiya, we will see you on the wedding day in sha Allah idan kinyi inviting namu, Hawwa May Allah bless your home, Allah miki albarka, nasanki da ibada da yawan azumi Allah shine maganin komi so call on to him shine yasan wats best for you" kuka taji yana zuwan mata amman tahadiye ta gyadamai kai ta tashi ahankali tafito tana tafiya zuwa office nata wani officer yace "Miss Hawwa kinada bakuwa bamu barta tashigo nan ba tana chan" yamata pointing waiting room nasu, da mamaki tadinga tunanin waye ko wacece zatazo wajenta, dudda Ammi na hanya dan yau zata dawo amman ai baici ta iso ba tace mata by 11 zatabar gida, why is she even thinking of Ammi? Ammi bazata taba zuwa wajen aikinta ba, hanyar waiting tayi ganin Ni'ima taci gayu cikin atampa mai kyau ta yafa dan gyale ta rike handbag a hannunta yasa ta tsaya turus Ni'ima tamata murmushi kawai ta taso da gudu tazo batai wata wata ba ta rungumeta tace "Best suprise" chak Hawwa ta tsaya without hugging her back harsaida Ni'ima tadago ta kalleta tace "are you not happy to see me?" Dan girgizamata kai Hawwa tayi tace "no is not like that" dasauri Niima tace "muje office naki anata kallonmu anan" kawai takama hannun Hawwa, ahankali Hawwa tabita har zuwa office nata suka shiga idanunta ne suka sauka akan iPhone 15 pro max na Hawwa dake kan table last she check Hawwa was using Samsung S10 harya chanza mata wayane? Lallai gayen nan, abu taji ya tsaya mata arai dasauri tasaki hannun Hawwa tai wajen wayan tadauka tace "wow kin chanza waya Hawwa? Kin koma iPhone? Ni fa banson iPhone ance basu rike charge duk application saika saya? Baka iya downloading movies anyhow, komi kudi, Ke kika siya ko mijinki ya saya miki"? Karasowa Hawwa tayi ciki tazauna ahankali tace "shi ne" wani irin

murmushi Ni’ima tana danne bakin ciki da zafi datakeji aranta tayi tace “awwwn lovebirds, ohh my my, Hawwa I’m happy for you Allah yaga how patient you are yabaki mai sonki, wai yaushe kuka hadu ne baki taba bani labarinsa ba, eh yaushe kuka hadu?” Baki Hawwa tabude zatai magana akai knocking kofan da sauri dukansu suka kalli kofan Abraham ne ganin Ni’ima yasa ya tsaya yace “can I see you Miss Hawwa”? Gyadamai kai tayi tace “sure” ta mike suka fice tarufe kofan dawani irin sauri Ni’ima ta danna screen din wayan ganin babu password yasa tashiga cikin wayan dasauri tace “calls” call log tashiga d only number datai magana dashi for long batai saving ba saina Ammi datai saving da Ammi hakan yasa tashiga kwashe number da she’s sure Khaleel ne dan ya kikkirata bata dagawa daidai tana gama kwasa tanaji ana taba kofan da sauri tafita tarufe wayan ta ijiye kan table Hawwa ta shigo rike da Maltina ta ijiye gaban Niima, Ni’ima tace “thank you Best” Hawwa ta zauna Ni’ima tace “gist me Best ya shirye shirye? Kayan daki kayan kitchen? Na kaiki wajen wanda yamin na dakina?” Ahankali Hawwa tace “Baba da Ammi are in charge of everything bansan mesuke ba” gyadamata kai Ni’ima tayi saikuma tace “wai har yanzu kin rikeni azuciye ne? Best I’m really sorry wlh ina sonki you mean the world word to me kinji” dan lumshe idanu Hawwa tayi saita gyadamata kai tareda bude idon, Ni’ima tace “anko fa? Nafitar miki da anko?” Shiru Hawwa tayi saikuma ta gyada mata kai, murmushi Ni’ima tayi tace “thank you, can you call Baban Yaseer for me yanzu da wayan naki”? Shiru Hawwa tayi all maganganun Ammi nadawo mata ahankali tace “Ni’ima banso nakara shiga lamarinki da Baban Yaseer I promise kaina that, for licence naki nayi magana za’a samu nasara in sha Allah” murmushin karfin hali Ni’ima tayi tana danne abinda takeji azuciyanta tace “shikenan hakan ma I’m grateful after kalan abinda namiki not everyone will even help me that much, kinada zuciya mai kyau Hawwa, thank you” gyadamata kai Hawwa tayi, daidai nan wayan Hawwa yahau ringing Ni’ima ta saci kallon screen din ganin number data kwashe ne kaman Hawwa bazata dauka ba, but ganin Ni’ima and tanaso tanunama Ni’ima she’s cool with Khaleel kodan tacire tunanin Baban Yaseer da ita aranta yasa gently tadauka takai kunnenta, murya chan kasa Khaleel yace “I sent a delivery guy what’s your office number”? Shiru tayi chan tace “baza’abarshi ya shigoba” dan murmushi yayi yace “no one can stop my delivery, office number Kulu” murya chan kasa tace “0040” katse wayan yayi almost 1min saiga knocking anatse Hawwa tace “come in” bude kofan akayi wani delivery guy ne rike da flowers na red roses da akai wrapping katon gaske, saikuma platter na yan gayu na different intercontinental dishes da note ajikin both of them delivery guy din yace “I’m looking for Mrs Hawwa Alhassan Ibrahim Khaleel” Ni’ima jitayi yawun bakinta yayi daci da kyar tahadiye, ahankali Hawwa ta mike ta nunamai table din zuwa yayi yafara mika mata flowers din dake kamshi sosai like Khaleel plus kamshin roses again, office din yacika da kamshi, karba tayi ta ijiye sannan yabata platter na abincin shima ta ijiye

yabata note nashi tai signing sannan ya tafi, kafin Hawwa ta zauna har Ni’ima tasa hannu tadauki card dayayi note ajiki tace “love bird bari muga meya rubuta miki” dasauri kafin Hawwa tace wani abu, tace “_I know you haven’t had breakfast banson matana looking skinny you are too light for my liking, eat and get chubby, cheers to starting your leave today! Sowie about yesterday with love Mijin

Kulu  _”

Murmushin dole Ni’ima tayi ta ijiye card din, taja platter box na abincin tana budewa tace “eat mana” wow tafadi ahankali lafiyayen abinci ne aciki dat are very hot, mash potatoes da chicken wings, samosas, Pasta sai Mandi rice, ga salad ga fruits juice very cold ga sweet da cingum na mentos, kallon abincin itama Hawwa take, deep down she feels happy but then she don’t wanna feel d happiness ahankali tace “ke kici idan zakici” dasauri Niima ta girgiza kai tace “a’a inacin abinci nafito” gyadamata kai Hawwa tayi saita rufe platter ta matsar gefe idanunta suka sake saika akan rose din kawai ta tsaresu da idanu Niima duk na kallonta, aranta tace “munafukar mugun son mijinta take amman tana bobboyewa, hala ma sun riga sun sadu” wayan Hawwa ya shiga ringing dasauri ta waigo ganin Khaleel ne yasa ahankali tadauki wayan takai kunne murya chan kasa Khaleel yace “have you eaten? Is the food good? Kona chanza mana Chef? Shizai dinga mana girki bayan auren mu, abincin yayi”? Shiru Hawwa tayi murya ciki ciki tace “mesa baka dafa da kanka ba”? Dan zaro idanu Khaleel yayi yace “Momy bata barina in kitchen I don’t know me akayi a kitchen” murya chan kasa Hawwa tace “uhnn Moms boy” murmushi kadan Khaleel yayi yace “do you like the rose?” Kin magana Hawwa tayi, ahankali Khaleel yace “but I said sowie about yesterday” murya chan kasa Hawwa tace “sowie is not sorry” dan dariya kadan Khaleel yayi ahankali yace “wa akace tana tareda ke a office?”

EPISODE 

Faduwa gabanta yayi jin tambayan daya mata, hakanan sai takasa magana, “answer me” yafadi da kakkausan murya still kin magana tayi sai kawai ta zare wayan daga kunnenta takatse ta ijiye takalli Ni’ima ahankali tace “zan tafi gida natashi” tashi Ni’ima tayi tace “toh nima bari natafi, bari natayaki daukan rose din saike ki dauki platter” wani iri Hawwa taji amman saita daure ta mike tashiga hada abubuwanta tadauki car key suka fito tare ita tana rikeda platter Ni’ima na rike da rose din har zuwa inda motar Hawwa yake, Ni’ima sai kallon motar take tanaji kaman tahadiye zuciya ta

mutu idanunta harsun kada sun chanza, abayan motan sukasa komi Ni’ima na kallon motan irin wannan fa ba tokunbo car Hawwa ke dashi ba no, asalin sabuwa gal ce, komi na motan ba ariga an daye mata ledaba, maida kofan bayan Hawwa tayi tarufe tace “bye” tawuce ta shiga gaba Ni’ima na tsaye tana kallonta, Hawwa taja mota tabar wajen abinta, da kyar Ni’ima ta iya wucewa zuwa wajen tata motar zuciyanta kaman an barbada busheshen barkono da danye tsabagen azaban radadi dayake mata, sai kawai ta tsaya tana kallon motan ta, motar Hawwa tada Toyota Camry ce 2006/2007 ita lokacin da Baban Yaseer yabata Camry nan na 2014 kaman zata haukace dan tafi na Hawwa kyau da tsada gata latest, but yanzu dataga motan da Hawwa keja benz datakai irin 150M sai taji ta tsani tata motar, saitaji ta rainata, wai tayaya ma rana daya Allah zai dauki miji mai bala’in kudi yabama Hawwa ne? Eh? Within a blink of an eye rayuwan Hawwa ya chanza kakap, big phone iPhone 15 pro max, ita tana fama da Samsung S21 dinta da ada takejin dadi yafi na Hawwa S10, Hawwa ce big car, ga sadaki mai tsoka, ga gwalagwalai, Hawwa ko sisi taki bata, da dane da hala yanzu Hawwa tabata like 20M from that sadaki wlh dan Hawwa bata kyashin bata abu, Hawwa is going to big house now and yaron seems to love her alot, jibi yanda yake bata gifts, ranan su diamond agogo dasu turare yau abinci da flowers masu tsinannen kamshin dadi, he’s so romantic, she thought babu miji that will be as sweet and romantic as Baban Yaseer yanzu taga wanda yafisa.
Hawwa ta hadu da irin gayen kan taki fadamata har sai bayan tayi hauka? The way suke soyayya hakan nan she can swear Hawwa tadan jima da sannin gayen? Wannan dayaketa bata gifts sunyi sex ne? Hawwa is so happy she wants her to be sad, tafison taga hawaye da bakin ciki da bacin rai da damuwa akan fuskanta, wannan gayen ya shigo rayuwanta yasa Hawwa ta chanza bata damu da itaba yanzu, imagine wai ita Hawwa ke shama kamshi, what will she do yanzu? Da kyar ta lallaba tashiga motan ta tada tabar wajen tana tana tafiya akan titi tazo ta wajajen banex ta kalli masu bara dake wajen, sai kawai tayi parking motan tafito taje wajensu tace “zan baku kyautan kudi sosai amman saikun bani wayanku na tura wani sako” har rige rigen bata wayan ake, kakkarba tayi marasa kati har tana samusu ta bank dinta, sako tashiga turama number Khaleel da kusan duka number su sannan ta basu 5k suraba tawuce takoma mota tana murmushi taja abinta zuwa gida.
**

Khaleel na cikin mota tareda Sam wayanshi yayi kara daukan wayan yayi yaga messages guda 5 from different numbers hardly unknown ke kiranshi ma talk more of sako, kaman bazai budeba saikuma yabude daya.
“_Hawwa is a whore! Tsohuwan karuwa ce she sleeps with everyman dayake zuwa yace yana sonta saisa suke guduwa basa aurenta sabida tabasu abinda suke nema_”

Chak Khaleel ya tsaya yana kallon messege din to be very very honest he doesn't care idan Hawwa sleeps around or not cus yasan tun zamanin da wato old days aka daina samin virgins, konji is real babu yanda za'ayi yataso maka baka nemi wanda you will sleep with ba so what ai d'ane tayi, baida right to judge her life is not easy takai this years 29 without a man, shi tun yana 24 yafara ai, but dudda haka saiyaji still zuciyanshi namai wani iri sai kawai ya ijiye wayan da sauri without opening sauran messages din ahankali yace "park the car" Dasauri Sam yace "lafiya? We are not there yet" dan murmushi Khaleel yamai yace "just give me a moment" fita yayi daga motan yafara tafiya zuwa chan gefen titi baitaba sani akwai randa za'a gayamai wata yar iska ce harma yaji abun yadameshi ba, ko yadingajin ciwo aransa ba, duk sai yaji wani iri, who even send the message? What if is Hawwa? He don't think she will ever defame kanta dudda yasan batason auren su but Hawwa is someone that value self respect and image nata, ko kadan batason compromising self respect and imagine nata saisa he even use that picture and threaten her with it, cus yasan she will not want him to expose that koda ba gaskiya bane dan she values her self respect, juyowa yayi yakalli Salman daya fito daga motan yana kallonsa da hannu yama Salman alamu daya daukomai wayansa amota daukowa yayi yazo wajen yakawomai dasauri ya karba yabude second message din.
"_Hawwa babe din boss dinta ne DIG she slept with him in order ya dauketa yasata a task force din nan dan she was an ordinary police girl before without any star_"
Sai another message. "_Officer Hawwa sleep with yaran office example Abraham data girmeshi da shekaru slept with Hawwa countless times_",
Yanda zuciyan Khaleel ke bugawa kasa cigaba da bude sauran messages din yayi ya manna ma Salman wayan a kirjinshi yace "track those numbers all of them for me, track them! I need information uuughhhhh!" Ya dunkule hannu yayi punching air yawuce fiuuuu yatafi mota ya shiga da kanshi yarufo da mahaukacin karfi akaja motan Sam yace "lafiya are you okay"? Lumshe idanu yayi yaki magana har sukakai party saukowa yana shiga yadauki about 5 shots na tequila yana sha Sam yace "Lee are you okay? Why are you drinking like that" ko kallonshi baiyiba shaye shayen dayahau yi saida yabama duka abokanshi tsoro saida yayı total out sannan Sam da Moh suka kaishi sama aka kwantar dashi agado Moh yace "kasan what's wrong with him"? Girgixamai kai yayi suka wuce suka fita daga dakin aka barshi warwas agado.

EPISODE 

Washegari Khaleel yafarka adakinsa da kyar ya lallaba yaje yayi salla wuraren 9, ko wanka baiyiba yafito yasauko kasa Mommy na falo tace “good morning Son” ko kallonta baiyiba Noor ta taho wajenshi da gudu tace “Daddy” kanta yashafa kadan yace “go to grandma I’m coming Noor” yafice idanunshi sunyi ja duk sun nuna alamun bacci, yayi waje yana kallon Salman daya taho da sauri Khaleel yace “ya?” Salman yace “we tracked the numbers duka numbers din beggars ne dake hanyar banex, da kyar bayan nabasu kudi suka iya sanar dani wata mace ce tazo tabasu 5k tayi amfani da wayansu” dasauri Khaleel yace “did you ask them description nata?” Salman yace “yeah wai batada tsawo sosai she’s very fair and da Toyota tazo” shiru Khaleel yayi kaman mai tunani, kawai yawuce wajen motar sa Salman yabiyosa ya shiga driver ma yashiga sukabar gidan, ahankali cikin muryan gajiya da bacin rai yace “my wife’s house” jan motan sukayi har zuwa unguwan su Hawwa.
Baba na kofar gida azaune da aswaki a bakinsa ya hango mota yasan Khaleel ne kawai sai yafara murmushi kafin ma abudemai Khaleel yabude da kanshi yafito Baba ya tsareshi da idanu ganin idanunshi adan kumbure hakama fuskanshi dasauri Baba yataso shima Khaleel yawuce wajen Baba kafin yayi magana har Baba yakai hannunsa kan fuskanshi cikeda so yace “bakada lafiya ne Ibrahima”?Baba Khaleel ya kalla dan ranshi abace yake yayi shiru yakasa magana sai dan huci da yasauke Baba sai kawai hankalinsa yatashi yace “meya sameka? Tell me”? Dan ijiyan zuciya yasauke yajuyo yakalli Salman da hannu yamai alamu yakawomai wayanshi wayan aka kawomai muryan Khaleel ba dadi yanunama Baba wayanshi yace “Baba wasu sakonni aka turamin marasa dadi bazan iya karanta maka ba kaima, nasa ammin tracking number” yadanyi shiru Baba da gabanshi ke faduwa yace “ina jinka gayamin menene ke faruwa”? Cikeda jin zafi Khaleel yace “Baba matana ta batamin rai sosai, ina kyautata zaton har yanzu tana tareda mahaukaciyan nan, so nazo na ganta ne”

Dudda Baba baiga sakon ba but ayanda yaga Khaleel yasan Ni’ima tayi wani abu ranshi inyayi dubu yabaci tsabagen bacin rai yace “muje ka shiga gidan kacimata mutunci ba anan waje zan kiramaka itaba, ai gidana nakane ban maka iyaka da ko’ina acikin gidannan ba, muje” Baba yayi gaba Khaleel yabishi abaya suka shiga cikin gidan ko’ina a gyare ta buga sallama gaban dakin Hawwa, Ammi ta amsa yace “da mijin Hawwa nazo Zainabu” Hawwa dake zaune daga ita sai dan rigan bacci tana danna wayanta dasauri tadauki hijabi tasaka dark blue har kasa, ita dama Ammi da hijabi ajikinta Ramla kuma na kitchen tana aiki dasauri Ammi ta tashi da fara’a tace “bismillah bismillah kushigo” shigowa Baba yayi Khaleel biyeda shi abaya, kan Khaleel na kasa yace “ina kwana Mom”

“muntashi lpy Khaleel” ahankali Baba yace “biyoni Ammi” binshi Ammi tayi suka fice daga dakin tareda maido musu da kofan suka rufe, Khaleel yazuba hannu a pocket nashi yana kallon Hawwa dako dagokai batayi ta kalli inda yakeba, kaman ma batasan da mutum awajen ba, Babu wasa kan fuskanshi rai abace yace “wacece ke tareda ke jiya a office?” Batare da Hawwa ta kalleshi ba tace “da wanda nake tare, ko wanda nai magana, ko wanda nagani a office is none of your damn business” ran Khaleel abace ya daka mata tsawa da saida dakin ya amsa. “Nace dawa kike tare jiya an office!”? Dagokai Hawwa tayi adan tsorace sabida yanda yayi mata tsawa ta tabbata anji a tsakar gidan, tashi tayi daga gadon ta taho inda yake dasauri dan bataso su Ammi suji tanamai ihu suhau mata fada akanshi, hakan yasa tace “who do you think you are kanamin ihu aka?” Ran Khaleel abace yanunata da hannu yace “dawa kike tare an office jiya?” “My friend!” Hawwa ta amsa kai tsaye ganin yadameta da tambayan, cikeda jin haushi tace “I was with Ni’ima me akayi? Sabida an auramin kai saina tambayeka kafin naga kawata konai magana da kawata”? Wani irin fizgota Khaleel yayi yakai hannunshi zuwa wuyanta ranshi abace yace “what is so special about that witch of a woman da kin kasa hakura da ita? Are you a lesbian!? Are you really into girls?”

Ja idanun Hawwa suka soma yi tafara dukan hannunshi hakan yasa yasaki wuyanta tadanyi tari kadan sannan ta kalleshi tace “da aurenka gwara zama da Ni’ima! At least ita bata living wayward life irin naka!”Radadi zuciyan Khaleel yafara sai kawai yakara fizgo Hawwa yakama kafadunta ya matse yana kallon cikin idanunta zuciya yakaimai wuya da kishi kai da komi ma ganin yanda Hawwa ke son Ni’ima yace “idan nakara ganin ki da yarinyar nan i will killl her! I will ruin her life! I will make her life a living hell you know me so well to know duk abinda nakeso nayi sainayi, stay away from that witch evil vile woman inba hakaba saina kasheta!”

EPISODE 5️⃣7️⃣

Ayanda yau taga idanun Khaleel saida Hawwa ta tsorata wlh, bata taba ganinshi haka ba, yanda ranshi yakai ga baci yasa kawai ya turata yajuya yabude kofa yafito Baba da Ammi na tsakar gidan sunyi charko charko a tsaye, yama kasa kallonsu sabida baison suga kwayan idanunshi yawuce zaure da sauri Ammi tabiyoshi daidai ya shiga zaure tace “Ibrahim!” Chak Khaleel ya tsaya batare daya juyoba, dasauri Ammi ta taho tazagayo ta gabanshi sai kawai Ammi tasa hannu takamashi ta zaunar dashi kan bench dake zauren ahankali yazauna sai kawai yakai hannayensa biyu yarufe

fuskansa yafuzar da iska masu zafi kaman zai kama da wuta sakonnin nan nacimai rai, ahankali Ammi tace “it’s okay ya isa Khaleel ya isa” sauke hannunshi yayi ya gyadamata kai ahankali yace “thank you Mom” anatse Ammi cikin hikima tace “can you show me sakonnin da aka turamaka game da Hawwa”? Araunane ya girgiza kai yace “Mom banso kowa yagani, sirrin matana ne I can’t show you banso kumata wani kallo” kirji Ammi tanuna tace “nine mahaifiyar Hawwa, show me Ibrahim idan akwai abinda yakamata namaka bayani zan maka, banso ku fara aure da zargi ko kokonto aranka, ayanda abin ke tafiya nan gaba hala za’a iya maka sakonnin dayafi wayan nan daci ma da tada hankali ma, so show me” Allah yasani sabida nauyin Ammi dayakeji ne yasa gently yamikama Ammi wayanshi daya bude mata message yace “5 numbers suka turo sakkonni, nasa anmin tracking akace lambobin wasu beggars ne, jiya danai magana da ita suna tare a office dinta, I believe somehow she took my number from wayan Matana batare datasan anyi ba” duka sakon nin Ammi tabi takaranta ran Ammi yama Ammi badadi sai kuma takaraji ta natsu da Khaleel tama aminta dashi gabaki daya, dawani ne da yasaketa yace yafasa aure but shi yazo kawai yayi warning nata kan zama da Ni’ima ne, ahankali tace “Khaleel wlh karyane kazafi akeso ama Hawwa! Babu wani abu na Hawwa daban sani ba, Ni’ima so take takashe auren ku, wlh Hawwa bata taba soyayya da Oganta ba, Hawwa maza tsofaffi ma basa burgeta, sheri ne diyata ba haka takeba, sai kuma abokin aikinta Abraham tabbas ta sanar dani yaron na bibiyanta shima bawai ya iya yafurta da bakinsa yana sonta ba, ai bata bashi fuska, yana mugun shakkanta, Hawwa bazata taba iya soyayya da wanda ta girma ba Khaleel kuma wanda yake ba addininta ba, saikuma na karshe sauran samarinta“ anatse Ammi tace “Ibrahim Hawwa na can be everything, stubborn, mafadaciya da sauransu amman Hawwa na ba mazinaciya bace! Dudda ta dade batai aure ba bata taba kallon zina as solution na matsalolinta ba, duk ina maka bayanin nan sabida ni uwa ce bazanga ana so akashe auren y’ata naja baki nai shiru ba, duka sakon nin nan karya ne Khaleel koda bakai trusting Hawwa ba trust me ni mahaifiyarta, I will never lie to you kaji”.

Sosai Khaleel yake kallon Ammi natsuwan da tun jiya yakasa samu bayan yaga sakonnin nan sai Ammi tabashi natsuwan in just few minutes ya yarda and he believed her, gyadama Ammi kai yayi ahankali yace “I know! Deep down I know my wife is not like this, kawai bansan mesa zuciyana keta zafi yana radadi ba bayan na karance messages din” yasan inda Hawwa yar iska ce da bazata taba tsanan halinshi ba, sabida batayi saisa she despise his way of life, dan murmushi kadan Ammi tayi tace “sabida kana sonta ne saisa kakejin haka!” Tsare Ammi Khaleel yayi da ido jin tace yanason Hawwa bayan shi yasan baya sonta he just wants to show her he can have her idan yanaso, ahankali Ammi tace “Khaleel aure

Hawwa na zaune kan dadduma tareda Noor sun idar tana koyama Noor azkar yarinyar is 4 amman wai bata zuwa islamiyya sannan babu mai koya mata agida, Baba kuma na hira da Ammi da Dado da Anty Lami Miemie da Ramla basa dakin sallama akayi Aminu ya bude kofan dakin yashigo dawata katuwar kwali na LG washing machine saiga su Hafsat duka biye dashi Hawwa tabisu da kallo Ammi tace “a’ah wannan kuma menene Aminu haka”? Dan murmushi yayi yakalli Hawwa dake kallonsu yace “Ammi hada kudi mukayi muka saiwa Ya Hawwa washing machine na tambayi Hafsa tace shine kadai baku sayo ba dakukaje sayayyan kayan daki” yadanyi shiru yakalli Hawwa ahankali yace “Ya Hawwa I wish nafara aiki and I wish I can afford more than this wlh Ya Hawwa zan iya baki duka duniyan nan kin chanchanci haka”dakin kowa yayi tsit yana kallonsu, Ahankali Hafsa tashare hawayen daya zubomata tace “Ya Hawwa baki taba kallonmu kaman yaran kishiya ba, ko ki kallemu da abinda Umma take miki, Ya Hawwa da Baby Minal na ciwo bataci abinci ance a asibiti she is under weight Babanta baida kudin soyamata abinci” tai dan shiru saikuma tafashe da kuka sosai tace “Ya Hawwa kadaice tafito da kudi tadinga siyanma Minal abincin yara daban daban, kala kala, wlh babu wanda bata siyamana ba, cerelac su gaber rice babu kalan abincin yara da bata soyama Minal ba har yarinyar tazo tafara ci tanata kumari” ahankali Hawwa ta tashi dagakan dadduma idanunta yayi ja kanninta are making her emotional, Hafsa tace “I wish kowa aduniya zai sami big sister kaman Ya Hawwa, she takes care of dukanmu zuciyan Ya Hawwa daban ne, she’s too good” hannu Hawwa tabude mata dasauri Hafsa ta rungumeta tsamtsam a jikinta su Khadija ma haka, Aminu Hawwa ta kalla tace “come here big head” zuwa yayi tabashi side hug tareda shafa kanshi hawaye na zubowa daga idanunta she wish this was real marraige, all this farin cikin da yan uwanta keyi she wished for mutum better than Khaleel sukemawa, su Ammi kowa saida ya goge kwalla ganin Hawwa dasu Aminu, ahankali Hawwa tace “zan dinga amfani da washing machine din nan kullum kobanda wanki ma” dariya duk sukahau yi su da ke kuka daidai nan akai sallama ana bude kofan dakin duk suka dago Umma ce sanye da Hijabi kowa ya tsaya turus

yana kallonta Umma bata taba shigowa dakin ba, Hawwa ta kalla daga bakin kofan tace “nashigo?” Gyadamata kai Hawwa tayi da sauri shigowa Umma tayi tazo gaban Hawwa ga mamakin kowa kawai saitai kasa zata duka dasauri Hawwa tariketa tace “Umma mehaka”? Fashewa tayi da kuka kawai tace “Hawwa ki yafeni ki gafarceni duk abinda na miki na dauramiki tsana akan abinda baki duniya akayi, na dinga miki mugun fata kema ki dade baki aure ba kaman yanda mahaifinki yamini, nayi kuskure amman yarana sun ganar dani, sun nunamin hanyar gaskiya Hawwa kiyakuri dan girman Allah” Dasauri Hawwa tace “Umma wlh bakımın komiba kiyakuri ki yafeba both Babana da Mamana abinda suka miki kinji” Gyadamata kai tayi tace “na yafe musu har abada” ta rungume Hawwa tace “Allah yamiki albarka, Allah ya albarkaci aurenki yabaku zaman lafiya da yara masu albarka” kowa na dakin harda Baba sukace Ameen, Umma tadauko tadauki ledan data taho dashi tabude atampa mai kyau ne ciganvi na gold irin na 15k dinnan tace “ga gudunmawa kinji” cikeda farin ciki Hawwa tace “Umma wayyooo Allah na nagode Umma tayi kyau ina sonta wlh saida salla zan dinga nasaka” Umma ta washe baki she loves yanda Hawwa ta nuna tanaso itadakeda atampopin millions a akwati Hawwa tawuce takaima Baba dasu Ammi tace “Baba Ammi kallo abinda Umma na tabani” Baba da Ammi tace akashe lafiya zuwa wajen dash Baba suke Umma tayi tace “Zainab Malam kuma kuyafemin” Ammi tace “Zainab komi yawuce amanta da baya” Baba yace “nayafe miki Zainabu nima kiyafeni” ahankali tace “nayafe Allah ya yafemana duka yahadamu a Aljanna” kowa yace Ameen, tace “Zainabu meya rage ba’ayiba? Mezanyi?” Ahankali Ammi tace “jere za’aje gobe agidanta inaso ke zaki jagoranci abin Umma, ga Lami kuma” Umma tace “ba matsala Allah yakaimu gobe da rai da lafiya” kawai suka shiga hira ana planning biki gobe dan akwai dinner da daddare karfe takwas Hawwa sai kallon kowa take adakin one big happy family all this farin cikin da planning bikinta hala nan da wata daya, ko sati daya, ko sati biyu yasaketa fa ko? Gashi mashayi, dan party, dazata gayamusu bazasu yarda ba, babu mai daukar bad magana akan Khaleel, lallen hannunta dayayi fitinannen kyau ta kalla wai itane zatai aure yanzu, kiranta Munawwarah tayi hakan yasa ta tashi ta kwantar da Noor datai bacci agado tawuce taje ganin magani zata bata yasa tace “ba Ammi tace adakata ba Anty” Munnawara ta dungure mata kai tace “wannan ba maganin mata bane, maganin cicciko da naman gaba ne taciki, batace kar abaki wannan ba ai, shanye nidai kibani kitafi” kama hanci Hawwa tayi tasha da kyar tanayi kaman satai amai Munawwarah tace “za’asha daga kafin afasa” Dasauri Hawwa tace “meza’a fasa”? Dan bata gane maganan ba Munawwarah tace “tashi kije nidai bacci zanyi” tashi Hawwa tayi tafice abinta taje ta kwanta. EPISODE 7️⃣

3️⃣

Da asuba Ammi ta tada Hawwa dan ta hada important kayanta datake bukata su Hafsat suka tayata akwati daya tahada na kayan datakeso uniform nata da credentials dinta, Umma ta karba sannan su Ammi da manyan maza suka shiga kai kayan Hawwa zuwa trailer da Khaleel ya aiko musu aka fitar da komi waje, zuwa around 10 mata suka shiga jeep da yazo daukan su, Aminu ma yabisu as namiji aka tafi dasu jere gidan Hawwa.

Kowa saida yayi salati dasukaga gidan Hawwa gate harsun gaji da kirgawa ga yan sanda da sojoji tako'ina, Mommy na tsaye wajen window office nata su Umma suka sauko daga mota tsaki tayi tace "bunch of local people look at them" tawuce ciki Excellency na falo tareda Khaleel daya kwanta yasa kansa akan cinyansa yana chatting abinsa cikeda masifa tace "wai Khaleely akanme zakaje kayi aure from this local family kuma harda biki maisa ba'ayi descreet marraige damuka sabayi ba? Wlh kunyan gayyatan mutanena reception na yau nake sabida kalan yar gidansu wayanda ka auro, batare da Khaleel ya dagoba yace "Pops talk to Mommm oooooo" Dasauri Excellency yadan rufe Mommy da fada yace "wai me haka Madam? How many time will you go forth and back on this matter eh? Kibar yaro yayi abinda yakeso idanma destination wedding yakeso let it be, meruwan mu da family su ko status nasu badai ya auri abinda yakeso ba fakat!"
Tashi zaune Khaleel yayi yakalli Mom cikeda rashin mutunci yace "ko kallon banza kikama family matana you will see the other side of me Mom" yana maganan yawuce hanyan side nashi yace "ask the workers akaimu su abinci da drinks" kaman Mommy zatai kuka cikin masifa tace "PA" zuwa yarinyar tayi da gudu Momy tace "attend to Khaleely Inlaws" ran Mommy abace tawuce fuuu tayi ciki Excellency yabita da kallo yana kadakai kafin ya cigaba da waya abinshi yau da gobe da jibi yadauki off sabida bikin dansa.

Mutane cike gidansu Hawwa kaman zasu zauna akatanga sabida yanda jama'a suka cika ko'ina, Hawwa na daki tayi wanka tasaka atampa mai bala'in kyau dinkin yamata sai addu'a ake ana mata Allah sanya alheri.
Wuraren 5 stylist nata da makeup artist nata suka fara shiryata in white gown around 7:30 aka gama shiryata lokacin duk an tafi da yan gida hall, salla tayi sannan aka mata daurin kai, wani diamond sarka aka samata Hawwa was screaming money ya Allah ita kanta data kalli madubi sai kawai ta tsaya dan she can't believe itace, bata taba sanın she's this beautiful ba, she looks like all this

instagram brides da ake gani online, dagata sukayi Hafsy dake rike da wayanta tace “mijinki sai kira yake Hawwa” kin magana tayi dan batajin dadin komi fita waje sukayi wani red roll Royce ke pake akofar gidansu da akai arranging da flowers ga motocin security gaba da baya bude mata akayi ta shiga ahankali batare data kalli Khaleel dake zaune yana kallonta ba aka rufe akaja motan hannunshi yakai zai taba bata tadauke dasauri shi kawai kallonta yake gobe tana dakinshi around this time dan tun 5 zai turo atafi da ita tahowa yayi yadaura fuskanshi akan shoulder nata yakawo wayanshi yayi snapping nasu yana murmushi yace “I have the most beautiful girl as my wife” mtswww Hawwa taja gajeren tsaki gaban hall din akai parking aka bude musu suka fito suka tsaya Moh yazo yana sanye da suit yace “you are late” Hawwa ya nuna da kanta ke kasa yace “matana tarikeni” “Welldone Mrs Lee” Sam yafadi yajuya yakoma ciki dan bride da grooom shigowansu su kadaine bayason hayaniyan mutane na binsu, daganan waje sukaji muryan MC yana ladies and gentlemen the moment is here, Momy and addy Uncle and sister the bride and groom gasunan abasu standing ovation DJ DJ” DJ yasaka wakan like my father by Jax wanda Khaleel yace asamai idan zasu shigo sabida Baba yabashi labarin Mahaifiyar Hawwa and he wants to communicate to Hawwa da wakan ya gayamata cewa he will loves her the way Baba loves her Mom,

Shiga Hall din Khaleel yayi da ita ya Allah Hawwa da Khaleel sunyi kyau watttttt 🔥 Tana sanye da white gown nata gawani net da aka dauramata akan gashinta da aka gyara yayi kyau kaman tasaka attachment, Khaleel na sanye da suit black yarike musu hannu, yanda ake kallonsu sai Hawwa taji kuka, wakan dake tashi that is so cool na ratsata kallonta Khaleel yayi cikeda so yanuna mata Baba dake sanye cikin kaya exactly irin na Excellency yana tareda excellency yana kallonsu yana murmushi sosai, kawo kanshi yayi saitin kunnenta suna tafiya yace “I will love you Hawwa just like the way Baba keson Maman ki har yau dudda she’s late, I will love you a million times more!” wani irin kallon Khaleel tayi tayi cus she felt his words har cikin heart nata cikeda so ya gyadamata kai yana kallonta.

Mommy datai shiga na alfarma tasha zinare sarkan jikinta har cıbiya ta tsaya tana kallon Khaleel da yanda taga yana kallon Hawwa daidai sun shigo tsakiyan hall din aka saki wannan hayakin soyayyan wanda duk aikin Juzzyfabevent ne dan ita tayi handling entire wedding decor din aka samusu wakan soyayya na Christina Perri A thousands years, Khaleel yasaki hannun Hawwa yanuna ta yana waka yana rawa Hawwa na kallonshi Excellency da Mom suka saki baki suna kallon Khaleel tunda suka haifeshi basu taba ganin Khaleel this happy ba ko ranan da aka haifi Noor but look at him,

today is the happiest day of his life ahankali Excellency yace “Khaleely this is not fun, you’re inlove” rawan yagama kawai yazo ya rungume Hawwa very tight akahau ihu Hawwa ta boye kanta ajikinshi sabida kunya dan har su DIG tagani dasu Abraham da Hayatu kowa ya gayyacesu oho, DJ yace “our shy shy bride”.

EPISODE 7️⃣4️⃣

Mommy was really scared yanda taga Khaleel was totally lost in love, baya second biyu cikakku batare daya kalli Hawwa ba, and ita yarinyar no even send her son, zata iya kirga sau nawa taga Hawwa ta kalli Khaleel shiko kaman zai cinyeta, Mom duk zuciyanta ya lalace.

Cewa akayi abada labarin Amarya Khaleel yace shi zai bayar kawai yafito yana kallon Hawwa dake kallonshi asanyaye yace “I have alot to say about matana da zan iyakaiwa gobe so I will make it brief” yayi shiru yana murmushi yace “my wife is a very special person, anytime idan zan tsokaneta i call her Kulu” aka kwashe da dariya a hall din, Khaleel yace “kona cemata Kululu kuluwa yar sanda” zokaga dariya Excellency yace ma Baba “haka kake bari yana tsokanar maka yarinya”?
Baba yayi dariya yace “barsu abinsu duk soyayya ce” murmushi Khaleel yayi yana kallonta sosai yace “my wife is the most intelligent and hardworking young lady dana taba gani a rayuwana the first ever one!”
Yayi shiru yace “the first day damuka hadu something happened I called her Ke” Khaleel yawani zaro idanu dayasa yan hall suka kwashe da dariya sabida reaction nashi tells abinda Hawwa tayi kaman comedy, cikeda tsokana yace “matana ta iya masifa” kai zokaga dariya a hall Hawwa ta sauke kanta kasa ahankali duk kunya yakamata, Momy ta haderai tam, murya chan kasa Khaleel yace “my wife is loyal! Honest, truthful and kind, she’s strict batason nonesense da rawan kai and she’s truly loving, she protected me and Noor, Hawwa means everything to me, and I’m her best friend hellooooooo” yawani daga hannu hall akace Hi ana dariya, yabada mic yakoma yazauna Sam yazo yabada labarin Khaleel shi sannan akace first couple dance da iyaye Khaleel yarike Hawwa suka fito Excellency Baba Ammi da Momy duk suka fito Mommy ta rungume Khaleel cikeda so tashiga share mai fuska yamata murmushi yana rikeda hannun Hawwa aka shiga manni aka koma.
Sai around 10 aka gama iyaye suka tafi yara aka tsaya after party su Hafsa sukakai Hawwa wani daki Kaman zatayi kuka tace “wai

ba’a gamaba” dük eh sukace kaya aka chanza mata zuwa wani pink gown dayamata kyau aka mata dauri aka fotoda ita Hawwa tayi kyau agaban hall taga Khaleel tasa wani crazy shirt ya bubbude botura yana mata wani irin kallo kaman maye da saida gabanta yafadi aka kirasu hall suka shiga suna kaiwa tsakiyan hall Khaleel yashiga juya Hawwa yana wani irin rawa da ita ana ihu chan kawai yahau kissing nata Hawwa naso ta kwace takasa ihuu ake a hall din na bala’i DJ kanshi saida yayi ihu a speaker yace “ango need a room guysss” dasauri Khaleel yasaketa ya rungumeta tsam ajikinshi cus harya sami erection baiso agani, yahau rawa ahaka da ita Hawwa kaman ta mutu da bakin ciki tawahala Khaleel ya wahalar da ita awajen rawa sai wajajen 2 nadare aka gama mota suka wuce tazauna zai kama hannunta ta dauke batacemai komiba aka fara tafiya lumshe idanu tayi wahalallen bacci yayi gaba da ita ahankali ta sauke kanta kan kafadar Khaleel tarike hannunshi kallonta yayi cikeda so saikawai yaciro wayanshi yamusu video yasaka a insta story, har sukakai gida bacci take, tsayawa motan yayi da gangan yakai hannunshi gaban riganta ya matsa boobs nata afirguce Hawwa ta farka takalleshi tace “mehaka”? Turobaki yayi yace “munzo gıda kona wuce dake gıdana? Hade fuska tayi daidai an bude mata kofa saukowa tayi ahankali tawuce cikin gidansu da kaman gari awaye hatta Noor batai bacci ba daki tawuce tarage kaya Ammi tabata ruwan zafi tafada bayi tai wanka tazo ta kwanta sai bacci tagaji, washe gari yinin biki by one za’ayi walima anan cikin gidansu agama by 4, anything 5 atafi da Amarya tunda Hawwa ta tashi taji kawai bakin ciki takeji
Ta kumbura tai tam Noor kawai tama wanka da kanta tasa mata kaya masu kyau tawuce ta tafi wajen su Miemie abinta, sata akaiyi tai wanka tasaka wani lace from akwatinta mai kyau za’amata makeup tana bataso su Hafsa suka fadama Ammi Ammi tace abarta dan tun safe taga kwayan idanunta, kwanciya tasakeyi agado Munawwarah tashigo tace “Oya tashi muje dakina” kaman Hawwa zatai kuka ta tashi tabita magunguna tabata daban daban Hawwa tasha taci farfesun da aka bata sannan tawuce takoma daki bayan anyi azahar aka shiryata Malama tazo na walima aka fito aka zazzauna wa’azi tayi kaman zamantakewan aure da hakkokan aure da yanda ake kissa dasauransu sai around 4 aka tashi aka hadu akai jam’i kafin ma su Idar Aminu ya shigo gidan yace “anzo daukan Amarya” Hawwa na sallame salla kawai saita fashe da kuka sosai awajen abin gwanin ban tausayi nan aka fara kaita wajen yan uwan Baba suka mata fada, Yan uwan mahaifiyarta suka mata fada, Abokanai arziki makota akama Hawwa fada sannan aka maidata dakinta lokacin around 5:35 Baba da Ammi ne zaune awajen su kasa kowa yafita.

Baba yasauke ijiyan zuciya yace “ina mika godiyana ga Allah subhanahu wata’ala daya nunamin aurenki Hawwarh, Hawwa na baki tarbiya nakuma san waye ke Hawwa kibi mijinki sau da kafa, nasan ayanda aurenku ya kasance amman inamai tabbatar miki

Khaleel na sonki baniba kowama yaga soyayyan nan ya shaida, Hawwa kada kiga kusan kanku daya banbancinku shekaru biyune tsakani kice bazaki girmamamsa ba, No ban yardaba kibama mijinki girmansa” Baba yace “yi nayi bari na bari, Dan Adam ajizini duk randa kuka sami sabani ku shirya kanku, nasan agidan iyayen mijinki zaki zauna dudda dai bangarenki daban ayanda Umma suka fada inaso ki kula da iyayensa kaman yanda kike kula da mu, ki girmama su ki daukesu tamkar ni da Ammin ki”.

EPISODE 7️⃣5️⃣

Baba yayi shiru yace “Ibrahima bai riga yace wani abu kan aikin ki ba koda nan gaba zai nuna ki barsa, ki barsa aure yafi aiki Hawwa, Allah yamiki albarka yabaku zaman lafiya, yabaku yara masu albarka, Hawwa ina sonki ina sonki amman yaune ranan barin gidan Baba zuwa gidanki Hawwa” wani kuka Hawwa taji yataso mata, she always wish tai aure tagaji da gidan Baba, takoma nata gidan but yau saitaji bata gaji da gidan Babanta ba bataso tabar gidan Babanta, Ammi ta sharemata hawaye tace “ya isa stop crying now, Allah yabaku zaman lafiya, banson dan kinyi aure gidan hutu ki sangarce Hawwa, ba ruwanki da yan aiki sai when necessary only when necessary, Hawwa ki dafa abincin mijinki da kanki ki basa yaci da kanki, ki gyara makwancinsa karki yarda kiba yan aiki daman gyara dakin mai gidanki, turaren wuta kullum ki kona agidanki safe dare Munnawara tamiki masu kyau duk an kai, ki zama mai tsafta komin aikin office ki dafama mijinki abinci kusan shine first kafin komi, ki tausasa muryanki a inda yake, idan yayi fushi ke karkiyi idan yana fada ki shiru Hawwa take care of yourself ki rike mijinki da kyau yanzu da Allah yabaki don’t let him go ko let him loose ki kamashi da abubuwan da kika iya na koyamiki, keba yarinya bane kinsan menake gaya, idan mijinki yakiraki ga shinfidarsa duk wani kalan gajiya dakikayi daga aiki ki amsashi kije gareshi Allah mimi albarka tashi kije da ni da mahaifinki mun sakeki lafiya mun yafe miki duk wani abu dakika mana jeki fara sabuwar rayuwanki cikeda albarka mu dakuma fatan alkhairin mu” zuciyan Hawwa har wani tsuma take takasa motsi sai kuka atare Baba da Ammi suka tashi sukazo inda take ko Wanne ya tsaya a side nata suka dagota gyaramata lullubi Ammi tayi sannan suka bude kofa sukai waje da ita Hawwa na kuka lokacin around 6 har zuwa kofar gida inda Jama’a suke jiranta, gaban wata sanuwan jeep dal da aka zagaye da flowers suka kaita tashiga kawia ta rungume Ammi da Baba da kyar suka zareta suka sata Ummu tareda Noor tashiga motan, Daddo tashiga gaba aka ja motan, kanninta suka shiga sauran motocin da yan unguwa kowa na so yaje yaga gidan

Hawwa aka wuce.
Wuraren 7:30 sukakai gidan motan Amarya ne kawai ba'ayi scanning ba sauran motocin saida akai scanning incase wani yadauki mugun makami compound din suka shiga da akai decorating irin na masu kudi ga jama'a acike ga abinci da drinks. Parking motan Amarya akayi gaban wani red flower carpet da aka shimfida body guard suka bude motan daidai Mom Sam da Hajiya Daraja da wasu tawagan manyan classic matan nera biyeda su faram faram suka gaisa da Daddo da Umma sukace afito da Amaryanmu tazo tafara gaida Maman Mijinta kafin akaita barayinta Juyawa sukayi suka fito da Hawwa ahankali wani sanyi Hawwa taji tana tuna memories nata na gidan nan which first one din is kidnapping na Noor second one din is rannan datazo daukan motanta taga wata na kissing Khaleel tako'ina Mom Sam tace "Masha Allah our beautiful bride" suka rike Hawwa da kanta ke kasa cikin lullubi aka wuce tawagan Hawwa na wucewa suna binsu har Side na Mom.

Mom na zaune kan wata hamshakiyan kujera tayi gayu harda makeup na bala'i ta zuba gwalagwalai awuya da hannu hannunta rike da bowl na fruits spa workers nata guda biyu sanye da uniform na matsa mata kafa aka shigo da Hawwa Hajiya Daraja tace "ga yarki an kawo miki Hajjaju" Daddo tace "kibiya kudin ganin fuska" aka kwashe da dariya Mom tabisu dawani irin kallon takaici but tuna maganan Khaleel ta daure takalli PA ta tace "basu konawa sukeso in any currency" bude wani jaka dake hannunta PA tayi tazo gaban Daddo tashiga zuba mata bandır bandır Daddo tace "ke ya isa" Mom Sam tace "bari mubude fuskanta" Yaye lullubin tayi fuskan Hawwa ya bayyana Mom ta tsareta da kallo kan Hawwa na kasa bayabo ba fallasa tace "welcome home" kan Hawwa akasa tace "akaita side nata" aka buga ayiriri aka fita Mom tabisu da mugun kallo taja mugun tsaki alwala aka.
Alwala aka farasa Hawwa tayi sannan aka shigar da ita side nata dake kamshin sababbin abubuwa babban mansion ne da dakunan ciki dasukai 10, duplex ne akwai elevator ga staircase gidan yahadu akwai falo kusan uku but main falon kayan designer na Khaleel ne, sama aka wuce da ita wasu yan kauye suna shiga lift yakaisu sama Hawwa aka bi bene da ita, wani daki suka bude wanda furnitures nasu ne aciki kuma yayi kyau sosai dan sun sai mata kaya mai kyau a all this turkish furnitures company bawai na Nigeria ba zaunar da ita Umma tayi kan gado Munnawara data biyosu tace "tashi kiyi salla zan baki magunguna" share fuskanta tayi tawuce tashiga bayi ya Allah bata taba ganin bayi mai kyau

Alwala tayi su Hafsa suka shiga kunna turaren wuta kowa murna yake cikinsu Yayarsu tasami gidan hutu jibi kalan gidan da Hawwa take ciki,Abinci aka shiga kawo musu ma'aikata da uniform kawai ke safa da marwa a flat din, salla Hawwa tayi wata makeup artist tashigo tazo mata makeup akwai event Hawwa kawai tahau kuka

wai tagaji da kyar su Umma suka lallashi ta aka mata makeup ta tashi tai sallan isha’i sannan aka shiryata cikin wani lafayan yan maiduguri ashe Excellency dan maiduguri ne, wai wushe wushe za’ayi welcoming nata around 10 akace sufito kan Hawwa na kasa kunya takeji suka fito an cika compound din ga Khaleel zaune gaban stage din cikin wani malum malum sai kallonta yake kaman yayi shekara bai ganta ba yaga duktai zuru zuru and she looks tired and even scared yanzu ne ta yarda sunyi aure sosai, kawota sukayi har wajensa yatashi ya karbeta yana murmushi murya chan kasa yace “you look so sad sabida baki ganni tunda kikazo bane” dan hararanshi tayi yasake mata murmushi kawai yaja hancinta yace “smile ita sunna” akahau ihu da sauri yakalli crowd din yama manta suna gaban mutane zama sukayi aka fara event din sai around 1 aka gama Khaleel yarike hannunta yace “tunda zasu kwana muje side dina mu kwana” fizge hannunta tayi daga nashi tace “don’t even go there” tsayawa yayi yana kallonta yace “to muje namiki massage saiki dawo kin gaji” makemai kafada tayi agajiye duk yana kallonta saikuma yace “marowaciya” kin kulashi tayi daidai su Hafsa sunzo wajen kawia tabisu suka tafi side nasu yana kallonta Sam yazo wajen yace “munafuki you’ve fallen deeply kasa amaidasu gıda kayi amarcinka mana” kaman zaiyi kuka yace “kunyansu nake lemme just be patient gobe kowa zai tafi ahhhhh”. Wankan ruwan turare akasa Hawwa tayi kawai ta chanza kaya tabi gado ahaka tai bacci tanajin hayaniyan yan uwanta sama sama washe gari da safe suka tashi aka shiga aiki ana kara gyara komi ana turara ko Hawwa gabanta sai fadi yake tuna yanda zasu tafi anjima.

EPISODE 7️⃣6️⃣

Mom da Excellecy na zaune afalo around 5 na yamma Khaleel yasauko daga side nashi wajen window yawuce direct yana daga labule yana duba ko suntafi, Excellency da Mommy suka bishi da kallo, ya leka yaduba yafi a kirga duk ya kosa su tafi, Mommy ta dauke kai kirjinta na tafarfasa ahankali tace “akan tsohuwa old cargo dinchan yake rawan jikin nan” Excellency dake kusa da ita yace “there’s no old cargo in love, please let him be zamanin da muna soyayya munyi wanda yafi haka” dasauri Mom ta kalleshi dagamata gira daya yayi duk haushi yakamata ganin baya gane abinda take fadi.
Shidda daidai duk suka fito Hawwa dake sanye dawani lafiyayyen gown na material red tabiyosu zuwa gaban kofa zata fito Umma tace “kul kada kifito” hawaye ne yazubo daga idanunta tace “Daddo Umma dan Allah karku tafi ku banni, Hafsa kudawo please” tafashe

da kuka sosai dayasa su Hafsa sukahau dariya, Umma tace “kinga kanninki suna miki dariya katuwa dake kina kuka haka, ai auren kenan Hawwa kiyakuri kinji zamu dinga zuwa dubaki, I’m sure kafin Ammin ki takoma zaria itama zatazo dubaki so daina kuka” kasa daina kukan tayi tace “to su Hafsah su zauna zuwa anjima kadan dan Allah Umma” dariya Umma tarike tace “mazajen su na jiransu Baba yace babu wacce zata kwanamai agida yau su tafi koma ciki kinji” Allah baku zaman lpy Umma taja kofan Hawwa tafashe da kuka tana kallonsu haka suka jamata hadadden security door nata suka wuce suka tafi tawuce ta wajen window tana kallon yanda suka shishiga mota tafashe da kuka sosai kafin ta tashi tayi stairs tawuce sama kawai tashiga dakinta tasa key a kofanta ta kwanta akan gado tana kuka sosai sai share hawaye take
She’s so sad shikenan tabar gidan Baba this is now her house where zata dinga zama as matan Khaleel wanda hala ko one month bazatayiba, da kyar ta tashi tashiga bayi ta dauro alwala tafito tahau kan dadduma tai salla ta tashi
Tasake kwanciya abinta tana kallon saman dakin tana wajen akai İshak ta tashi tayi sannan tasake kwanciya tana azkar da hannunta tana kallon sama still komi baya mata dadi, tana ahaka taji an bude kofan falo haderai tayi chan taji anyi knocking kofan dakinta. “Hello Ma’am this is PA Momy, your mother Inlaw sent me to call you” dan yunkurawa Hawwa tayi ta tashi zaune bamatasan mezatace ba tace “okay” tashi tayi tawuce another daki dake dakin wanda yake walk in closet tadauki gyalen da Hafsa ta ciromata na kayan jikinta maroon tayafa ta kallo madubi dudda babu makeup kan fuskanta amman tayi kyau, kana ganinta kaga amarya ga lalle ja a palm, baki abaya hakama kafafunta sunsha lalle tayi kyau ga kamshi gashinta a kwance but a gyare an mata parking nashi fitowa tayi tabude kofan taga PA tsaye da uniform nata takalli kafafun PA dake sanye da boot kawai taji wani iri amman tayi shiru, anan wajen kofa a falo tasaka flops datagani white awajen tafito suka fita.
Dadan tafiya daga Side nasu zuwa na Mom haka suka wuce bude kofa akayi suka shiga babu kowa a falo hanyan spa PA tayi da ita Hawwa tana mamakin setting na ginin gidansu da zata iya bata aciki sukai wajen dataga an rubuta spa bude mata kofa PA tayi tana kallonta Hawwa ta shiga ahankali PA tabiyo bayanta ta maida kofa tarufe Mommy na zaune kan kujera mai kyau ana matsa mata kafa gawani katon swimming pool but kaman madara ne ko menene aciki oho but dai fari da roses ga wasu mata about 8 duk da uniform some of them ma oyinbo ne duk suna kallon Hawwa, adan hankali cikeda jin nauyi da dan kunya Hawwa tace “ga……gani Mom” PA Mom ta kalla hakan yasa PA tace “munada sharudda some rules and regulations agidan nan wanda ake karanta ma duk matan da Mr Khaleel zai aura” PA professionally take magana abinta tace “by now you know waye Khaleel shine the only hair na Mangal, measure responsibility naki as matarshi is to just please him in bed idan kikai haka u will get kome kikeso this house will

secure present and future naki” kallon PA Hawwa keyi wani iri, PA tace “we believe Mr Khaleel will want to share bed with you today so za’ayi prepping naki for him, za’a miki wanka awannan ruwan madaran cleopatra, za’abaki some aphrodisiac dazakisha sabida Mr Khaleel yadanji dadin mu’amala dake he doesn’t like dry ladies, sannan za’a shiryaki cikin wani perfect enticing kayan bacci that will suit his liking tonight” Hawwa always wants war nata da Khaleel to remain nasu but wat is all this da mutanen nan ke gaya mata? Are they tasting her patient, baci ranta yayi tana wani karajin tsanan Khaleel aranta duk yanda tayi tunanin suke sunfi haka cus wat is this? Mata dolls yadaukesu kome? PA ta nuna mata matayen 8 dake jiranta gaban pool din tace “please ana jiranki” tanuna mata matan takoma ta tsaya jikin kofa, kallon matan Hawwa tayi saikuma ta kalli PA da wayanda ke matsa mata kafa takalli PA again, total of mata 12 adakin, kasa rike zuciyanta Hawwa tayi tace “ni za’ama wanka? Agaban kowa anan?” PA professionally tace “Madam zatai accessing jikinki taga ko kinada tabo ko bakida shi Mr Khaleel baison mata masu tabo” azuciye Hawwa tace “damn you and damn the Mr Khaleel da baison masu tabo, ni Mr Khaleel dinne banso gabaki daya, I’m not interested in him or this marriage so save all this kuma other matansa not Hawwa” tazo gaban kofan tama PA wani kallo tace “get out of my way” chak PA ta tsaya babu ko alamun tashi atattare da ita tace “you can’t leave here ba’a miki wankan nan an shiryawa Mr Khaleel keba, ba akanki aka fara ba definitely ba akanki za’a dainaba” Allah yasani Hawwa batazo gidan nan dan tayi bala’i da kowaba but wlh indai ita sukace zasuma wanka yau she will bring the entire house down akwai bura’uba kutumelesi, duk Mommy na kallo batace uppan ba PA tace “Ma’am we don’t want to force you please cooperate!” Tayi maganan tana kiran sauran matan takwas kawai sukazo masuma Mom massage ma sukazo suka zagaye Hawwa, Hawwa duka tabisu da kallo saita dago kanta ya kalli Mom suka hada ido anatse Hawwa babu wani tsoro ko shakka tace “with all due respect Mom! I’m not here for this! I’m not interested in Ibrahim! This abubuwan kuma matan that are interested in him yakamata amawa, I don’t want to cause any trouble out of respect for you bawai dan I can’t trash this girls dake nan ba, Mommy kindly instruct them su tashi daga hanya nafita nakoma dakina bacci nakeji” kallonta Mom tayi yanda yarinyar keda courage da rashin tsoro ita take kallo tanama magana haka, lumshe idanu Momy tayi hankali kwance tace “and I know just how to deal with yara irinku” kawai aka bude wani kofa acikin wajen Hawwa taga wasu securities mata manya manya guda 6 sun shigo, faduwa gabanta yayi sosai kawai sukayo kanta Hawwa ta tsaya chak babban cikinsu na zuwa takai hannu zata kama gaban rigan Hawwa Hawwa ta dauketa da mari jikake tasssss! Security ta dafe kuncinta saikuma ta sauke hannu kaman ba ita aka maraba Hannu Hawwa takara dagawa zata mareta kawia sauran suka rirriketa rai abace tace “ku sakeni! Let me go, ku sakeni nace leave me” zip head spa din kawia tajama Hawwah tana zare gyalenta ta

yar akasa, Hawwa tayi ihu tanaso ta kwance kanta takasa mata kusan 4 suka shiga kokarin bude mata riga Hawwa na kokawa dasu daidai sunja hannun rigan down nata suna barkawa har bra nata ana gani mai bala’in kyau red Hawwa kawai tafada cikin ruwan swimming pool din day is not deep daidai aka bugo kofan dakin aka shigo Khaleel ne yana huci.

TWO EPISODES FROM NA GOBE

EPISODE 7️⃣7️⃣

Khaleel na sanye dawani milk yadi mai taushe anmai milk dinki irin ango sak dinnan ransa abace, tundaga kan Mom yakalla zuwa kan matan dake wajen swimming pool din ga gyalen Hawwa red akasa, ga Hawwa cikin ruwan tana kokarin jan riganta dasuka barka tana ana kare gaban bra nata dake showing, wani irin kumfa zuciyan Khaleel yafara yakalli securities din strictly yace “did you touch my wife?! Matana kuka taba!?” Yayi Ihun da saida ita kanta Mom saida ta daura hannu a kunnenta tace “Khalee…….” “Shut the fuck up Mom!” Khaleel Yama Momy ihu kaman wanda yazare yace “I willl come back to you” yasake kallon securities din da jikinsu ke kyarma sosai danshi baya wasa da ma’aikatan su so ana tsoranshi sosai cus yafi kowa power agidan nan he rule Baban shi da Mamanshi yace “Matata kuka tattaba? Kuka yagama kaya”? Jikinsu nadan rawa sukace Madam tace “ayi stripping nata amata wanka ashiryata akai maka” kanta Khaleel yayi wacce tai maganan kaman zai rufeta da duka yace “duk duniyan nan babu mace ko namiji that have any right over jikin matata banda ni! How dare you guys, dukanku kafin nayi counting 3 ku kwashe kayanku kubar this house har abada you are fired, don’t ever step in to my house again” yayi maganan yawuce da sauri yadauki sabon towel yayi wajen pool din yaduka yana kallon Hawwa da ta tsorata iya tsorata dan batasan such kind of life exit ba kaman a film wai ama yarinya wanka akaita wajen wani, idanunta sunyi ja but batai kuka ba ya warware towel din yakai hannunshi da sauri yajawota ta taho yadaura towel din ta gaban kirjinta ariketa yafito da ita tana tattaka matattakala yazo ta bayanta yajamata zip sama sannan ya warware towel din yarufa mata daga baya yakama hannayenta yana dubawa yanda duk sunyi ja alamun an rike mutum kawai yasaki hannun yawuce inda mom take tray kayan massage dake kusada ita dana pedicure da ake mata Khaleel yasa hannu yawani kabar kararrarra!!!!Abubuwan sukai kara akasa Hawwa ta kalleshi dasauri tana tsaye ganin abinda yakema Mamanshi, Khaleel ranshi yabaci yace “Mom who do you think you are kisa adauko min mata daga side nawa

akawota nan ki sa mata su tabamin ita kafin ni nama tabata?” Mom na kallon kwayan idanunshi ganin yanda ranshi yake abace tace “this is the tradition, this is what we’ve always done to duka matayen ka, bayau aka faraba nothing new Khaleel just tradition”amugun zuciya Khaleel yace “fuck the tradition and fuck you Mommy!” Bura’uba Hawwa ji tayi kirjinta ya buga kunnenta yamata wani dummmm jin yanda Khaleel ya zagi Mamanshi, No she can’t stand anan, wani irin tarbiya mutanen nan suka bama dansu? Yau kota haukace bazata taba iya zagin Baba ba kai ko Umma ma datake ba mahaifiyarta ba, dasauri tai wajen kofa zata fita PA Mom ta tare Hawwa ta tsaya turus tana kallonta, Khaleel yace “idan kin sabama those creatures dakike auromini an gayamiki matana is part of them ne haaa?” Yanuna Hawwa da hannu yace “nina nemo matana dakaina, nine aurota who gave you right na adding nata in to your stupid old age tradition Mommy? Ban yarda wata taga jikin matana ba! Hawwa was completely created and brought into this world for me! Mommy me! Me alone not you, not your dead Ass brain big for nothing workers kinji!” Daidai lokacin aka bude kofa aka shigo Excellency ne da Musbahu da Mahe shigowan su gidan kenan ko lura da Hawwa basu yiba yayi wajen Khaleel dasauri harda dan gudunshi yakama Khaleel yace “Leely? Khaleel look at me daina kallon Maman ka what happen?” Khaleel na kallon Mom dake kallonshi kaman zai kasheta yace “ask your wife Pops” yana rike da yaron gam yakalli Mom yace “me kikama Khaleel Madam ranshi yabaci haka? I told you to avoid batama yaron nan rai ko? Me kikamai tundaga compound nake jiyo voice nashi wat did you do?” Dan ijiyan zuciya Mommy ta sauke she’s extremely hurt har muryanta baya fita da kyau ma kawai bataso tasaki kuka cus Hawwa na wajen ne bazataso taga weakness nata ba, ahankali tace “zagina yake tayi sabida nasa akawo matarsa zamu mata wanka mukaimai ita dakinshi”cikin mugun masifa Excellency wanda yamafi na Khaleel yace “ba dole ya zageki ba!” Dasauri Hawwa ta kalli Excellency itama, yace “yau yarona zai tare yahuta who asked for your opinion Khaleely yacemiki yanaso kuma matanshi wanka ne? Maisa kin cika shishigi allow children to do as they please suyi enjoying rayuwansu mana haba ke wace irin fitinanniya ne eh Madam?” Dasauri Mahe yace “it’s okay brother” shima yakama Khaleel dake huci sosai yana kallon Mom ranshi abace yace “ya isa Son it’s okay calm down please dau matarka ku koma flat naku dan Allah” fizge hannunshi yayi daga na Mahe dakuma Babanshi kaman dasu yake fada yawuce zaiyi wajen Hawwa Mom bakinta yashiga rawa sosai tace “Alhaji ni Khaleel ke zaga yana ciwa mutunci sabida that old girl datai kwantai aduniya shiyazo ya taimaka ya aureta!” Chak Khaleel ya tsaya sai hannunshi suka fara rawa garrrrr ba kakkautawa, Hawwa na kallonshi, Mommy tace “idan ana kirga matayen dana aurama Khaleely she’s the worst in terms of beauty, body, brain gata tsohuwa tukunna ma ba mashinshini” juyawa Khaleel zaiyi dawani irin sauri Hawwa tai yunkurin rikeshi amman ina yayi kan Momy kaman zai daki Mom fa Excellency da

Mahe suka tare Khaleel but so yake ya fizge yayi kanta, yayi wani ihu yace “Daddy I will kill Mom, I will kill her I hate her! She’s abusing matana” Momy tace “ku sake shi zoka kasheni sabida na zagi matarka, ku sakeshi kasheni Khaleel” cikeda masifa Excellency yace “wai bazaki shiru ba Zeenatu you will see the other side of me fa” rai abace idanunshi sunyi jajir Khaleel yace “Pops I’m living this house!” Faduwa daga gaban Mom har Excelelncy yayi, bakin Excellency har rawa yake yace “kabar gidan nan kaje ina? Ta ina zamu iya rayuwa bama ganin ka atare damu? Dan da Allah yabamu agabanmu kabar gidana when you know nace maka I want to live taredakai forever” Khaleel na fushi sosai yace “I am taking my wife and my daughter mubar gidan nan bazan taba barin matana a inda za’a dinga insulting nata ba, I didn’t marry Hawwa to get insulted by Mom, idan Hawwa is 100yrs I love her! I fucking love my wife Pops! Nobody can abuse wat I love na hakura! I love love and love Hawwa Pops” Kallon Khaleel Hawwa take sosai zuciyanta na bugawa in every word na love da Khaleel ke fadi akanta, Ihu Khaleel yayi
Yace “I love Hawwa! Pops inason Matana regardless of koma mecece ita, I…I……,” sai jikinshi yafara rawa da sauri Mom ta sauka daga kujeran tace “Khaleely” takai hannu zata tabashi yadaga hannunshi dasauri zai kabar da hannunta kawai ya suma ajikin Excellency Babanshi, Hawwa karan kanta dudda ta tsani Khaleel but saida ta tsorata ganin kalan suman da Khaleel yayi ta tako tazo wajen da sauri, Excellency ya rude yace “Mahe c….a……ll his his docto…….. Innalillahi Ya Allah! ya Allah!” Dasauri Mahe yashiga ciro wayanshi Excellency yarikeshi gam gam yana kallon Mommy data fashe da kuka yace “are you happy yanzu? Kika kasheshi ai sai ki huta, kin manta yanda right from age 8 zuwa age 13 Khaleel was hospitalized battling for his life, kin manta sabida kinga he is happy and living life” girgixamai kai Mom tayi tace “I’m sorry, I’m sorry Innalillahi Khaleel kayakuri kaji, wlh ina sonka sama da rayuwana gabaki daya” duk suna wajen saiga Dr yashigo aka sashi awani bed aka fita dashi asandare, Excellency yakalli Hawwa da hankalinta yatashi from her eyes yace “koma flat naki ki zauna ki huta in sha Allah babu abinda zai sameshi, Khaleel was once a cancer patient but he has been cancer free tun at the age of 13/14 bansan meya sameshi ba nima ba, but lokacin da suma suma sumewa irin wanda yayin nan yanzu yafara ciwon har akai diagnosing nashi da cancer, no no nooo” Pops ya girgiza kai yace “Cancer Khaleel bai dawoba in sha Allah, nasan babu abinda zai samu yarona koma dakinku kinji babu abinda ko wanda zai kara damunki” gyadamai kai Hawwa tayi ahankali tajuya tawuce.

EPISODE 7️⃣8️⃣

Tafito tana ganin ana wucewa da Khaleel clinic na gidan tawuce side nata ahankali tabude kofa ta shiga tawuce sama dakinta kasama chanza kayan tayi daya jike saitaji gabaki daya ta damu she's not happy at all, so Khaleel yayi ciwo tun yana 8yrs old he had cancer har zuwa age 14? Could this be the reason iyayen suka batashi haka? Suka kasa bashi tarbiya? İs that the reason suke sonshi haka na fitina? İs that the reason sukeda asibiti agidansu sabida ciwon Khaleel? Could this be the reason Khaleel yazama likita? Is that the reason Mamanshi ke everything to make him happy bataso abatamai rai saidai afaran ta mai rai? Wani kalan cancer yakeda shi? Babanshi yace lokacin yafara ciwon da yawan suma is the cancer back yanzu wannan daya sume yana cikin magana? Nooooo tafadi da sauri, She knows batason Khaleel ko kadan but she felt so bad dataji yayi rashin lafiya, from age 8 to 13/14 that's long time, sai kawai tadinga addu'a Allah yasa ba ciwon ne yadawo ba, tadamu sosai iya damuwa sai kawai ta tashi tafada bayi tacire kayan tayi wanka tafito tasaka wasu kaya tasa na bacc tasakai hijabi tafara salloli wlh kawai tadingama Khaleel addu'a, har zuwa 3 Hawwa bata runtsa ba, addu'a takemai har akai sallan asuba tayi itama sai ta sauko falo tazo jikin window tabude tana kallon tsakar gidan babu kowa banda securities nasu da bindigogi saita zauna akan kujera tai shiruuu chan takara tashi ta leka tsakar gidan but shiru haka tasake komawa ta zauna around 6 ta tashi tasake lekawa ta window
Khaleel ta hango yana tahowa side din sanye da kayan jiya ga kanula a hannunsa, dagudun gaske Hawwa tasaki labulen tayi kofa tabude da sauri tana kallon Khaleel chak Khaleel ya tsaya ganin Hawwa tabude kofa tana kallonshi damuwa sosai akan idanunta, wlh kallo daya yamata yasan babu one single sleep a idanunta, sai kallonshi take cikeda damuwa amman ta tsaya chak bata cemai komiba kuma batazo ba shikuma wlh she must show him care, da gangan yawani kama kanshi yace "ashhhhhhhh" sai kawai yayi baya kaman zai fadi dawani irin sauri Hawwa ta taho wajen ko silipas babu akafanshi tawani tareshi cikin murya mai bala'in dadi cikeda kulawa tace "Khaleeel" saukar da kanshi Khaleel yayi awuyanta ahankali yace "jiri take me inside" dasauri tashiga tafiya dashi hannunshi yakai yarike waist nata gam itama tarikeshi da kyau suka wuce ciki daidai su Mom da Excellency nafitowa daga clinic Excellency yace "look at wacce kika tsana! Look at them, jibi yanda ta fito ta tari danki jibi yanda yayi kaman ba shine yafito da kafansa ba".

Daki Hawwa tashiga dashi akan dogon kujera ta zaunar dashi ya zauna taje ta rufo musu kofa tazo wajen sai kawai yaga Hawwa tayi kneeling agabanshi tana kallonshi cikeda damuwa tace "me zakaci na dafa maka? Are you hungry"? Wani dadi ne yakashe Khaleel, kaman mai shirin suma yace "I want to drink kunu and kosai! But I

wanna brush nai wanka da salla can you help me to my room”? Dasauri tace “yes” tashi tayi ta dagashi yatashi ahankali zatai stairs dashi yace “I can’t muje lift” lift din taje dashi suka shiga tana rike da shi sai kallon fuskanta yake sukakai sama tashiga kallon dakunan batasan wannene nashi ba wani room yamata pointing hakan yasa tayi wajen dashi tabude kofan suka shiga dakin yahadu zaunar dashi tayi abakin gado tace “bari nasakaka toothpaste a brush” bathroom nashi ta shiga yabita da kallo da gangan yashiga cire kaya harda wando yabar boxer kadai toothpaste tasamai tafito daga bayin ganinshi zaune ba kaya ga kayanshi akasa saida gabanta yafadi tadai daure bata wani kalleshi ba tace “muje” hannunshi takama yataso ahankali sukai bathroom din tace “zaka iya wanka a tsaye?” Ahankali yace “cikamin bathtub bazanyi a shower ba I can’t stand for too long” gyadamai kai tayi tawuce wajen bathtub shikuma yashigayin brush yana kallonta ta mirror cika ruwan tayı tana sa hannunta karyamai zafi da yawa takalli abubuwan wanka tasa komi yafara kunfa da kamshi tadawo daidai yana rinsing bakinshi da mouthwash ta tsaya gefenshi tana kallon fuskanshi tace “kagama”? Gyadamata kai yayi ahankali hannunta takai takamashi wani yirrrr Khaleel yaji sabida hannun da lema leman ruwa but yadaure bai nunamata ba suna kaiwa wajen bathtub din ba kunya yawani sauke boxer nashi kasa da mugun sauri Hawwa ta juya but still tana rike dashi, cire boxer yayi tass ya wurgan da boxer akasa sannan yashiga ruwan yace “you can turn around” Juyowa tayi tadan kalleshi shima shegen kallonta yake tace “bari nafito maka da kaya kagama call me” gyadamata kai yayi tajuya tafita yabita da kallo tana fita yawaniyi dancing cikin ruwan yana fancakali da kumfa yace “yesssss!”

Walk in closet nashi Hawwa ta shiga tabi ko’ina da kallo kaman wani shugaban kasa tama tasa mezata ciromai sannin zaiyi salla yasa tadauko jallabiya da boxer da cream da turare guda daya ta ijiye agadon takıma tadauko short dawata yar t-shirt ta ijiye ta shimfida dadduma tadauki kayan daya zubar dasu anan kasa taga wani laundry basket a closet nashi taje tasa daidai tafito taji muryanshi kasa kasa yace “Moon” dan dakatawa Hawwa tayi takalli kofan bayin murya chan ciki yace “Moon, Wife” baki tabude kaman zata amsa saita tuna batai accepting nashi as miji ba ahankali tabude kofan bayin a tsaye taganshi tsirara cikin bathtub din dasauri tajuya tace “subhanallahi” murmushi yamata yace “give me towel from the hanger” dasauri takalli hanger wajen kofa tana mamakin yanda baya kunyanta tadauki sabon white towel dake wajen ta warware takare fuskanta tana tahowa, dariya kaman zai kashe Khaleel but yarike dariyan har gaban shi tazo tabashi ta juyamai baya dasauri, daura towel din yayi a waist jinshi Hawwa tayi abayanta dasauri tajuyo sai kawai ya rungumeta tsam tsam batare dayayi magana ba duk ruwan jikinshi ya manne mata a hijabi zuwa cikin jikinta wani yammm taji tama kasa magana saikuma adan hankali ataushashe cikeda kulawa da damuwa tace “meke maka ciwo yanzu?” Khaleel jiyayi kaman ya kurma ihun dadi

ganin yanda Hawwa tadamu dashi, abin nema yasamu yawani kashe murya kaman wanda zai mutu yanzu yanzu yace “ko’ina kemin ciwoooo” yayi maganan ashageabe, gently Hawwa tadaura hannayenta abayanshi tai patting ahankali Hawwa tace “sorry ko” gyadamata kai yayi murya kadan like a baby, calmly tace “muje kasa kaya kai salla” gyadamata kai yayi yadago daga jikinta tarikeshi suka wuce daki zaunar dashi tayi kan gadon tanabin yanda gashin kansa ke fitar da ruwa saita juya takoma bayi karamin towel tadauko tazo gabanshi tadanyi jimmm tana kallonshi kaman mai lissafi but ganin baida karfi and baida lpy sosai kawai saita daura towel din a kanshi tana sharemai gently sabida kar kanshi yayi ciwo, Khaleel yadago kanshi yana kallonta kin kallonshi tayi ta goggogemai fuska da bayan wuya sai kawai ta tsugunna agaban gado dudda gabanta na faduwa ta daure towel din zuwa kirjinshi ta goge ruwan, sannan tama hannu da kafafu zuwa knee ta ijiye towel din a gefe, tadauki cream nashi tana budewa mamaki yagama kashe Khaleel da ace an gayamai Hawwa zata iya kula dashi haka he can swear karyane bazata iyaba, so Hawwa is tHis caring,
zuba man tayi a hannu ta malka tadan kalleshi bakinta har rawa yake tace “uhnnn na….na shafamaka?”
Gyadamata kai yayi yadan lumshe ido sabida ta shafamai comfortable, shafamai tayi a fuska gemunshi taushi sosai kaman tana shirya yaro, rawa hannunta yafara dazata shafamai a kirji but ta daure ta shafamai gaban Khaleel yafara tashi sabida hannunta dake shafamai jiki that is very soft amman ya harde kafa da sauri, a hannu ta shafamai zuwa kafa saitadauki jallabiyan ta samai aka tace “bani hannunka” bata yayi tasakamai, boxer ta kalla sai kawai tadauki turare ta fesamai takwashi kayan shafan tace “ka karasa ina zuwa” tawuce closet nashi tamaida abubuwa tana fitowa taga yasa boxer ya yarda towel din akasa, daukan towel din tayi takai bayi tafito tace “tashi kai salla” tashi yayi ganin haka tafice daga dakin tawuce dakinta wayanta ta dauka tafito tana sauka kasa tai dialing number Ammi ta shiga kitchen ringing daya Ammi ta dauka tace “oyoyo Amaryana” adan kunyace tace “ina kwana Ammi na” Ammi tace “kun tashi lpy ya mai gidan naki” murya Chan kasa tace “fine” sai cha tace “Ammi inada gero ahhhmm” ta idan shiru tace “wai kunu zaisha” murmushi Ammi tayi tace “da kyau yar albarka haka nakeso ki dinga dafa abincin mijinki da kanki eh akwai gero Daddo duk ta kawo miki kayan hatsi harda alkama Umma ina kukasa kayan hatsi Hawwa na neman gero” daga wajen Hawwa taji Umma na cewa ta duba store duk suna wajen, Ammi tace “ance kiduba store” gyadama Ammi kai tayi tashiga store nata wlh Baba da kowa ma sunyi kokari buhu buhu tagani haka tashiga budewa tana mamaki ina zatakai all this abubuwa taga gero ta debo da wake shima tafito ta jika tana neman blender nan taga bucymix.

EPISODE 7️⃣9️⃣

Buchymix ta sauko dashi da food processor, tabude freezer taga anyi stuffing da kayan cefane taga nama dasu kaza daban daban frozen, tawuce store again luckily taga su attarugu an jera mata awasu basket na yan gayu dasu onions ta debo tashiga hada girki ta tasa ruwa a electric tashiga buga kosai data nika.

Cikin 1hour Hawwa tamai kunu da kosai tahada komi a tray tawuce sama, bude kofan dakinshi tayi bacci yake a wahale but jin an bude kofa bude idanu yayi ahankali yatashi yazauna ahankali, ijiye komi Hawwa tayi akan carpet na kasan dakin tadan taho takama hannunshi calmly tace “sauko” saukowa yayi ta zubamai kunun, dasauri ya dauka yakai bakinshi ya kurba sai kawai yamata murmushi yace “it taste good” dan murmushi kadan tayi tabudemai kulan kosai kafin ta shiga zubamai haryakai hannu ya dauki daya yace “wowww kosai how did you do it this fast” yakai baki yace “ohhh my God it’s delicious I’ve never had sweet one like this” samai komi Hawwa tayi sannan ta mike dasauri yakalleta yace “let’s have breakfast” ahankali tace “wanka zanyi ka dinga ci I’m coming” gyadamata kai yayi baiso yasa tazama uncomfortable wannan da yau Allah yadaurashi akanta tawuce tafita bayi tafada tai wanka tafito kofa taje ta murza key sannan tashiga closet, wani simple material tasaka mai shegen taushe da tsantsi white and gold gown yamata kyau sosai, gyara gashinta tayi yayi kyau sosai tasamai ribbon white sannan ta feffesa turare tasa kwalli a idanu tana kallon lallin hannunta da kaman yanzu ne ma yake mata kyau, tabi gown din da kallo ya karbeta kwarai yafito da hips dinta da boobs nata da kyau, dan eyeliner tasa saman isadu daya kara maida fuskanta yayi kyau kaman ba Hawwa ba taja baya tan kallon kanta overall gown din yamata kyau kaman wata model sannan tafito tazo gaban dakinshi
tabude ahankali, yana zaune yaci rabin kosankulan ya shanye kunun kaman ma ya kara dan duk ya zubar da kunun a tray dan bai iyaba bai saba sakama kansa abinci ba, binta da kallo yayi tamai kyau sosai amman yadaure yadauke kai baiso tafara tsoro da jin haushin shi ahankali yace “I don’t know how to put more kunu shine ya zube sorry” dan murmushi tayi kadan tace “it’s okay” zubama kanta tayi kawai yaga ta gyara zama tanasha agabanshi tadauki kosai tanaci sai kallonta yake kasa kasa duk bata luraba ta gama ta tashi ta kwashi kayan ahankali yace “take them to kitchen and come and help me to bed nai bacci” kai ta gyadamai tawuce tafita yabi ass nata da kallo kaman yayi spanking nasu ya dunkule hannu yamaida ya ijiye, wanke komi tayi ta wanke hannunta

tadawo sama gaban dakin tazo ta bude ahankali tashigo zaune taganshi gaban gado dagashi sai boxer tadauke kai ta taho tace “me kake bukata kuma”?a
Baba nama Ammi ihu data taresa cikin bacin rai yace “Mijinta zata sama bindiga akai sabida wani katon banza da wofi iyye hauka Hawwa zatayi ne? Akwai wanda yafi mijinki daraja da kima da iko awajenki ne?Bakison aure kinfi son zaman gida? Billahillazi yaron nan ya sakeki idan kin zauna a gidana Allah ya tsinan albarka saidai kije kiyi zaman kanki koki shiga duniya, shegiyan yarinyar mai zuciyan arna! Ni ku banni na mammake tambadaddiyar konaji dadi” Baba yayi kanta Hawwa tasaki Umma tahau gado taje chan karshe tana kuka cus Baba can injure her ayanda ranshi yabaci, sosai Umma da Ammi suka rike Baba dake nishi kaman zai mutu sabida bakin cikin Hawwa, muryanshi har rawa yake yana shaking irin na wayanda suka tsufa din nan yace “da aurenki ki bude baki kina cewa mijinki eh kinason wani sabida ke sokuwa ce, katuwar banza ko Miemie autan gidan nan bazatai kalan sokoncin nan ba, eh mijinki da babu abinda baya miki, kullum tsakaninki dashi saidai kice kin tsaneshi eh, Hawwa ni zaki tozarta ki ciwa mutunci? Ni zaki zubama toka a idanu? Sabida kinga yaro na sonki yana bibiyanki kaman wata sarauniyan mata shine kika sami waje kina shuka iskanci kinama yaro kaman kece uwarsa harda zagin iyayensa, kai wlh idan ban kashe yarinyarvnan ba bazanji dadi ba” Baba ya fizge hannunshi zaihau gadon Umma takama Baba dasauri tayi ihuuu sosai tace “Malam dan Allah, dan Allah kayakuri, Malam kayakuri ka zuciya dayawa, Malam idan tana dauke da juna biyu fa iyye? Baka daki Hawwa da ba sai yanzu? Dan Allah Dan Allah Malam kayakuri”kirjinshi Baba ya daka yace “kinsan me Hawwa tayi kuwa? Zan iya kara kallon yaron nan kuwa? Dan ubanta batasan kishi yake ba yasa yake dukan watsastsen makirin yaron nan Aliyu, idan tahanashi yaki hanuwa meya hanata kama mijin nata kaman yanda kika kamani yanzu eh? Miyahanata yin haka? Amman saidai kisamai bindiga aka kice zaki harbesa akan wani katon banza ke gaki yar sanda, to bari kiji na rantse da Allah dagayau baki ba aikin yar sandan! Kika kara zuwa wannan aikin ban yafemiki ba Hauwa’u! Abarma maza aikin, kaico! Nagama jin haushin Ni’ima yau da raina Allah ya nunamin tawa diyar zata iya abinda yafi na Ni’ima ban kunya tir da hali irin naki, Hawwa yau naji takaicin da kika kasance diyata!” Ya fizge jikinshi daga Umma yajuya yafita kai Baba ya zuciya bakadan ba, Hawwa ta taho wajen Ammi tana kuka sosai ganin Baba yafita tace “Ammi dan Allah kuyakuri wlh na rantse bazan kara abinda nayib……” hannu Ammi

tasa takaimata mari bataso tacigaba da marinta hakan yasa takalli Umma tace “bani dorina!” Umma zatai magana Ammi tace “bani dorina nace Umma banson wani magana” Ammi takalli Hawwa dake wani kalan kukan ban tausayi tace “zamanin mu duk girman mu iyayenmu na cin kaniyan mu idan munyi kuskure ko bayan mun haifi yara goma, ban bari Babanki yadakeki ba sabida namiji ne shi karfe yadaga but that doesn’t mean ni bazan hukuntaki ba, Hawwa magana da wa’azi basa aiki akanki ko? You feel kaman kin girma you are out of reach ko? Zakici gidanku” daidai Umma na shigowa rike dawata yar karaman dorina karama
Hawwa tazabura zata gudu Ammi tawani riketa duk karfin Hawwa takasa guduwa, hannayenta biyu Ammi takama tahada ta zubamusu dorina tace “hannayen nan dakike dukan mijinki dasu kina dauramai bindiga aka duk randa kika sake attempting yi wannan bulallan zaisa kituna mahaifiyarki ta taba hukuntaki akan haka” Ammi ta shauda mata guda biyu a hannun masu kyau Hawwa nawani irin kuka cus sun shigeta dorinar da zafi, Ammi ta saki hannunwan da gudu Hawwa tai baya zata gudu Ammi kawai tarike kafafunta gam ta hadesu Hawwa takai hannuwan takama hannun Ammi dake rike da dorinan tace “Ammi kiyakuri, baki taba dukana ba ko Baba bai taba dukana ba dan Allah kiyakuri, wlh zafi Ammi dan Allah” fizge hannunta tayi Ammi ta zubamata bulala biyu akafafu tace “this is for saka kafafun nan a hanya kifice daga gidanki batare da izinin mijinki ba next time idan zakiyi haka remember this” Ammi tasaki kafan kawai Hawwa taga Ammi tarike fuskanta dasauri takulle bakinta cus tasan next thing is her mouth, Ammi tace “ai baki isa release bakin dayafi iya rashin kunya da zage zage da maganganu marasa dadi, saki bakin nan!” sakin bakin Hawwa tayi ta tsorata da Ammi sosai, Ammi babu tausayi ko wani abu ta kaima bakinta duka mai kyau da lafiya saiga jini a lips nata cus sun datse da hakoranta Ammi tace “good jinin dama nakeso ya zuba, stupid girl mara tarbiya mai bama iyayenta kunya, mai zagi da dukan mijinta” Ammi ta yarda dorinan akasa tajuya tafita daga dakin itama fuuuu Umma tawuce wajen Hawwa data rungumeta sosai tana kuka tana bata hakuri tana mata kuma fada.
Azaure Ammi taga Baba yazauna flat akan simenti ya yarda sandanshi a gefe yabuga tagumi idanunshi sunyi jaaa gwanin ban tausayi ahankali Ammi ta zauna kan kujeran wajen tace “kayakuri Malam na zaneta yanzun nan kafin nazo nan nahukun tata, dan Allah kayakuri yanzu yaza’ayi bazamu barta anan ba, muka barta mun nuna munyi supporting bad dabi’unta ne hakan ba halinta dattaku bane” Muryan Baba yayi rauni yace “Zainabu kunyan Ibrahima nakeyi Zainabu kinsan yanda yaron nan ke sona kuwa”? Baba yayi shiru saikuma ya matse hawaye yace “na gayamiki ai yakawomin takardun babban gida ya sayamin nakoma ciki nacemai a’a bazan taba barin gidan nan nawa ba har abada, Zainabu na gayamiki yakawomin katuwar mota da driver dazai dunga kaini duk inda nakeso wlh naki amsa nagayamai badan kudinsa nake sonsa ba and sabida ya auri yarinyata basaiyamin abubuwa ba, namai

tatas naki amsa, na nunamai idan yacigaba yanamin irin abubuwan nan zan batarai dashi, Zainabu still yakara zuwan mini da maganan zai kaimu aikin Hajji dukanmu da yaranmu, daganan yanaso yawuce dani turkey amin aiki asamin kafan karfe nadinga tafiya da kaina batare dana amfani da karafunan nan ba, wannan ne kadai maganan Khaleel dana aminta na yarda ko jiya saida yagayamin zai aiko ranan asabar har gida azo amana passport nakira su Hafsa dasu Aminu da ke dasu Ramla duk suzo gida amana baimasan zakizo Abuja jiyan ba a asibiti yakemin magana" Baba yayi shiru yasake share hawaye yace "Zainabu kunyan Ibrahima nake yaron daya girmamani ya daukeni tamkar ubansa, yayi kuka ajikina yarikeni, Ibrahima baitabamin kallo kaman baban matarsa ba saidai mahaifinsa, Hawwa tarasa wanda zata ciwa mutunci sai shi, dakuma iyayensa, nima ai na takurawa yaran wasu nasama yaran unguwa ido saida Allah yasa y'ata taki auriwa nazo na gyara kuskurena, Point din is ai nima ba mutumin arziki bane, banda aiki sai zama kofar gida na sama yaran mutane idanu ina Kai karansu wajen iyayensu ni maisa wasu yaran basu zageni ba? Iyayyenka ko bokayene babu wanda ya isa ya zagan maka su, Zainabu Hawwa ta kama yaron mutane taita bugu iyye? Lahaula fi sha'atillah! Hasbunallahu wa ni'imal Wakeel! Zainabu takama yaron mutane tanata bugu tana sharara masa mari? Zan iya rantsuwa iyayensa basu taba marinsa ba wai kinga yanda mahaifin Ibrahima ke sonshi kuwa? Ina ganin ko ihu baitamaba yaron nan ba balle har akaiga mari amman Hawwa taita zubamasa mari takama yaro tana bugu tana jibgansa? Zainabu idan na cemiki ban tsani Hawwa ba nai karya nayi karya!" Ammi ta runtse idanu ahankali, yace "Wlh wlh da Aminu zai auro yarinyar dake hali sak irin wanda Hawwa na tayi wlh sainasa ya rabu da yarinyar nan, ba matan aure bace amman yau Hawwa! Hawwa na fa danake gani tafi duka yarana hankali take abubuwan nan sabida taga yaron sangartacce kaman baida wayau dukya haukace a sonta shine take haka kome?" Baba ya tambayi Ammi ranshi abace yace "uban me zaimasa ta tsaya tama kula Baban Yaseer Aliyu da aurenta? Ai bayan gaisuwa bai kamata tama tsaya sauraransa ba kwata kwata kamata yayi ta tada mota tabar wajen" Baba ya girgiza kai yace "Zainabu na rantse miki banjin inada karfin dazan iya kallon idanun Ibrahima ba ko kadan diyata tariga ta tozarta ni nan nan kafin ta yardan masa su hada shimfida saida mukasa baki eh wani kalan zuciya ke ga Hawwa"? Baba yace "kinga kucemata tafito tabarmin gida billahilazi ko ruwan gidana aka bata tasha sai nahau sama na fado kasa da mutum tazo tabar gidana idan zaki tafi da ita zaria ne chan muku amman nidai Hawwa bazata zauna gidana ba!" Dasauri Ammi tace "Malam nasan ranka yabaci amman dan Allah ka fahimceni, na farko dai bazan taba daukan Hawwa na tafi da ita zaria ba yoo ai nama daure mata gindi kenan! Kawai so nake ka kira Khaleel yanzu yasa abarmu mu shigo idan mun kaita abada hakuri asa tabashi hakuri tunda bai riga yasaketa ba" Baba yace "naje nabada hakuri gobe tasake marinsa? Gobe tasake bugunsa? Koko gobe tama

harbesa gabaki daya”?.
WLH DUK WACCE KO WANDA YAKARANTA MIN LITTAFIN NAN BATARE DAYA KO TA BIYABA BA BAN YAFEMATA BA HAR ABADA HAR ANADA!!!
07012181461 chat me up and pay is 3k Document
Telegram group inda zaki karanta complete is 1k

EPISODE 1️⃣1️⃣9️⃣

Dasauri Ammi trying to calm Baba that is extremely angry down tace “wlh bazata karaba, Malam Hawwa bata da hankali karmu mubiye mata, za’a mana dariya muka bari aurenta yamutu ko tadawo gida yan anguwa aka gane yaji tayi dariya za’a mana sosai” ahankali Ammi tace “koni inaso Ibrahim ya hukuntata amman dan Allah adakinta kaji Malam, dan Allah, yarinyar nan na son mijinta hauka ne ke damunta da sokonci but she will learn her lesson, kaima nasan bakaso aurenta ya mutu, kar zuciya yasa muyi dana sani, kafin ya aiko mata da takardan muje mu tare komi, da zafi zafi ake dukan bakin gatari mu ciccimata mutunci agabansa, kaji Malam” shiru Baba yayi yana kallon Ammi yabuga tagumi, Ammi tace “trust me bazata kara dukansa ba wlh namaka alkawarin nan tashiga taitayinta, Malam ko basu shiryaba yau yacimata mutunci adakinta, yamata kome zai mata, kawai dai karmubar Hawwa anan wannan shine halin iyaye na kwarai kaji dan Allah Malam nasan kana fushi” ijiyan zuciya Malam yasauke yace “toh!” Ahankali tace “kirasa saika samo mana wani cikin samarin anguwa dazai iya tuka motan Hawwa banjin zata iya tuki ba bari naje ciki” Ammi tawuce tashiga ciki, Malam yadade zaune sannan yaciro wayansa bala’in kunyan kiran Khaleel yake amman yadaure yayi dialing number harya katse ba’a daga ba, na biyuma haka ana uku wayan na gab da katsewa aka dauka Baba yaji muryan Khaleel chan ciki ciki yace “Baabaa!” Saikuma yaji muryan kaman mahaifiyar Khaleel tana mesa kake bashi wayan Salman? Kashemin d’a za’ayi, wani iri zuciyan Baba yayi, anatse Baba yace “Khaleel idan harna isa dakai kasa abarmu mu shigo gidanku gamunan zuwa da ni da Ammi da Hawwa kaji d’ana” shiruuu Khaleel yayi baiyi magana ba Baba yace “Ibrahima naaa” ahankali Khaleel yace “ohh kay” ya katse wayan tashi Baba yayi da kyar yana kakkabe jikinsa.
Tana shiga gidan Ammi taga Hawwa dake kuka sosai idanunta sun kumbura suntum tana mata fada wajenta tayi kawai Ammi ta dagata tace “tashi dan ubanki muje, Umma kema sako hijabi” Umam tace “waza’a barma gidan Zainabu? Kuje zan zauna”

ahankali Ammi tace “okay” tadauki key motan Hawwa taja Hawwa dake binta luuuu babu karfi ajikinta, suna fita sukaga Baba dawani matashi tsaye kallo daya yama Hawwa ya dauke kai Ammi tabama yaron key tace “an gode” tabude baya tasa Hawwa ciki da kyar itama ta shiga Baba yashiga gaba yaron yashiga aka jasu har gidansu Hawwa suna zuwa ko bincika motansu ba’ayiba aka barsu suka shiga cikin gidan har wajen parking ga PA na Mom tsaye sanye da suit da Musbahu yana sanye da manyan kaya bude mota yayi Baba yasauko suka shiga gaisawa da Musbahu Ammi ta sauko tajuyo takalli Hawwa tace “sauko” ahankali Hawwa ta sauko kanta akasa, Musbahu yace “this way please” akai flat na Mom dasu Mom suka gani cikin shiga na alfarma a tsaye tasanya wani Bubu lace, ga Excellency shima a zaune amman wlh kana ganin fuskanshi kasan babu farin ciki cikinsa babu Khaleel awajen kafin su zauna ma Mom tace “me kuka kawota? Me kuka dawo da ita? So kuke takarasa kashemini d’a tukunna?” Excellency dudda ranshi abace amman yace “Madam atleast ki barsu su zauna tukunna common” yakalli Baba da Ammi dake tsaye Hawwa abayansu a tsaye kanta akasa yace “Bismillan ku”
Zama Baba yayi bayan yabama Excellency hannu sun gaisa Ammi ma tazauna Hawwa ta zauna akasa takifa kanta akan kafafu Mom tace “yarona zaki sama bindiga akai sabida saurayinki? Waye ke Hawwa? Me kike takama dashi? Dukanki guda nawa kike? Me akayi aka yiki? I can make one call yanzu agabanki ayi dismissing naki as a police saidai kiga wasu na aikin not you, an kawoki gidan nan bamu taba cutar dake ba, ko kuntata miki, amman kina kokarin daukan rayuwan danmu, me kukazo yi? D’ana yace baya auren? Zai aiko mata da saki dazaran ya sami kanshi, akan wani dalili zata kara shigo mana gıda, mesa ma Khaleel zaice abarku ku shigo”? Daidai lokacin aka bude kofan falon Khaleel yashigo da kyar Salman na rikeshi ga hannunshi da kanula muryanshi babu karfi yace “don’t be rude to my parents please Mom” dago kanta ahankali Hawwa tayi tana kuka takalli Khaleel Allahu Akbar! Dasauri Baba yadago kanshi ganin Khaleel sai kawai yatashi da sauri yayi wajen yana kama Khaleel cikeda usulin so yace “Ibrahima meya sameka?” Kafin yayi magana Mom tace “yarka taso kaishi lahira” kallon Momy Khaleel yayi hakan yasa tai shiru, idanun Baba suka shiga kukkullewa kuka na neman kufcemai Khaleel yabashi tausayi hawayen zasu fito dasauri Khaleel yace “noo Baba nooo, I had headache aka samin drip” Mommy tace “bakin cikin yarku yasa ya sume Salman yakawoshi gida unconscious likitoci biyu sukai reviving nashi, menene abin so a wajen yar sandan nan? Yarinya na son halakaka wannan wani irin GARGADAN SO ne?” Cikin murya mai rauni Baba yace “Ibrahima banda bakin baka hakuri dakai da iyayenka, ka yakuri Ibrahima ka gafarci Hawwa namaka alkawari zata chanza hali give her second chance” Mom tace “nifa dana yagama auren yarku kome zakuyi!” Zeenatu! Excellency yakirata azafafe hakan yasa tayi shiruuuu tace “hmmm” kowa ya kalli Excellency, mikewa yayi ransa abace yace

“Hawwa” ba karamin bugawa gaban Hawwa yayi ba ta dago kanta idanunta sunyi jajur sun kumbura, babu wasa kan fuskan Excellency yace “come with me” yashiga tafiya ahankali Hawwa tafara kokarin tashi tsaye wlh takasa Khaleel takalla dayaki kallo inda take magana yake da Baba he looks very sick Ammi ta tayata tashi.
Mommy ta zuba mata harara tace “muguwa mara kirki, mai bakin hali” sauke kanta Hawwa tayi kasa fresh hawaye na zubomata Excellency yace “come with me” ahankali Hawwa tafara tafiya da kyar Baba dake magana da Khaleel but saida ya lura da yanda Khaleel yadan juya yabi Hawwa da kallo wlh saiyaji Khaleel yakara bashi tausayi, how can you love mata dake maka rashin mutunci haka? How? Kamashi yayi da kanshi yace “muje ka zauna”.
Har wajen study Excellency sukayi yabude kofan ya tsaya yana jiran Hawwa dake tafiya da kyar saida takaraso wajen ta tsaya strictly yace “shiga” wucewa tayi ta shige ciki Excellency ma yashigo tareda maida kofan yarufe yasaka key karma Mommy tazo takara bashi takaici, yawuce Hawwa yaje ya zauna kan chair dake officer din ga table agabansa, ahankali Hawwa ta shiga tsugunnawa gabanta fadi kawai yake Excellency yadan fuzar da iska fuuuuu sannan yace “Mrs Hawwa from the first ever day dana ganki I liked you, I sees you as a responsible girl mai hankali natsuwa and hikima, there’s nothing da Madam batace akanki game da auren nan ba naki sauraronta, yar sanda is stubborn, Khaleely can’t manage you, zakifi karfinsa menene menene duk naki yarda da ita but why did you prove her right? Why did you disappoint me Hawwa? Eh!” Excellency yadakama Hawwa tsawa dan ranshi abala’in bace yake his very angry da Hawwa, the only dayasa he’s even doing something sabida yaga how deep Khaleely ke son Hawwa, despite everything ya kasa sakinta, bazai iya bari aurensu yamutu ba something might happen to yaronshi, yanda Hawwa ke kuka Excellency ya kalla yace “I just have couple of questions for you karki kuskura kimin karya, when did you started seeing your ex? Har yanzu kina sonshi ne?” Girgizama Excellebcy kai Hawwa tayi da sauri tana shesheka tace “Abba wlh he was never my ex, mijin kawata ne bantaba sonshi ba bamu taba soyayya ba, ina cikin mota naji anyi knocking kawai na ganshi, same thing this morning naje KFC nafito zan shiga mota na ganshi, Abba I find out he has been stalking me tunda nayi aure wai yana street din nan yana wuni that’s how he even find out rannan nafita haryabini court, Abba wlh he is not my ex na rantse” Har kasan ranshi Excellency yaji ya yarda da abinda Hawwa tace, anatse yace “rannan da kikaje kika dauko Khaleel daga wajen party nan drunk I was inside this office ina kallonku Hawwa I felt proud of you then, nobody has ever done that for d’ana saike I was happy finally someone na Khaleely’s life dazata chanza shi” Excellency ya fuzar da iska sosai yana runtse idanu cus this part pains him the most yace “why would you maaka d’ana a kotu Hawwa? Meyayi zafi dazaki bar gıda kije kotu? D’ana yataba abusing naki ne? Is Khaleel

hitting you? Molesting you? Raping you? Starving you? Wani babban abu Khaleely yamiki dazaki dauki d'ana ki maka a kotu eh?" Excellency yadaga murya dayasa jikin Hawwa har kyarma yake bata tabajin ta tsani kanta irin yauba, Khaleel baitaba raping nata ba, baitaba dukanta ba, baitaba molesting ko abusing koma verbal abusing nata ba, bata tabajin yunwa agidansa ba da gaske ne maganan da Abba yayi meyayi zafi dahar zata shigar da danshi court? Wlh saita kasa magana kawai ta daura hannayenta akan fuska tana ma Excellency kuka, Excellency muryanshi ba dadi yace "Hawwa you put a gun to my Son's head kinsan shekara nawa muka nemi haihuwa bamu samu ba kafin nasami yaron nan dakike kokarin harbi?" Yayi shiru yace "I know Khaleel, wlh yarona is not a violence person, I know he loves you deep there's no way zai ganki da wani da bazaiyi reacting ba, I know fear of karyayi kissan kai yasa kikai reacting just the way you did but Hawwa did you have any idea wat message you sent to your husband with that one single action naki?" Excellency yace "Kin gayama Khaleel nan gaba if something should happens that will warrant you to take his life you will not hesitate zaki dauka!" Hawwa ta shiga girgiza kai takasa magana, Excellency yace "koni bazan iya zama da matan da others comes first for her ba before ni mijinta, in that situation you should look at how hurt my son is not how hurt that other man is, believe me at that moment ciwon da Khaleely na yakeji a zuciyanshi yafi ciwon dayake jima shi dan bura'uba yaron that caused all this wahala ajiki" Kai! Maganganun Excellency wani kalan shiga Hawwa suke for the first time she's seeing this from another perspective he's saying nothing but the truth, Abba is right, Excellency yayi shiru yana kallon Hawwa da he's very very angry with her but then tabashi tausayi dan adam ajizine, No body is above mistake shima dan nashi yayi kuskure, Ijiyan zuciya ya fuzar yace "I have last question for you as mahaifin Khaleel you need to tell me the truth trust me bazan taba yarda d'ana yayi keeping naki in this house against your will ba ko sonki zai kashesa, Hawwa bamu taba cutar da kowa ba wlh ask duka matayen nan, kowacce da iyayenta da yardanta zasuzo nan, suke turo hotunan su da kansu, babu wacce ta taba shigowa gidan nan forcefully, we don't ruin life of the girls we make it better! Auren aure ne da suma sunyi for one or two selfish interest nasu, check all matayen da yataba aure they're doing far better than before, wat i am saying is bamu wulakanta su sauran matan da ga kalan auransu ba bazamu taba wulakanta ki ba, idan bakison auren ko Khaleel zai mutu da sonki wlh saiya barki Hawwa ba'a dole arayuwan nan dan haka tell me this is between me and you KINASON D'ANA KO BAKISON KHALEELY NA?!".

EPISODE 1️⃣2️⃣0️⃣

Kallon Excellency Hawwa tayi Excellency yace “idan bakison Khaeely I personally zan karba miki saki a hannun Khaleely yarabu dake for ever it’s your fundamental human right ki zauna in a marraige da kikeso not wanda bakiso, tell me DO YOU AT ALL LOVE MY SON HAWWA KOKUMA YOU HATE HIM?” Shiruuu Hawwa tayi rayuwanta da Khaleel from beginning of haduwansu kawowa yau na flashing right before her eyes, babu wanda yataba making nata special like Khaleel! Like he always makes everything about her! He loves her kaman itane alkibilan rayuwanshi, dazu dayace su rabu was the darkest moment of her life, she felt this fear of loosing him forever! She felt this urge na she can’t even go a day without Khaleel arayuwanta! Right now she’s feeling Khaleel in her heart, her tissues! Her organs and blood, she’s feeling Khaleel in her mind and soul ahankali tace “Abba inason mijina!” Tayi shiruuuu chan tace “I am afraid of loosing him!” Hawaye suka gangaro daga idanunta tace “Abba I love Ibrahim Khaleel with everything in me! Abba wlh ina bala’in son mijina kaman zan mutu!” Excellency yayi shiru yana kallonta, ahankali tace “I know I messed up! Nayi kuskure da dama, I disappointed you, Baba na, Mahaifiyata and mijina ma!” Muryanta yafara rawa tace “Abba just give me second chance I will make everything right! I will show Khaleel he was never wrong to love me! I will show him I am the only girl made for him!” Dan murmushi kadan Excellency yayi saikuma ya gyara fuskanshi yace “okay I will give you second chance! Khaleel is extremely angry with you! All explanations din nan dakikamin find a way make him listen to you sabida you guys have lot of misunderstanding na each other, don’t worry bazan taba bari ya rabu da ke ba aurenku mutu karaba but don’t ever make this kind of mistake kinji” gyadamai kai Hawwa tayi ahankali tana share hawaye,
Excellency yace “all of this dake faruwa are just OBSTACLES OF LOVE! find a way and overcome it! Everything is going to be okay alright”? Gyadamai kai Hawwa tayi sai kawai Excellency yataso yadauki tissue yazagayo da kanshi yasa hannu yadago Hawwa ta mike da kyar yakai tissue kan fuskanta yana sharemata hawaye yana kallon lips dinta da akwai jini yace “meya sami lips dinki?” Girgixamai kai tayi tace “bakomi” dasauri yace “did your parent hit you?” Sunnar da kanta kasa Hawwa tayi, cikeda masifa Excellency yace “Ha’a why will they hit you eh? An gayamusu ana dukan yarana you are just a child you made mistake okay shi Khaleely ai he’s not entirely innocent, shima he provoked you banson abu hakafa, No banson ana tabamin yarinyana fa” Wayyooo Allah kai! Maganan yataba Hawwa kawai saitaji she’s regretting cema Khaleel datayi iyayenshi basu bashi tarbiya ba iyayen Khaleel are very nice wlh! Abinda mahaifinshi yamata today ko mahaifinta bai

mata shi ba, he gave her a listening ear, ya saurareta, corrected her and yagoge mata hawaye, kawai sai Hawwa ta zube tai kneeling agabanshi tafashe da kuka sosai tace “Abba dan Allah kayafe mini I was very wrong I’m sorry Abba I am so sorry Abba dan Allah” kallonta Abba yayi sai kawai yaduka yadagota wani kyakkyawan side hug yabama Hawwa yace “shuuu shiiiii shuuuuu! It’s okay, I forgive you no need to be this hard on yourself okay, ya isa kukan, you’re just a girl! Akwai wanda baya mistake ne, dena kuka don’t worry everyone will forgive you har Khaleel, ya isa hakanan okay” yakai tissue yana sharemata fuska Hawwa tai lamo a shoulder shi feeling that fatherly love daga wajenshi, Ahankali Excellency yace “it’s okay karki damu da duk wani abu da Madam zatace that one dama tacika masifa but she’s also a good person like me, and she’s not wicked trust me she will come around and she will love you also kinji, just work on giving me GrandBabies!” Dasauri Hawwa tasakeshi tajuya da fuska tana jawo gyalenta tana rufe fuskanta kunya kaman zata shige kasa Excellency ya kwashe da dariyan manya yace “I want 20kids if possible, ayi abani jika Hawwa uhmm sarkin kunya” Hawwa taboye kai sosai, Excellency yabude kofan office din yace “let’s go” fitowa sukayi tare kan Hawwa na kasa suka shigo falon Mommy na hararanta Khaleel na zaune akan kujera kusada Baba yadan jingina kanshi a hannun Baba yayi shiru idanunshi a lumshe Hawwa tazauna akasa gefen Ammi kanta akasa Excellency ya kalli Baba yace “Alhamdulillah Malam naji dadi da kuka dawo da Hawwa immediately, this shows Hawwa tafito daga gidan manya gıda masu tarbiya da sanin yakamata, idan mata da miji sun sami matsala ba’a nuna anyi supporting yarinya dawo da ita ake hakan da kukayı ya kara nunamin yess! Danmu ya auro matan data dace dashi” Baba yayi gyaran murya yace “Hawwa ta kunyatani ta kunyatamu abubuwan datayi sam ba tarbiyan damuka bata kenan ba, amman ta sanarma da mahaifiyarta tariga ta janye zancen kotun tun aranan da taje kotun, kuma wlh duk randa kika kara batama Ibrahima rai gidan nan zanzo na ciccimiki mutunci kinajina!” Kanta na kasa tace “eh” cikeda fada Baba yace “kuma na sanar da ita bata babu aikin nan sabida harda aikin ke kara mata taurinkai da ji kaman ta isa tasama kowa bindiga akai” Baba yajuya yakalli Khaleel yace “Ina neman alfarma kabarta tace offis dinsu takai takarsan barın aiki da uniform bata da bindigar kaji Ibrahima” gyadama Baba kai yayi ahankali idanunshi a lumshe Baba yajuya yakalli Mom dake kumbure kumbure Khaleel yahanata magana yace “Hajiya nasan Hawwa ta batamiki rai muma duk ta batamana, abinda zaki la’akari dashi shine babu mata da miji da basa fada amfaninmu iyaye kenan idan sukayi saimu hadasu tare mu sosollesu tass mu ci musu mutunci, nasan duk maganganun da kikayi sabida kinason danki ne amman ina mai tabbatar miki Hawwa zata kula da danki da kyau, ki bama Hawwa dama tabiyu Hajiya zakiga chanji bazata kara abinda tayiba ayakuri ayakuri”
Dudda yanda Mommy ke fushi she loves how Baba looked at her

yamata magana dudda ta cicci mutunci yarsu agabansu, sai kawai jikinta yayi sanyi ahankali Ammi tace “ayakuri amata afuwa tayi kuskure” shiru Mom tayi for the first time saitaji kunya kawai yakamata da itane wata taci mutunci danta haka wlh ko kallonta bazata karayiba ballema tamata magana but look at ya da suka bata hakuri sai kawai ta gyadama Baba kai tace “toh” dan batasan yanda zata amsasu ba
Baba yajuya yakalli Hawwa sai kawai yadan daga kan Khaleel dake kafadanshi yace “ina zuwa Ibrahaima” yatashi dagakan kujeran yawuce dayan kujeran dake gefen na Ammi ya zauna yace “je ki fara bawa mijinki hakuri yafi kowannenmu matsayi da mahaimmancin arayuwanki sannan ki bawa iyayensa hakuri dan hardasu kika ciwa mutunci tashi” Ahankali Hawwa tadan kalli Khaleel da yana dauke kanshi completely baya kallon inda take gently ta tashi kowa na kallonta adakin harda Mom tazo gaban Khakeel ahankali tana kallonshi yaki kallonta zuciyanta kawai taji yana breaking, gently ta duka sai kawai tasa guiwowinta akasa tai kneeling hakan ba karamin dadi yama yan dakinba barinma Mom now that is how to beg yaronta cus her Khaleely is a king!
Hannuwanta Hawwa tahade ahankali tana kallon Khaleel dayaki kallonta sai kawai bakinta yafara rawa sosai ahankali tace “Kh…… l….eel” Baba yace “au haka kike kiran mijin naki gatseee” girgizakai tayi dasauri tace “Husbyyyyyyy” ko moving jikin Khaleel baiyiba kaman ba shi ba, wayyoo kawai Hawwa tafashe da kuka tace “I am very very, I’m terribly sorry Husbyyyyy, I am super sorry! I’m genuinely sorry! I’m fully, wholeheartedly sorryyyyyyyyy”
Sai kawai takama kunnuwanta tana kallonshi tace “I will never ever hurt you again I promise kayakuri, forgive me kaji mijina!” Wlh kaman baisan abu na gabanshi ba sai kawai ya yunkuro ahankali yatashi tsaye dasauri Hawwa ta kalleshi ta gefenta yabi zai wuce azuciye Excellency strictly yace “Ibrahim” juyowa Khaleel yayi yakalleshi ahankali bai amsaba, Excellency yace “bakaji matarka na baka hakuri ba”? Yanuna Hawwa that is still kneeling, murya chan kasa ciki ciki Khaleel yace “uhm I heard her it’s okay!” Yafadi ba yabo ba fallasa hakan yama Baba dadi da Ammi dadi yes yaci uban Hawwa! She deserves it inba hakaba she will keep on taking him for granted, kawai yajuya zai wuce dawani kalan sauri Hawwa ta tashi ba zato ba tsammani kawai yaji Hawwa ta rungumeshi tabaya tsam tsam, gam gam tace “I LOVE YOUUUUUUUU!” Chak Khaleel ya tsaya komi nashi na tsayawa as well!
Kowa na falon murmushi yayi suka daddauke kai daga kallon yaran nasu, sheshekan kuka Hawwa takeyi like a baby, bawai kalan kukan datakeyi tun dazu ba this is a special cry just for mijinta kaman wata baby sosai kuma, cikin murya mai kashe zuciyan miji tace “Ibrahim I love you!” Manna fuskanta tayi abayanshi sosai har kamshin sa tayi missing yaushe rabon da tajita ajikinshi tace “Inasonka Ibrahim Khaleel!” Ahankali tasakeshi ta zagayo ta gabanshi tana kuka takai hannayenta tadaura kan kirjinshi ta

kalleshi hada ido sukayi duk wani affection data saba gani nata a kwayar idanun Khaleel yau bata gani ba Heart nata na shattering into pieces tace “I can’t loose you sabida I love you! I’m sorry about everything, I love you Khaleel!” Wani shegen kallon tsana yamata, yace “ok so?“ ya Allah!That’s one of the coldest reply someone has ever given to her in her entire life jikinta kaman ya daskare, yatsine fuska Khaleel yayi ya kabar da hannunta daga jikinshi bluntly yace “whatever Yawucewanshi yabarta wajen tsaye yabude kofa yafice, jiri jiri Hawwa taji tanaji da sauri ta duka awajen tace “na shiga uku!”.

EPISODE 1️⃣2️⃣1️⃣

Mom tai murmushin jin dadi ganin yanda yaronta yatafi, Baba da Ammi ma sunji dadin abinda Khaleel yayi Excellency ne cikeda so yace “it’s okay Hawwa na, he will come around, je flat naku kihuta I want to talk to your parents” gyadama Excellency kai tayi tamike tsaye ahankali tana tafiya da kyar tasa hannu tabude kofa tafito, da hankali da hankali take tafiya har zuwa side nata tabude kofa tana shiga tawuce carpet na tsakiyan falon kawai ta kwanta tana kuka mai radadi da soya zuciya.

Kallonsu Baba Excellency yayi yace “daga Khaleel har Hawwa duka yarane, duk mu bisu a sannu muna correcting nasu, shima Khaleel din bawai he’s innocent bane, duk matsalan shi ta haddasa wannan fadan, d’ana na shaye shaye” Excellency yafadi ahankali there no point aboye an zama daya yanzu, daga Baba har Ammi suka kalleshi dan basu dauka zai iya fadin kalan maganan ba, ahankali Excellency yace “duk laifi nane inason Khaleel da yawa da nakasa gyara kuskuren shi but namuku alkawari komi zai chanza daga yanzu zamu tsaya tsayin daka akanshi ya gyaru”Excellency yace “kuma dan Allah Malam da Hajiya kada ku kara tabamin yarinya kuka kara dokanmin diya shari’a zanyi daku sosai” dan murmushi both Ammi da Baba sukayi Ammi tace “diyar taka akwai taurin kai ne amman za’a kiyaye harda fushi” Excellency yace “ga abin doka Khaleel ba’a dakaba sai iya” Mom ta tashi kaman ba itaba anatse tace “ko ruwa ba’a baku ba” shi kanshi saida Excellency ya kalli Mom but harta wuce Excellency yakalli su Baba yace “kar maganganun da Zainab tayi yasa ku dauka Hawwa zata wahala ko zata takura mata bar Zainab da masifa amman batada mugunta, abu kadan Hawwa zata iyayi ta sace zuciyanta” Baba da Ammi sukai murmushi saiga Mommy tareda ma’aikata dasuka dauko hadaddun ubansun trays dake dauke da drinks da ruwa da kulolin abinci da su fruits duk aka ijiye a tsakar falon Excellency ya sauko

yace “bismaillah Malam” Mom ta kalli Ammi ahankali tace “ni banson bakunta fa” Ammi cikeda raha tace “kikazo gidana Allah sa kada kiyi” Mom ta sauko Ammi ma ta sauko suka shiga hira da Mom har tana tambayan Ammi garinta suna hira sosai kaman ba fada yaransu suka gamayi ba sai wajajen shabiyu sukace zasu tafi har waje su Excellencu suka rakosu Ammi tace “bari taga Hawwa” tawuce
Hawwa na kwance akasan Ammi tabude kofan dakin ta shigo tana kirne fuska Hawwa na ganinta ta tashi zaune da sauri tana goge fuskanta Ammi tayi kaman bataga tana kuka ba, tace “abu daya nazo gayamiki kije tiktok ko IG kiyi searching M Shakur ki shiga class dinta na Kissa training da Intimacy ki koyi yanda ake abubuwa, idan zaki zage damtse kiyi zaman aure kiyi Hawwa, ga mijinki nan yayi fushi dake, tun wuri kafin dare yamiki kisan yanda zakiyi ki lallaba ki shawo kansa ku shirya, ni natafi zaria bazan kara dawowa Abuja sabida kin tapka hauka ba kome kika shirya yi kiyi, duk abinda zakiyi ki tabbatar kinyi kin shawo kan Khaleel kafin ya tsaneki da gaske” Ammi tayi kofa daidai zata fita taji Hawwa ta kama mata hannu dasauri Ammi tajuyo sai kawai Hawwa ta rungumeta tama kasa magana kuka kawai take jikin Ammi, ga jikinta yayi zafi, Ammi na so ta karaya but ta tuna this is the same thing she did jiya ta tausaya mata tahakura amman da safiyan Allah tayi shirmen dayafi na jiya so taji ajikinta, cireta kawai tayi daga jikinta tajuya abinta tafice tarufo mata kofa Hawwa ta tafi wajen window taga su Ammi sun shiga wata mota daban da yaron daya kawosu sun tafi.

EPISODE 1️⃣2️⃣2️⃣

Komawa Hawwa tayi tasake zama sai kallon kofa take jira kawai take Khaleel yashigo ahaka wani wahalallen bacci yayi awon gaba da ita, tana cikin bacci taji motsi dayake batai nisa a baccin ba da gudu tabude idanunta Khaleel tagani awajen kofa yana fita dawasu manyan akwatinan shi na LV guda biyu, mugun faduwa gabanta yayi da gudu ta tashi kirjinta nawani irin bugawa tayi wajen kofan tace “Khal…..” mugun kallon daya mata yasa takasa karasa kiran sunansa kawai yaja kofan ya kulle yawuce abinshi, Hawwa tayi wajen window dagudu tadaga labule taga flat dinsu yashiga da akwatinan sai kawai taji kuka yazo mata saida taji ana salla ta iya barin wajen tawuce dakinta bayi ta shiga tayi alwala, tafito tazauna kan dadduma tayi salla ta kwanta akan dadduma tana wani kalan sauke ijiyan zuciya her heart is so heavy kaman an daura mata

manya manyan duwatsu, takasa cin abinci takasa bacci sai kuka har bayan sallan isha da kyar ta tashi tajawo wani first aid box taga PCM tadauka tasha ta mike ta tsaya tsaye wajen window ta tana kallo babu Khaleel a compound din, ina yaje? She's missing him, wayanta ta dauka ta zauna bakin gado tai dialing number shi saitaji ana cemata number shi bayama kan network gabaki daya ijiye wayan tayi ta tashi tafada bayi da kyar tai wanka tafito tasaka wani sexy rigan bacci ta feffesa turare sai kawai tawuce ta tafi dakinshi tabude ahankali everything smells like him, zama tayi abakin gadon ahankali tana kallon gadon tana tuna how happy Khaleel use to be, his full smile yana kallonta, his loving eyes, his erotic talks, his sleep, yanda yake kankameta, yanda yake bacci ajikinta, yanda yake tashi da kyar, the way yake amsawa ummm idan ta tadashi, the way he acts like a baby, the way he dances for her, the way yake tsokanan ta, the way he calls her Kulu, Yar Sanda, muguwa menene menene menene, bata taba sanin she loves all the moments ba sai yanzu, like she will give anything just to experience those moments one more time yanzu, hawaye masu dumi taji yana bin hancinta yana diddiga ta tip na nose nata yana sauka a hannunta dasauri ta share da bayan hannu kaman mai mura cikin wani irin murya na ban tausayi da nadama da dana sani tace "I am sorry Khaleel!" Sake goge hawayen tayi tace "I really am, I'm badly sorry Khaleel, I miss you, I missed everything about you, please come back to me kayakuri" tayi maganan tana kwanciya ta kifa kanta jikin pillow dinshi Hawaye na gangarowa daga idanunta tana kallon kofan tamika hannu tadauki pillow daya ta rungume a kirjinta tana kallon kofa har 2 nadare takasa bacci ta tashi taje ta dauro alwala tadauko hijabinta tadawo dakin tai salla har four sannan bacci ya iya kwasheta akan dadduman.

Ahankali take iya bude idanunta ganin gari yayi haske yasa ta kalli wayanta da sauri taga 7:45, Subhanallahi tafadi da sauri ta tashi tashiga bayinshi tadauro alawala tazo tai salla ta idar tai azkar ta karatu ta gyara dakin tass ta kunna turare tawuce bayinta tai wanka har yanzu idanunta a kumbure closet nata ta shiga tasaka wani atampa riga da skirt dakeda red ajiki batasa komi a fuska ba tafito tasauko kasa kitchen ta shiga tayi tea a cup tafito tazauna tana kallon tea din wlh takasa sha sai kawai ta tashi taje kitchen ta ijiye tasa marfi tarufe tafito takoma sama ta shiga closet red mayafi ta dauka babba tayafa tafito tasauko kasa, crocks dake nan kasan falon na Khaleel tasaka tabude kofa tafito tana tafiya ahankali tawuce side nasu Mom.
Gently tabude kofan da sallama a bakinta ta shiga ciki Momy ne kadai afalon ga plate na fruits tanaci cus yanaci fruits take faraci dasafe idan Excellency na gari tana breakfast da wuri but jiya da night yatafi France saisa take breakfast ita kadai ga ma'aikata a dinning na jera warmers, kallo daya Mom tama Hawwa ta dauke kai tacigaba da cin fruits abinta, dudda gaban Hawwa na fadi but har gaban Mom tazo ta duka ahankali tace "ina kwana Mom" dauke

kai Mom tayi kaman bada ita take magana ba chan tace “lafiya” shiru Hawwa tayi still tana gabanta chan tace “Mommy dan Allah kiyakuri kiyafemin kinji Mom” kallonta Mom tayi tamata wani banzan kallo tace “tashi agabana” ahankali Hawwa ta tashi, gently tawuce wajen dinning saikuma tawuce kitchen, 3workers ne ke aiki an riga an gama breakfast na Mom dasauri suka gaida Hawwa. “Good morning Ma” gyadamusu kai tayi ahankali Hawwa tace “me kuke dafawa” babban ma’aikaciyan tace “an gama breakfast na Madam, tace ama Mr Khaleel kunu da akara shine zan fara yanzu” Dasauri Hawwa tace “ki barshi zanyi” batama jira amsan su ba tace “ina wajen wake? Da gero”?

EPISODE 1️⃣2️⃣3️⃣

Dukansu suka nuna mata store sai kawai tawuce store ta debo wake da geron kunu tafara aiki sukace mezamuyi tace “no karki damu, kawai zan dinga tambayanki unda abubuwa suke” tafara aiki she will do everything in her power to win Khaleel’s love back. Kunu tashiga yima Khaleel, Mom na zaune a falo kusan 30min saikuma ta juyo badai yarinyar nan taje tana taya yan aiki yin aikinsu ba, juyowa tayi but bata ma iya ganin kitchen daga wajen, tashi tayi ahankali rike da empty plate na fruits nata tazo wajen kitchen din duk basu ganta ba turus ta tsaya tana kallon Hawwa dake buga kosai yan aikin sun zazzauna suna kallonta, yaune rana na farko da Momy ke ganin Hawwa babu mayafi dan ta rataya gyalen a kofa tana aiki gaskiya yarinyar is very very beautiful she cannot even lie and she’s tall and very pretty dan kitson datayi dan ya zubo a bayan wuyanta kuma gashinta da tsayi, tai shiru kawai tana kallon Hawwa somehow she’s seeing why yaronta ke sonta, Hawwa kaman taji ajikinta ana kallonta juyowa tayi ganin Mom yasa gabanta yafadi da sauri ta ijiye bowl din ta taho wajen kitchen din bayan taja gyalenta daga kofa ta yafa cus is her own way of showing iyayen mijinta tana girmama su, yan aikin na tashi suma dasauri, ahankali cikeda respect Hawwa tasa hannu takarbi empty plate dake hannun Mom, cikeda girmamawa tace “Momy kina bukatan wani abune namiki?” Tsayawa Mom tayi tana kallon Hawwa shekeke sabida mijinta yayi yaji itama tazo tawani biyoshi nan, saikuma cikeda masifa tace “me kikemin a kitchen nina aikeki”? Kanta na kasa tace “Momy kiyakuri kosai zanmai” dariyan takaici yakusa kufcema Mom tace “eh kin iya kosai amman baki iya kulamin da yaro ba mara mutunci kawai, kinaso ki kashemin dan dayadaya ne” Mom tajuya fuuu Hawwa tajuya takoma kitchen she just promise kanta she will show Momy she’s a good person and

she will win Momy da Khaleel dukansu, komawa tayi tashiga soya kosan da ko’ina yacika da kamshi.

Sai bayan yadawo daga masallaci yasami bacci, kamshin kosai daya ratsa hancinsa yasa ahankali yabude idanu hardly kamshin abinci ke shigowa side nashi wat happened yau kodan ba’a cika kosai bane anan he just hopes kosan will taste good kaman na Hawwa. Yadan sauke ijiyan zuciya sabida fadomai zuciya da Hawwa tayi, sannan ya tashi yafada bayi yayi wanka but still idanunshi jaaa closet nashi ya shiga yasa AMI Paris shirt just 2 buttons na kasa yasaka yana yasa wani 3qyater dark blue ya feffesa turare har wani dan ramewa yayi yasaka flops yashiga saukowa yana folding hands na riganshi Mom dake zaune tana bude news paper ta dago kanta takalleshi yarinta duk ya susuce yadawo wani kala tashi tayi tana ijiye jaridan cikeda so tace “Khaleely” he’s not happy kawai bayama walwala ko kadan tarasa wani kalan so yakema Shegiyar yar sandan nan mara kirki bayan ga mata wayanda suka fita sosai, ahankali yace “good morning Mom, an mini kosan”? Gyadamai kai Mom tayi takama hannunshi tace “let’s go lemme feed you” Hawwa na tsaye a kitchen tana karasa tuyan kosan taji Kamshin Khaleel ijiyan zuciya ta sauke ahankali kirjinta yahau bugawa.
Zama yayi Mom tabude flask na kosan dasauri yadauki daya yakai baki asanyaye dan baida energy yace “it smells good Mommy” yakai bakinshi Mom tashiga zubamai kunu, hakanan kosan na shiga bakinshi kawai it reminds him of Hawwa again yayi shiru ya dakata da taunawa, ganin ya tsaya yadena taunan yasa Mom tace “ba dadi ne”? Girgiza mata kai yayi baice komiba sai kawai yacigaba da ci, Mom ta zauna kusa dashi tana juya kunnun ta a spoon takai bakinshi tana bashi yasha why does it taste like Hawwa made this? Rabon dayaci abinci dayama bakinshi dadi tun ranan daya tafi office around after twelve sai yau dayabi Sam party, taba wuyanshi Mom tayi tace “Alhamdulillah temperature ya sauka sosai, idan kagama saimuje hospital ko?” Dan turomata baki yayi gabaki babu abinda kemai dadi yace “ni yaro ne zaki wani bini hospital they will send the result to Dad” Murmushi Mom kawai tayi ganin first of all he’s hurt and not in good mood tace “to shikenan yarona uhmm cigaba da cin abincin ka” baki yabude mata tadebo kunu a spoon zatakai bakinshi ta gefen idanunshi yafara ganin kaman yaga Hawwa wai idanunshi gizo sukemai ne yadai daure yaki motsi gently Hawwa tafito daga kitchen din tazo wajen kirjinta na bugawa kawai saita kara kneeling awajen batare dataji kunyan Mom ba ko yan aikin dake kitchen ahankali tace “go……g…good morning Husby” Kaman Khaleel baisan mutum na wajenba yakalli Mom batare daya sha kunun datake bashi ba, voice nashi ba dadi yace “did she make this food?” Yatsine fuska Mom tayi tace “ban sata ba taje takama aikin daga hannun masu yi tahau yi” mikewa Khaleel yayi cikin kakkausan murya yace “this should be the first and last time za’a bani abinci made by her Mom!” Wani irin katsewa zuciyan Hawwa yayi tana wajen aduke tana kallon Khaleel

sai kawai yadauki tissue ya share bakinshi ahankali yace “bye Mom” yajuya zai tafi karaf Hawwa takama hannunshi tarike dasauri yajuyo ranshi a masifan bace, tashi Hawwa tayi ahankali takalleshi kaman yanda yake kallonta da tsana akan idanunshi gabanta faduwa yake sosai, bakinta dake rawa sosai tashiga budewa zatai magana but zuciyanta ma ba karfi kawai tafashe mai da wani sassanyar kuka yakalli hand dinshi data rike yace “sakeni! Let goo off my hand!” Kin sakinshi Hawwa tayi tana kallon kwayan idanunshi ganin yanda rayuwa juyi juyi ne, da fa ita Khaleel ke rikewa haka tadinga bala’i tana gaggayamai magana tana cewa yasaketa kawai saitaji she’s regretting everything more, cikin murya mai bala’in rauni batare data sakeshi ba tace “Husbyyyyy I want to talk to you! Please give me just a minute, dan Allah” dauke idanu daga kallonta Khaleel yayi yace “for the last time let go off my hand and kada bakinki yakara kirana da that name my name is Ibrahim Khaleel” Kirjin Hawwa bugawa kawai yake da tsoro da fargaban ganin mijinta ya tsaneta muryanta babu ragowan kwari tace “I love……” “Ke!” Khaleel ya fizge hannunshi daga nata ya nunata da yatsa idanunshi na kadawa saikuma ya matso dab da ita ta yanda dagashi sai ita zasuji maganan yace “don’t you dare say that word cus it makes me even hate you more! Na tsaneki!” Baya Hawwa tayi kaman zata fadi dasauri ta dafa chair Khaleel ya watsamata mugun kallo yawuce yayi kofa abinshi.

EPISODE 1️⃣2️⃣4️⃣

Khaleel na fita yashige motanshi yana sauke ijiyan zuciya.

Momy da fadansu kaman tana kallon tv haka abin yake mata tana xaune abinta a dinning tana kallo tawani harari Hawwa dake zaune akasan falon tana goge fuska sai kawai ta wuce dakinta abinta. Khaleel na zaune cikin mota wayanshi yahau ringing Baba ne hakan yadaga Baba yace “kazo gida ina nemanka” ahankali yace “toh” har unguwansu yaje ya gyara buyuran rigansa yafito daga mota Baba namai murmushi sai kawai yakama hannunshi suka shiga xaure dayayi shimfida ya zauna shima ya zauna, Baba yace “ya jikinka?” Anatse yace “naji sauki Baba” Baba yace “yau result dinka zai fito ko”? Gyadamai kai yayi yace “amman inaso Dady na ya karbo I told Dr yabashi result din” murmushi Baba yayi cikeda so yace “zamuji alkhairi in sha Allah” yayi shiru hakan yasa Khaleel yace “Baba menene?” Cus yaga yanayin shi, anatse Baba yace “maisa kake shaye shaye Ibrahima?” Dasauri Khaleel ya kalli Baba saikuma ya sunnar da kanshi kasa kunya na kamashi sosai, ahankali aba yace

“jiya mahaifinka ya sanar damu” Baba yayi shiru yace “ko kadan bakai kama da mai yiba Ibrahima yaran arziki basa shaye shaye kuma nasan kai yaron arziki ne dan haka nace saina kiraka namaka fada, inaso ka bari kaman yanda mahaifinka yace bayan kayı aure karage yi, inaso ka cigaba ahaka kama daina gabaki daya, sabida Allah sannan sabida lafiyan jikinka, inaso kazama mutumin arziki kamili yanzu kai ba yaro bane, kanada mata da yarinya duk rayuwan banzan nan abarma yara kaji, akwai mutum biyu yanzu da hakkinsu na kanka dole kazama namiji kafita daga sahun yaro ko yaron Mamanshi kadawo namiji tsayayye kaji” gyadamai kai Khaleel yayi Baba yace “inaso ka rike kanka, kaji tsoron Allah ka gyara rayuwanka kanunama matarka kasan mai kakeyi kayı haka zakaga bazata taba rainaka ba kajini”? Anatse Baba yace “inasonka ne Ibrahima saisa nake maka fada, inaso kazama mutumin arziki a better person, na hana Hawwa aiki but kai inaso ka dinga zuwa naka aikin dazaran ka gama samun lafiya kaji” gyadamai kai Khaleel yayi, Baba yadanyi shiru chan yace “Hawwa batason Baban Yaseer wlh, bata taba sonshi ba kuma bazata taba sonshi ba wlh” lumshe idanu Khaleel yayi, ahankali yace “I know! Nasan dalilin dayasa tai magana kawai kalman yacimin……” saikuma yayi shiru yadan sauke ijiyan zuciya yace “Dady yagayama min everything da maganan da sukayi, yan sandan da aka tura hospital din sun karbi wayansa sun tabbatar min yajeyi stalking Matana yakeyi, ga hotunanta tundaga sanda tafito daga gidana ma, da every move nata” Gyadamai kai Baba yayi yace “rayuwan nan zomu saba ne zomu shirya, Hawwa tayi ba daidai ba amman yanzu tasan tana kaunarka kayakuri kaji, Ibrahima ina sonka da diyata sosai tayi kuskure ka gwada mata tayi sabida nan gaba kada ta karayin makamancin sa, amman kada ka tsaneta yarinya ce kasan mata da kalan tunanin su gasu da tapka shirme, kayakuri” gyadama Baba kai yayi ahankali, Baba ya shafa fuskanshi, dan kallonshi Khaleel yayi for the first time sai yayi dan murmushi kadan yace “thank you Baba namaka alkawari zan gyara halayena kamin addu’a kaji Baba” Baba yace ina maka yarona, Khaleel yatashi yace “zan tafi” Baba yarakashi har waje yatafi.

Wuraren 12:30 na rana Mom ta farka daga baccin safiyan datayi ta watsa ruwa tafito tana sanye da waya mahaukaciyan lace tazuba gwalagwalai da 2friends nata zasuzo ta tsaya turus ganin Hawwa a falo ita kadai zaune akan kujera takife kanta a hannun kujera bacci yadan kwasheta mamaki abin yabama Mom badai tun safen nan yarinyar nan tana nan bata koma side nata taje ta kwanta tayi bacci tahuta ba.

Wucewa dakin ma’aikatanta tayi suna ganinta duk suka tashi zaune tace “an gama girke girken danace ayi?” Babban Chef nata tace “Mrs Khaleel cooked everything Ma, she asked us to rest” baki Mom tasaki saikuma ranta abace tafito tawuce dinning tashiga bude warmers ya Allah! Lafiyayyen biryani Mandi, gizzard dodo, pepper chicken, kofta, samosas, moimoi, salad, sai juice na fresh juice zobo da cucumber juice Hawwa tayi, sannan ta yankama Mom

